» *AUREN GADO* ğ

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
And now AUREN GADO,

ASLM MAKARANTA, INA YIWA KOWA FATAN ALKHAIRI, GODIYA MARA IYAKA ZUWA GA MASOYA RUBUTU NA A DUK INDA KUKE, JINJINA TA BANGIRMA GAREKU, SOYAYYAR KU ABIN ALFAHARI CE AGARENI, GOYON BAYANKU SHINE SILAR CIGABA NA ALLAH YA BARMIN KU A DUK INDA KUKE CIKIN AMINCI, TUNDAGA MASOYANA NA NIGERIA DA KUMA NA KETARE INA WA KOWA FATAN ALKHAIRI, NAFA DAWO BATAREDA NA SHIRYA BA DOMIN KU MASU BIYONI SUNA ROKONA, MATAR SOJA KIFARA MANA AUREN GADO MUN MATSU, TOH GASHI NAN SAI NEMAN GOYON BAYAN KU KAMAR KODA YAUSHE,

with ur help wnn lbrn zaitafi AUNTY deeja domin bantaba tsallaka koda airport ba don haka keep guiding me akan komai, and please make sure kin turomin na jirgi nasameki a bangkok din nan just once please, tunda corona ta hanani zuwa makka bana, but don't worry kudin na gona just pray muyi harvesting buhu dari na soya beans, bana zamuje vocation a duk fadin bangkok, ayi kokari a biya don Allah zansiya takin gona ğŸ˜‰

BISMILLAHIR-RAHMANIR-RAHEEM

ğŸ†“ page

1â*ƒ*£&2â*ƒ*£

A kwance yake abakin wani tafkeken beach , yana kallon duk matan dake kaida kawowa a wurin cikin fitinannun bikini da kuma lafta laftan sun glasses, wani irin ya mutse fuskar shi yakeyi domin kamar kashi haka yake ganin su, ba Abinda ya dameshi, bayajin mace zata iya burgeshi just like that saboda shigar banza,
Kallon shi nayi dakyau, gayen ba laifi chocolate ne shi duk da banga idanun shi ba saboda suna boye a cikin sun glass, Amma nasan zasu kasance masu kyau da tsari, lips dinshi kuwa I can clearly see them suna sheki very soft and shinny, he is behaving like jinin sarauta Amma I don't know yet who is he? Gefen shi system dinshi ne tareda wayoyin shi guda biyu, daya tayi kara ya dauka cikin sauri domin ganin sunan dake jikin screen din wayar, "heartbeat, Hmmm no wonder mata basa burgeshi duk da yawon da sukeyi a gabanshi necked, sai dai me, yanda yake zuba shagwaba tareda maganar da yakeyi yasa mamaki ya cikani domin daga gani bada mace yake magana ba, is he a gay???

"Yaya please, wai kai are you really serious you are getting married??,
Banajin maganar dayan side d'in saidai Amsar shi, "of cos yaya dole inzo Auren ka nine fa best friend best brother and ur best partner in life, am coming insha Allahu, but kasan halin momy kuma I don't want problem shiyasa nake zama na a bangkok, is alright am on my way don't worry heartbeat, just for you.
Datse call din yayi ya mike, a lokacin na kalleshi da tsarin jikinshi daba riga sai guntun wando kawai ga six packs dinshi da suka fito gwanin burgewa alamar yana gyming, tareda kulada lafiyar jikinshi sosai, zare sunglass din yayi, na kalle sexy eyes da lashes dinshi kamar na mace zaro zaro, he is really handsome, one look zakiyi mai ki afka soyayyar shi indai zaki kalli wa'innan killer eyes dinshi, gashi ya iya juyasu, kamar wani karuwar namiji, cikin takun kasaita ya zura beautiful sleepers dinshi na maza ya kwashi kayanshi tareda key ya nufi can gefe inda ya parker open jeep dinshi, ya zube su tareda zama yajata a guje yabar wurin,.

Wani D'an madai daicin gidane a cikin jerin gidajen dake cikin unguwannin dake shahararriyar Unguwar ta
Phetchaburi Road, Makkasan,
Ratchathevi, Bangkok 10400 Thailand. unguwa ce ta wanda ya tada Kafada da Abubuwan duniya, duk da gidan da ya shiga ba wani kato bane amma kana ganin shi kasan ya gaji da haduwa, maid dinshi ne yayi saurin taron shi da gorar ruwa tareda towel, karba kawai yayi ya nufi bathroom, ya dauki Kusan hour guda kafin yafito kamar zai canjo fata,
Yana fitowa daure da guntun towel ya tsaya Turus tareda zubawa dakin ido yana mamakin ta, tayi mai dai dai tareda kashe shi da idanu, he just hate that character a wurin mace, shi so yake rana daya Allah ya hadashi da mace mai kunya, that is, tagama siyemai zuciya, but this kind of girls dake rayuwa a irin wannan garin wai in the name of study, Ahh he really hate them, karuwai kawai,
Ganin kallon rainin wayau Dayake watsa mata yasa ta zaburo tareda matsowa cikin rangwada, doguwar riga ce har kasa she cover all her body but akwai gyara a al' amarin ta, duk da kyakykyawa ce gata a dire, kuma fara tas bai hana kagano idanun ta sun bude,.
"Hey dear tafada cikin kashe murya, wani irin kallon don't touch me ya mata tayi saurin daga

hannun ta sama tareda cewa "is ok I won't dear, but please just once give me chance to prove myself.
"Dont even try to suffer ur self, nafada miki fauzy am not interested, just back up. " am ready to follow you I promise zanyi duk y'anda kakeso am ready to change for you, nafada ma dady na kai nakeso zamu koma kano tare dakai please na horu ka soni don Allah, "Look don't even try, bazan Auri sauran wasu ba infact am not ready for marriage now shiyasa dana gama school naki komawa gida saboda nasan Abinda zai faru, don haka kifita a rayuwa ta banason naci.
Kuka tasa mai tareda dukawa kasa, "I swear bantaba bari wani yasanni ba kawai romance ne kuma kasan is a normal thing ai, kana ganin saboda kai nakasa komawa gida kullum cikin karya nake musu please karka tarwatsa min Rayuwa kaine cikon numfashi na, tausayin ta yaji sosai domin ta dade tana wahala a kanshi tun baya kulata har yafara D'an sauraran ta, "Oh come on, kinsan natsani kuka ko, ki shirya am going tomorrow mutafi nija am going for good, if you are ready..... "Of cos dear am ready, tafada tana dariya mai hade da tausayin kanta, goge hawaye tayi tafita cikin sauri domin ganin ta tattara duk Abinda zata bukata.
"Ahhh yafada tareda dafe kai, this girl is headache I swear,
Shiryawa yayi cikin guntun wando da black singlet yafito gwanin burgewa sai tsadadden agogon shi da kuma dankwalelen zoben dake karawa hannun shi tsari da kyau wa'inda baya taba rabuwa dasu, infact ko shopping zaiyi agogo ne first a tsarin shi he just love watches saboda suna karamai tsari da kwarjini,

Abincin shi ya zauna yafaraci wa'inda duk ganye ne sai crabs roasted ones, saida ya dauki lokaci kafin ya kammala ya sanya tissue ya goge bakinshi ya mike, duk al'adar Chinese ta gama ratsa shi abincin su harshen su al adunsu, wainda zasuyi matukar wahalar dashi a nija,.
Saida yayi clearing komai a daren, about visa da sauransu, karfe uku na Asuba jirgin su ya daga wanda zai kasance long journey duk da a jirgine, tafiyace ta Kusan awoyi, tana zaune a gefen shi ta zuba mai ido sai faman danna system dinshi yakeyi like ba wata halittar dake existing a kusa dashi,

She don't bloody care tunda yace su koma nija tasan komai zaizo cikin sauki,
Saida ya dauki lokaci kafin ya rufe ya saka headphones ya rufe idanun shi yana farin cikin zaije wurin yayan shi wanda yafi kowa daraja a duniya a wurin shi yana mashi so mai girma yana kaunar shi fiyeda kanshi,
Duk da su marayu ne ubansu ya mutu tun yana D'an karami, baiyi lacking komai ba, domin baban su gawurtaccen D'an siyasa ne kuma D'an kasuwa wanda yanada share a manyan campanonin dake ciki da wajen kasar mu harma da ketare, subiyu ne kacal wurin mahaifiyar su, yayan shi Ahmed sai shi Ibrahim khalel wanda khalel din ne yafi amfani dashi,
Gatan da yake dashi baya faduwa haka kudi ba matsala bane a rayuwar su domin mahaifiyar su itama ba azaune takeba tana aiki da first bank tareda matsayi mai girma,
Akwai banbancin hali a tareda shi da d'an uwanshi, domin shi mai zuciya ne, shikuma Ahmed yanada sanyin hali da hakuri, shakuwa ce mai girma da tausayi a tsakanin Y'an Uwan biyu sukan iyawa juna sadaukarwa ta kowacce hanya, tun suna yara balle kuma yanzu, kowa yasan how they love each other, don haka ko ginin su a hade yake basu taba raba gida ba duk da sunfi karfin hakan, katoton gidan mahaifin su suka kara fadadawa tareda buga plat biyu nasu

tangama tangama sai na mahaifiyar su wanda a ciki ma akwai part part dinsu, domin bataso suyi mata nisa, mace ce mai tsananin zafi da kuma rashin hakuri gashi bata son sunan talaka bare kuma talauci batason rashin Aji a rayuwar ta don haka kullum burinta ta fantama, bakaramin shiri takeyi a Auren ya'yan taba tunkafin su tashiyi ma, saidai kash ansamu akasi domin Ahmed ya kaucewa tsarin ta ta hanyar dakko Y'ar talaka tulus, wanda bakaramin daga akasha ba kafin ta Amince da zancen Auren bayan dogayen sharuddan data gindaya bayan Amincewar ta. To muje dai zuwa yanzu zamu fara,.

Karfe goma jirgin nasu ya sauka a babban filin jirgin na Aminu kano, wanda sukaci karo da motoci birjik a jere na taron su, tuni fauzy ta matso "you see kamar jira akeyi indawo kaga irin motocin da sukazo daukana please ka yarda muje gidanku after two days sai intafi gida. "Hmm yafada tareda watsa mata kallon you lost ur mind, kafin ya ce "al adar Chinese ce wannan ba ta bahaushe ba don haka go home zanyi inviting dinki to my brother wedding ok,. "Ok tafada cikin farin ciki, ta nufi masu taron ta wainda kana ganin motocin kasan itama Y'ar gidan wani kwallon barawon kasar muce,.

Hango yayan shi da yayi yasa ya tafi da sauri cikin farin ciki ya rungume shi, Ahmed din ma kyakkywa ne suna matukar Kama saidai shi fari ne while Khaleel chocolate ne, "my yaya kai kadai kazo were is mommy?
"Long story muje ko, yafada yana karbar jakarshi karama tareda bawa driver umarnin kwaso kayan da yazo dasu yakai boot, saida suka zauna yace "Am sorry yaya sai jiya nayi placing odar na kayan matar ka zasuzo tunda by air ne kafin bikin insha Allahu nasan zakaso su. Rungume shi yayi cikeda farin ciki tareda cewa "tank you my kani, but please karka bari momy tasani kawai zamu Ajiye mata ne a dakina har akawo ta. "Why? Cos momy batason ta infact bakaramin yaki akayi ba kafin ta Amince ayi komai. "Mommy mommy bazata canja ba, so why she hate her? "Because she is poor. Saurin kallon shi yayi "so brother is your foult kasan momy tunfarko ai why ka dakko poor girl uhm?
"Because I love her so much I love Naziya a lot khaleel, she is innocent and young she is very cute I can't help it, bazan iya Auren wata ba in har aka hanani zama da ita. Rungume shi yayi cikeda so da kuma tausayin D'an Uwan nashi yace "is ok am here you know I will support you, don't mind mommy, but her name is unique. "Yeah she is also unique brother, yafada yana lumshe idanun shi tareda jin soyayyar ta mai zafi har wasu irin madarar ruwan hawaye ne suka taru a idanun shi,.

A cikin fitacciyar unguwar ta sulaiman crescent suka yada Zango cikin wani tafkeken gini na kece raini, tsarin gidan kamar a turai, ya fito tareda shakar iskar kayan marmarin dake zagaye da ginin gidan,
Harabar gidan shake yake da motoci different product da kuma runfuna na Alfarma dake karkashin bishiyoyin kwakwa ta ko ina irin na gargajiya da masu kudi keyi,.

Kallon shi Ahmed yayi tundaga kasa har sama "bazaka canja character dinka bako yawo

daguntayen kaya imagine tundaga bangkok kazo da three quarter da t shirt baka ko jin sanyi? "Kamar ka mantani ko yaya nifa I hate heat wallahi shiyasa nake wuni a beach., zaka hadu da momy muje ciki,.

A tafkeken katon falon an tsara shi fiyeda tunanin mai karatu kujeru Kusan set uku ya mamaye amma da sauran fili kowane set da center carpet dinshi masu laushi da nutse kafafu, standing art tangama tangama ta koina bayan na jikin gini wainda suka zama kamar decoration a falon, A tsaye take tanata kai da kawo kamar Y'ar sintiri tana jiran fevourite son d'inta, ya iso, ta hana masu aiki sukuni sun kalkale but parts dinshi yafi sau uku da safen nan, dishes kuwa kamar a hotel saboda d'oki,
Macece hakima kamar Aisha D'an kano margayiya taci Abuja style cikin tsadadden leshin ta wanda yafi karfin dari a jikin ta, da glashin ta na kara karfin idanu, wanda yakara fito da haiba da hutun ta harma da masu gidan ranar data tada Kafada a ciki,

Sallamar su yasa tamike cikeda fara'a tana "Oyoyo my happiness welcome back dear tafada tana rungume shi tareda bubbuga bayan shi, "tank you mommy munsame ku lafiya? "Alhmdulillah tafada tareda dagowa tana "ai dai tunda kadawo yanzu zanji saukin lamura na at least inada inda zancika burina, ka huta ka dage ka dakko min Y'ar gidan bayero ko buhari, ka huce min takaici. Tafada tana watsawa Ahmed harara, dukar da kanshi yayi tareda daukar Karamar jakar D'an Uwan nashi yayi ciki da ita, zama tayi a set daya tareda janyoshi tana faman korafi tun bai hutaba, " hope zaka dakko Y'ar gidan mutanen arziki kai ba Y'ar matsiyata ba? "Mommy mommy mommy please meyasa kike hakane? Nifa am here because of my brother, kinsan banason korafi kibarshi ya Auri choice dinshi koda cripple ce tunda shi zai zauna da ita please allow him to be happy I beg of you. "Shikenan tunda kaima kabi bayan shi, amma promise me zaka share min hawaye kaji? "Ok I promise bari inje in huta am tired, fresh up akawo maka abinci a ciki ko? "Yes please kinsan me nakeso ai ko? "Sosai karka damu na shirya maka komai.
A zaune yasamu brother dinshi yana dafe da kanshi ya zauna tareda dafashi cikeda tausayi "relaxed bro am here komai zaiyi normal kaji, Aunty what ma sunan ta? "Naziya, yafada fuskar shi na washewa domin sunan ta kawai nabashi farin ciki, "get ready zamuje unguwar su anjima kaganta kaji. "Ok my heartbeat. "Stop that name kafin my Naziya taji tayi kishi fa. "Oh no yaya zata shiga tsakanin mu ne, to nima zanbi bayan mommy fa. Rungume shi yayi tareda cewa "no no no tasan da zaman ka, tundaga lokacin da muka fara haduwa, da ita, ka huta zanfada maka komai game da ita kafin muje gidan,.

Karfe biyu ya farka daga baccin gajiyar da yayi yaga Ahmed zaune ya na baza kamshi cikin D'an datsesiyar getzner tana maiko, tashi yayi "yaya har kayi wanka? What is the time now? Agogon shi ya nuna mai ya zabura yana holy shit, ya diro a lumtsumemiyar katifar shi, yayi bathroom domin baiyi Azahar ba, cikin sauri sauri ya zura jallabiya ya tada sallah, domin duk abinda yake yi baya son wasa da ibadar shi amma idan ka kalleshi zaka dauka rayuwar duniya tafi komai ratsa shi amma yarone mai riko da Addini bisa ga goyon yayan kwarai da yazamo

mai tamkar uba.
Saida ya idar ya bude jakar shi tareda ciro kananan kaya.
"Wait gidan kawu zamuje a mandawari kasan halin shi ka sa manyan kaya nasa an shirya maka new ones a wardrp dinka na nan dana can side d'in.
"What? Kasan nifa banason zafi ga garin nan da zafin tsiya kuma insa kayan da zasu hanani sakewa, "wait yaya ba an gama zuba komai ba a part dinmu why muke nan har yanzu? "Bisaga umarni na khaleel bazan yarda a saka Y'ar talakawa cikin ginin da na narkarda dukiyar mijina datawa ba, a kawo min gayyar k'uma da kudin cizoba ta zo nan ya isheta zama tunda bazata iya zama a katon giniba, domin ko dakin generator dinmu yafi gidan ubanta girma,. Saurin kaucewa khaleel yayi domin inda sabo sun saba, ya nufi katon wardrp din yaga kaya shake saida yayi murmushi saboda yasan aikin yayan nashi ne,
Fito da Kala daya yayi irin na jikin shi ya nufi hanyar bathroom domin ya canja saboda mommy dake dakin,
Tana zazzaga complain, fitowa yayi tareda rungume ta yana baza kamshi shima kanshi da yasha askin matasan zamani ya na sheki ya sha gyara ya ce" mommy please enough of your complains kibar yayana yasamu farin cikin shi mana,. "Oh wato kuna tunanin bansan what is best for him ba ko? Bayan na kawo mai yammata Kala Kala Yaran kawaye na masu ilimi amma ya nace sai Y'ar talakawa mtsww, ka kara Abinci kafin kutafi gidan kawun naku kafin yazo yana baza min fitinar shi shima yace na hanaku zuwa ku gaidashi, ta fita tana kasaita, "Hmmmm Sorry brother kariga kasan halin momy. "Is ok eat muje ko?

Hour guda ta kaisu gidan na kawun nasu Alhaji modu mai gwal wanda D'an kasuwa ne sosai a harkar gwalagwalai, mutum ne a tsaye akan zumuncin shi domin baida wasa yanada mata biyu da yara sunkai goma, shikadai Hajiya balkisu ke shakka domin yafita fitina kuma shima yanada kudi shiyasa take ragamishi domin sau tari yakan yimata Abu tace yaci Arzikin Aljihun shi. Sunada kanni biyu mata bayan mahaifin su khaleel shine babba sai Alhaji modu din, su Y'an Asalin garin maiduguri ne iyayen su ne suka kawosu babban birnin na kano, sunginu suma duka domin ba talaka a cikin su har matan ma domin suna gidajen kusoshin kasar mu,

Y'an mata ne birjik a gidan wainda kowaccen su nada burin samun daya daga cikin wa'innan zaratan mazan saidai sam su Hankalin su baya kan kannin nasu infact basa burin Auren zumunci ma, itama Hajiya balkisu bata ra'ayi domin batason ya'yan ta suyi Aure inda bazata iya juya Suruka ba,,
Domin tasan Y'an Uwan mijinta duk ba wai mutunci sukeda shiba wanketa zasuyi akan ya'yan su,
Sun samu tar bar bangirma daga uwar gidan Kawu modun kafin ya dawo,
Sundauki lokaci a gidan har kawun nasu yazo, wanda yayi farin ciki sosai ya musu nasiha tareda basu shawarori, "yanzu tunda kadawo khaleel saika tallafawa D'an Uwan ka domin yayi matukar kokari wajen tafiya da campanoni da kuma masana'antun ku, sai kuci gaba da tafiyar da kasuwancin ku cikin tsari, Sannan naje munyi magana da uban Naziya, Auren naku nan da sati biyu aka tsayar don haka ka je ka karasa shirin ka "na kammala komai kawu ni ta wajena.
"Toh masha Allah, sai mu jira lokaci Allah ya tabbatar da Alkhairi, Amma dattijon nata mutumin

Arziki ne baidamu da Abin duniya ba gaskiya karka damu da shirmen mata wannan gidan irin shi ya kamaci namiji ya nemi Aure. Wani irin dad'i yaji tareda sauke Ajiyar zuciya, saida suka yi magrib kafin su bar gidan, suna hanya yana bashi labarin Naziya,..... ğŸ–Š

watch out, domin salon zai tafiyar daku masoya muje zuwa

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ» *AUREN GADO* ğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
And now AUREN GADO,

ğŸ“ page

3â*ƒ*£&4â*ƒ*£

..... D'an karamin gidane mai zaure a cikin tsohuwar unguwar ta jakara, almajirai ne birjik a zauren da Alama malami ne a gidan mai Y'ar Karamar tsangayar Almajirai, ko tsakar gidan ma akwai wasu dakuna dake dauke da Almajirai, rayuwar gidan sun dauki Almajiran kamar Yaran gida ba kyama ba wulakanci, matar gidan inna kulu mace mai hakuri, tanada ya'ya mata guda hudu manya biyu sunyi Aure sai Naziya da kanwar ta Shukrah, Yanzu Naziya nada shekara goma shatakwas sai shukrah mai shabiyar, ta kammala secondary dinta Bana a makarantar gwamnati, a tsugune take tana wanke kwanonin da suka bata Y'ar Karamar wayarta ce a kunne a gefen ta tana sauraron karatun Al'qur'ani mai girma tana bi a hankali cikin kwarewa,
Kare mata kallo nayi domin yarinyar batayi Kama da kalar talaka ba domin dai dai da duddugen

kafarta farare ne tas kyakkywa ce sosai kamar wata Y'ar larabawa tana sanye da guntun hijabi akan al adar ta da kuma koyarwar inna kulu domin gidan su akwai mazajen Almajirai akoda yaushe, fitowa dattijuwar tsohuwar tayi tareda cewa "inkin kammala ki dora mana Abincin rana Naziya, shukrah ta kai mana markade tunda duk babu Almijirai yau, "toh Inna. Tafada tana wanke wurin data bata, she is really cool and beautiful ga tarbiya dake tattare da ita jikinta ba rama kuma bakiba duk da tana cikin hijabin ta nagano hakan jikinta D'an dai dai bazaka taba yimata kallon talauci ba duk da Abinci baifi karfin tukunyar suba, mahaifin su yana koyarwa yana sana'oin shi wanda yake daukar gidanshi da kuma hidimomin iyalin shi,
Haduwar ta da Ahmed wata rana ce tadawo makaranta a gajiye shikuma yazo unguwar su gidan wani yaron shi dabaida lafiya, tafiya takeyi cikin gajiya a kuma natse ta gefen titi, y'anda ya kwaso motar tashi yasa ya watsa mata ruwan datti kasancewar gari ne na damuna ga kuma yanayin unguwar da yatara guraben ruwa ta ko Ina, saurin jatayi ta tsaya domin gaba daya uniform d'inta ya baci Har fuskar ta ma ruwan ya fallatso mata, saurin fakawa yayi ya fito da sauri yana so yabata hakuri,
Dago kyawawan idanun ta tayi tareda goge fuskar ta da gefen hijabin ta inda jan ruwan bai bata ba, ta kuma kallon y'anda ya saki baki yana kare mata kallo batareda ya iya cewa komai ba, yarinyar ta gama tafiya dashi, juyawa tayi ganin baida niyyar cewa komai tayi gaba, saurin shan gaban ta yayi "Am sorry please ki tsaya muyi magana, ya zaki wuce batareda kince komai ba bayan nayi miki laifi?
Saurin Tsayawa tayi tareda dago idanun ta masu narkar da zuciya tace "nice zanbaka hakuri domin hanyar bata Y'ar talaka bace Nazo kuma na tsaya, sannan don Allah ka matsa in wuce kafin ayi wani tunani akaina a cikin unguwa ba mutuncin gidan mu bane tsayuwa da bako a kan titi. Tafada tana rabewa tayi gaba.
"Wow wow wow what a magic voice, yafada yana binta a hankali tana sauri har ta fada gidan su da gudu domin tana jin takun shi a bayan ta a mugun tsorace take dashi domin yayi Kama da Aljani a wurinta domin he is very handsome kana ganin shi kaga D'an hutu,.

Gefen Ahmed tunda yasa Naziya a ido yakasa sukuni saida yabi ta gefen yaron shi yaji komai akanta, tuni yagano Y'ar babban gidace wato gidan dattijan kwarai, baiyi kasa a guiwa ba ya dawo yasamu mahaifinta tareda neman izinin neman ta, Malam garba yaso ya hana domin ganin D'an gidan wani ne Bayason ya saka Y'ar shi cikin matsala, ya nuna mai mahaifin shi ya rasu kuma shike rikeda kanshi ba wata matsala, bai Amince ba saida ya turo kawun shi yazo suka tattauna ya Amince yabada izinin neman ta,.

Allah yagani bawai Ahmed baiyi mata bane, ita batada burin shiga gidan da yafi karfin ta wanda bata ma riga taga dukiyar ba tukun kawai shitake gani kudin su na bata tsoro, ganin irin k'a'i dar mahaifin ta, baya ko sake mata kudi infact tuni ya daina zuwa da shigar da zata hanata sakewa dashi domin ya lura da yanayin ta dana gidan su tsab, yasamu kanta ta hanyar nuna mata akarkashin wani yake shima yana hustling ne,. Shiyasa yasamu kanta har ta Amince suka Gina soyayya mai karfi a tsakanin su she really loves him domin he is very simple baida fushi baida girman kai saurayi ne mai natsuwa wanda ko yatsanta bai taba kokarin kamawa ba soyayya yake mata mai tsafta, har kawo yanzu da Al amarin yakai ga zancen Aure, zaman ta dashi tagano Abu biyu sune masu matukar muhimmanci a rayuwar shi, mommy and khaleel

wanda basa hira sutashi bai kira sunan shi ba tagano irin tsantsar soyayyar da yakewa kanin nashi ta hanyar bata labarin shi a kullum zaice "in munyi Aure zaki rika dafa mai Abincin da yakeso baya son irin namu na nija zansa akoya miki irin dishes din da yakeso. Abun na bata mamaki ace mutum Abincin mu na nija mai shegen test baya burgeshi sai mara magi? she almost know everything about him by now saboda labarin shi, tasan yana karatu a waje kamar yadda Ahmed yafada mata kawun su ya kaishi waje karatu, Ita kanta so take taga wannan khaleel din da labarin shi baya karewa a bakin Ahmed,. Tana son Ahmed sosai halin shi, yanayin natsuwar shi ya banbanta da na samarin zamani masu burin cakumar mace da sunfara soyayya.....
Wannan shine D'an takaitaccen labarin Naziya da Ahmed.

A hanyar su ta dawo wa daga sabon titi yake bashi labarin komai na su Naziya tareda fadamai boye mata kudin da yayi saboda batason mai kudi y'anda ta nuna mai. Khaleel yasamu kanshi da yin dariya, " she is funny wace mace ce batason hutu da kudi in this era? " my Naziya wants a simple life ba a ginata akan greedness ba, all this kyale kyalen duniya basa burgeta do you know nasha siya mata gifts in ajiye domin gudun matsala ko fushin ta, do you know tun zaman mu bata taba demanding tana bukatar wani Abu a wurina ba, "she is such a diamond in the rocks, she is different khaleel my Naziya is perfect I told you. "Hmmm Allah yasa tana sonka like you love her? "She do Insha Allahu, koda baikai wanda nake mata ba nasan tana sona,
Karar wayar khaleel yasa yace "my God this witch. Yafada yana cutting call din. "Fauzy right? "Yes yaya ta cika naci bana son mace mai naci. "Hhhhh you are lucky khaleel fauzy batada laifi and secondly irinta mommy keso Y'ar gidan wasu kaga babanta ne minister na kudi, don haka bakada matsalar mommy kabada kai musha biki bayan nawa. "Yaya why ake Aure? "Hhhh khaleel saboda Aure sunnah ce mai karfi, sannan ba Abinda ke karawa namiji mutunci irin Aure, ga kuma samun natsuwa da soyayya idan kayi dace. "Yaya I don't need any natsuwa a wurin mace ni. "Ah bakada lafiya ne? "Kalau nake kawai bana jin akwai macen da zatasa inji ni a namiji sai kawai in lafiyata ta motsa,. "You are wrong khaleel, kana samun macen da kakeso manhood dinka yadaina kwanciya cikin sauki, domin the moment you fall in love, zaka ji duk duniya ba Abinda kakeso sai kasamu kwanciyar hankali da farin cikin zuciyar ka, you are my younger brother but bazan boye maka ba na matsu ba a daura min Aure da Naziya ba am eager to have her ban taba jin lafiya ta tana aiki ba saida na hadu da ita, don haka kaima duk ranarda ka afka soyayyar wata zaka gano komai. Dariya kawai yayi domin shi yasan lokacin da kawai yake samun erection sai inya tashi a bacci yake sanin he is healthy ba wata Y'ar macen dake daga mai hankali domin bai sawa ranshi ba ma bare Abun duniya ya dame shi.

Cikin unguwar suka nufa wadda tuni yaji wani iri musamman irin kofar gidan dayaga sun tsaya Almajirai birjik sunata karatu ga hasken farin wata daya dallare KO Ina fiyeda hasken lantarkin dake wurin, wayar shi ya daga tareda danna number ta, ba bata lokaci ta daga hade da yin sallama, "Gimbiya kifito ku gaisa da heartbeat tare muke dashi.
Cikin murna ta mike tace "gani nan zuwa yanzu inga wannan kanin namu.
Yana kishingide ko motsi baiyi ba impact bayajin zai iya fitoda takalmin shi wajen wannan unguwar, dole momy tayi spark ai, don ma batazo tagani ba ma da in sama da kasa zata hade

ba Yarda zatayi ba yasani.
Fitowa tayi cikin natsuwar ta sanye da hijabin ta, ta karaso jikin motar dayake tsaye nad'e da hannu, ya zubawa kofar gidan idanu har ta karaso kusa ta d'an tsaya nesa kadan kanta akasa ta gaida shi, "Ina wuni. "Lafiya kalau gimbiya ya kike? "Alhamdulillah, cikin muryar ta mai cikeda natsuwa, kwankwasa glass din motar yayi, ya sauke a natse tareda gyara zaman da yayi kamar wani sarki, kamshin shi mai matukar tsada ya huro tareda muryar shi mai cikeda wasu irin sirrika suka sakata dago kai cikin sauri,
A cikin kyawawan idanun shi nata yasauka domin hasken motar na haskashi dakyau, wani irin sanyi jikin ta yayi Mata domin Sam baiyi Kama da sunan kanin Ahmed ba a wurin ta saidai Yaya, irin cika motar da yayi da kwarjinin shi tareda kamshi da cikar haibar shi, kallo daya ta sauke idanun ta akanshi Wanda tsab da ita gwanace ya isa ta Zane hoton shi, daga ganin shi bazaiyi yawan magana ba, kuma zaiyi miskilanci sosai. Tunanin ta ya katse ne lokacin da taji saukar muryar shi a cikin kunnen ta "Yayana naga Auntyn zamu iya tafiya ko? Shine kalmar data fito kawai batareda gaisuwa ko wani dogon zance ba. Ta shirya sakewa dashi domin karo dankon soyayyar ta a zuciyar Ahmed, amma is impossible yanzu don taki jinin girman kai da nuna isa just because yaje waje karatu, tuni taji yafita a ranta takuma daura damarar Kama kanta da Al amarin shi koda ta shiga gidan nasu,. Saida Ahmed ya leka kanshi tareda zuba mai ido "come on brother kafito mana ku gaisa da kyau, "no mungaisa daga nan ka sallameta mutafi nagaji kasan bangama hutawa ba, yafada a mugun kagare yake subar wurin yanajin warin Almajirai daga inda yake Idan yakara more minutes a wurin he will surely vomit,. Ya lura da yanayin shi don haka a gurguje ya sallameta ta tafi tana mai jin takaicin wannan khaleel din,. Yana tada motar yace "Yaya wannan Y'ar yarinyar zaka Aura? Why?? she is too young for you please, fuskar shi a kwabe, "hhhhh she is perfect banason Auren katuwar mace ko over twenty nafison irinta mutum ya mori kuruciyar ta yafi Amma Idan ka Auri wayayyun mata bazaka mori komai ba, nafison innocent girl da zankoya wa komai,. "Hmmm zakasha aiki wallahi ai wahala zakayi kafin wannan ta iya daukar ka, kuma Yaya iyayen ta suka yarda suyi mata Aure? "Yes saboda mu anan takai Aure tunda ta kammala secondary,.
"What? Yaya this is too much, da Ina nan bazan bari kafara sonta sosai ba gaskiya. "You are too late now, domin inaji a jikina Idan ban Auri Naziya ba zaku iya rasani so ku tayani Addu'a kawai Ina son ta fiyeda tunanin ka nasan you will always support my back. "Of cos brother Insha Allah.

Karfe goma suka isa unguwar su, Wanda mommy Saida taci gaba da fada "kunje ghetto Area ko nasani saiya jamun kai, ka wuce kayi wanka kazo kuci Abinci kaima wuce ka watsa wainnan kayan dustbin kafin ka dawo falon nan kajini ko? Wucewa yayi cikin sanyin jiki ya tafi dakin shi Yana mai jin bakin cikin halin na momyn shi, kasa fitowa yayi saboda rashin jin dadin Abun, shima khaleel kasa cin komai yayi ya kalli momyn dake kan korafi "mommy why please? Ki yi hakuri Ki daina fada akan abunda dole za ayi. "Yes za ayi Amma ni Balkisu bazan bari ya cakuda min iri da na talakawa ba mu zuba tunda dangin ubanku sun nuna sunfini iko akan shi ni kuma zan nuna musu sai naso komai ketafiya mu zuba nida su.
"Momy ji nake kamar in koma bangkok kawai domin bazan iya tsayawa inga d'an uwa na a damuwa ba, please Ki barshi ya samu natsuwa mana. "Khaleel, kana ganin uwa zataki d'an

tane? Ina son Ahmed kamar yanda nake sonka saidai bazan iya kawar da idona akan kwashi kwaram din da zai debo min ba.
Mikewa yayi kawai cikin fushi yabar mata Abincin yayi dakin yayan nashi, a kwance yake Yana tunani, dafashi yayi, dagowa yayi tareda rungume Khaleel din, "brother am worried, bansan irin zaman da zamuyi da Naziya a gidan nan ba, bana so injefa Y'ar mutane a damuwa bayan an bani amanar ta. Bubbuga bayan shi yayi "karka damu Ina nan zan taimaka maka ba Abunda zai samu baby doll dinka. Yafada cikeda dariyar tsokana domin ya kwantar da hankalin d'an uwan nashi,
Shigowa tayi dauke da tray tana fara'a domin taga Alamar Idan tayi sake yaran nata zasu juya mata baya akan zancen Auren nan, Wanda bazata taba Yarda da hakan ba,

"Toh yaran momy ga Abincin nakawo muku ni na damu kuci, kashin awaki, ta ajiye a tsakiyar gadon tareda jansu da hira kamar zata mayarda su ciki, tuni suka ware suka kwashi deshes din, tana cewa "bayan rasuwar mahaifin ku nayi iya bakin kokari na ganin bakuyi maraici ba, Alhamdulillahi yau dukan ku kunkai matasa Abun Alfahari a wurina, forgive your mother Ahmed na dauki buri mai girma akan ku naso nice zanyi maku zabin matan da suka dace daku Amma ka watsa mun duk shirina Ahmed. "Am sorry momy, kuma nayi miki Alkwarin zaki samu Naziya a duk yanda kikeso bazakiyi dakin sani ba yarinyace mai tarbiya da kin Amince da tuni nakawo miki ita ma kingan ta. "Aa tunda ansa rana ai lokacin zaizo don haka basai ka kawo taba, bakomai zan cika burina akan khaleel. "No mommy khaleel ma yanada tashi zabin ai, yafada Yana kashe mai ido, "no no no bana sonta Yaya please meye haka she is my mate fa tare muka kammala karatu why zaka ce Ina sonta ita keso na ni banga Y'ar da zanso ba har yanzu'
Wani irin dadi mommy taji ganin khaleel bazai juyuba a wurin mace tunda ita keso shi bayaso ai irinta takeso, "wow Auta na wacece wannan yarinyar? "Mommy Y'ar gidan minister kudin Nigeria ce, "what? Tafada tana dafe kirji, "Y'ar gidan mai nasara kake fada? Oh my god khaleel, ta rungume shi, that's my son, ka kawomin ita kaji kace tazo inganta Amma ka gama wanke min zuciya d'an nan. Tafada tana mikewa bari inkira Auntyn ku infada mata tafara shirya mana babbar harka ta Fita tana danna kiran kanwar tata mai ra'ayi irin nata. Binta sukayi da kallo suna mugun mamakin halin na mommy, sai kace wadda bata jiku da kudi ba, kullum she is hungry for more, kallon Ahmed yayi da fuskar tausayi yace "why zaka fada mata Yaya kasan am not ready, kuma yanzu tunda taji bazata taba bari insha ruwa in Ajiye cup ba. "Is OK fauzy love you a lot kuma meye laifinta nasan tun lokacin da kuke tare, ya isa haka ka Amince bayan nawa kawai a daure min kai, do you know, Ina mafarkin ganin Auren ka? Ina so inyi witnessing Auren ka inga jinin ka. "Hhh oh come on Yaya kamar wani tsoho na barin wasiyya please tare zamu cika gidan nan da yara, "who know Khaleel? Allah kadai yasan me zai faru gobe, kasan cewa nan gaba kaine zaka rike gidan nan? "Why Yaya? Indai har kana nan bazan taba daukar girma ba saidai in tafiya zakayi dole in rike kana dawowa zanbaka komai domin ka shagwaba ni tuntasowa ta Abu daya nasani shine in saka master card dina inciri duk Abunda nake so ba tareda antanbaye ni me nayi dasu ba, Yaya nasan kudin da daddy yabari bawai haihuwa sukeyi da kansu ba kaine kakara habaka su har suka kai haka kaine jigon gidan nan bazan taba iya Abinda kakeyi ba..... "Shhhhhh zakayi Idan bana nan fiye ma da Wanda zanyi saboda I believe kai jarumi ne kafini iya tafiyar da Rayuwa. "Enough of this discussion kana sani a damuwa. "OK

now kakira fauzy kafara bata kulawa domin tunda zancen yaje kunnen mommy ba fashi, yafada Yana dariya,.

Fita yayi daga dakin yayan nashi yanajin wani iri "Aure? Gaskiya bai shirya ba infact zaiyi ne saboda yayanshi ya insisting kuma koda baison Abu Idan yayan shi na sonshi dole shima ya soshi, Allah kadai yasan iyakar soyayyar da yake wa d'an uwan nashi, kwanciya yayi a kujera a dakin nashi Yana mai runtse idanun shi, so yake ya tuna komai na fauzy da quality's dinta just for Ahmed, Amma first thing da yafado mai a rai yasa ya zabura tareda girgiza kai, "no no no why her?
Cikin Sauri ya dauki wayar shi domin ya k'aryata tunanin shi, fauzy ya Kira, kamar mai gadin wayar ta ta dauka jikin ta na rawa "oh my goodness darling you call me? Tafada tareda Sanya kukan farin ciki, tundazu take kiranshi yaki dagawa har wani zazzabi takeji saboda damuwa tana yimai wani irin so mara misali. Tun isowar ta ake tarairayar ta Amma duk natsuwar ta bata tare da ita,
"Yes I call. Yafada Yana gyara zaman shi domin baisan ma mai zaice ba kuma. "Tank you darling for calling, please Ina so inganka kasan is hard for me kwana daya bansaka a idoba I can't. "Is OK zaki iya zuwa gidan mu gobe yanzu dare yayi. "OK am coming tomorrow tank you darling. Tafada tana buga tsalle tareda rungume filo, tasan yafara damuwa da ita tunda har yake so taje gidan su yanzu, hakurin ta ya fara aiki yanzu. Kwanciya tayi tareda Addu'ar gari yawaye ta ganta agidan su.

Gefen Naziya ta shiga gida da takaicin khaleel, domin yaron mugun d'an wulakanci ne, inba wai gizo idanun ta ke mata ba kamar kallon kyama yake mata, bayan duk unguwar su an shaida tsabtar su, duk da suna fama da Almajirai Inna kulu nada kokarin ganin ta tsabtace gidanta sosai,. Kwance take tana juyi shukrah ta matso gefen ta akan Y'ar madai daiciyar katifar tasu, tace "Aunty lafiya? "Hmm bakomai. "Aa Ina kallon yanda kike ta juyi tundazu kinkasa bacci, meke faruwa ne? "Kawai Ina tunanin yanda zan zauna da Ahmed ne tareda kanin shi shukrah dazu sunzo, baida k'irki irin Ahmed ya cika girman kai da nuna shiyayi karatu a kasar waje. "Ni kuwa Aunty kallon Arziki sosai nakeyiwa Yaya Ahmed fa. "No yafada min Yana da ubangida mai kirkine watarana motocin yake zuwa dasu, "nidai Aunty Ina tantama domin ko tsarin jikinshi ya isa ya nuna Yana cikin hutu. "Ni kuma me zakice dani? Tunda kowa kallon Y'ar masu kudi yakemin a school ko in munfita, halitta ce kawai. "Hmm tom kiyi bacci Ki kyale wani kanin shi Bashi zaki Aura ba.

Washe gari Karfe goma tayi mata a gidan su khaleel cikin tangamemiyar motar ta ta yayi, da kanta ta tuko kanta, da taimakon shi ta zo gidan domin unguwar su ba boyayya bace, momy ta zage sai rawar kafa takeyi an shirya mata tarba Kala Kala, cikin adon jan material doguwar Riga dinkin yayi na yayan masu daula, taci gwala gwalai wuya da hannayen ta tana zabga sheki da kamshi. Ta hadu ba sauki domin ta iya caba ado. Tasamu tarba gefen momy, Wanda koda tazo

gidan bai tashi baccin safe ba,
Momy sai Ina ta saka Ina ta Ajiye takeyi da ita, sai zare idanun ta takeyi taga inda zai bullo.
"Huh khaleel na bacci haryanzu bai tashi ba, kinsan da gajiya a jikin shi.
Shigowar Ahmed ne yasa Momy tace "ka duba d'an uwan ka ko ya tashi ga bakuwar ta iso.
Gaisawa sukayi Yana Kara ganin wayewar ta da kudi Wanda yasan ba yanda za ayi Naziya tazo gidan nan saboda shi, banbancin yayan talaka kuma y'an gidan mutunci kenan da kuma ya'yan masu kudi. Yanzu meye Abun burgewa a nan mace ta nuna rawar kafa akan namiji, idanun fauzy ya gama budewa gaskiya and zasuyi kusan sa'a da Khaleel like he said, wucewa yayi Yana daya sanin bashi goyon baya akanta,.
A kwance ya sameshi Yana kallon saman pop, "oh you wake up? So kazo fauzy is here. "You see tunda Asuba mayyar ta tanbayeni address nafada mata don uwar ta a gidan mu zata karya? Dariya Ahmed yayi, "Auzubillahi yada zagi? "That's why Yaya bana sonta wallahi batada kamun kai Sam ace Karfe goma ta zo wurin saurayi saikace ba iyayen ta a gidan.
"Yanzu dai katashi kayi fresh up kafito tana jira mother in law dinta ta bata big welcome. Tashi yayi ya shige bathroom, like Always Saida ya kwashe hour guda kafin ya fito Wanda shirin nashi ma Saida ya kwashi rabin hour cikin guntayen kayan nashi kamar yanda ya saba.
Cikin takun kasaita da shan kamshi ya fito falon, fuskar shi Sam ba fara'a, "ga shinan yaron kirki ya fito. Mommy Tafada tana mikewa tareda taroshi kamar wani kwai jitake kamar ta goyashi saboda so, jikin fauzy na rawa tace "hy darling kamar ta ruga ta rungume shi takeji. "Tashi kuje dakin shi zakufi sakewa bari insa a hado muku breakfast akawo ciki. Cikin sakewa tace "Saidai baby ni ai mommy kin cika min ciki tun zuwana kike duramin ciye ciye, Tafada tana Dariya, "Allah Y'ar nan, to bakomai ai gidan kune nan.
Zama yayi a falon fuskar shi a cakude yace "ke iyayen Ki basa gidane kika fito early morning?
Kallon fuskar shi tayi tareda yin murmushi duk da tasan maganar banza yafada mata ranta bai baci ba, "mommy na nan dady na nan kuma sun san inda naje. "Really? Kuma basuyi kokarin hanaki ba? "Why zasu Hanani? Bayan su masu goyon baya na ne akan duk Abinda nakeso kasan cewa sun san komai akan ka dady na a shirye yake da katuro neman Aure na, please khaleel ka cika mun burina I promise zaka sameni yanda kakeso zan share maka damuwar ka duka zanbaka gatan da mata basa iya bawa mazajen su just give me chance.
"OK zanturo tunda mommy ta Amince dake and my brother too yanzu kije gida zanturo. Tsalle ta buga tareda Dane shi ta rungume shi kam" don Allah da gaske zaka tura? Oh my god khaleel zanyi suman dadi yau. Tafada tana share hawaye, ban bare ta yayi a jikin shi ya ce "oh come on a gidan surukai kike fa behave yourself.
"Farin ciki ne yamun yawa baby muje mota indakko wa momy tsarabar ta please, Tafada tana riko hannun shi, jinta takeyi kamar anyi mata bushara da gidan Aljannah..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ» *AUREN GADO* ğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
And now AUREN GADO,

ğŸ†“ page

5â*ƒ*£&6â*ƒ*£

..,..... Kaya na kece raini ta kawowa momy tsaraba Wanda tayi ta godiya kamar zata goyata, bayan tafiyar ta bata da wani zance sai na "Ibrahim khaleel bikin ka zamu gwan gwaje ba karya kaga Abun Arzikin da ta kawomin tun ba ayi Aure ba? Wucewa yayi cikin dakin shi domin shi yanzu daya sani yake mara iyaka daya Amince mata tazo gidan su har Mommy ta ganta, yanzu ya boni shikam.....
Wasa wasa Saida aka kwashe kusan sati daya bai kuma daukar wayar taba ta Kira ta turo msg yafi hamsin Yana shareta, momy tayi nacin zancen turawa gaisuwa Yana ja baya, domin shidai bai shirya ba infact baya ra'ayin zama da fauzy she is not his choice zai cutar da itane kawai, bazata taba samun kanshi yanda take soba. Bikin Ahmed da Naziya ya matso gefen gidan su shikadai ke shirin shi da Abokan shi Yana cikin tsananin farin ciki, momy tace bazata wahala akan Y'ar talaka ba, yan uwan tane dai suka fara cika gidan, musamman Aunty zarah, Wanda itace kanwar ta da sukazo hali daya, komai na Aunty zarah sai a hankali tana son gayu da babbar harka.
Duk akwatunan da Ahmed ya hada momy ta sa anrage duk wani gold tasa ancire ansa passion wai basu san darajar su ba talakawa ne. Baida yanda zaiyi saidai farin cikin shi daya Khaleel ya hadomai Nagani na fada a bangkok, don haka sunkai sun boye sai in ta tare, duk wani event mommy ta soke wai yarinyar da ba wayayya ba yaja musu Abun fada bada itaba, don haka ya hakura domin Albarkar Aure yake nema in Allah ya mallaka mai ita burin shi ya gama cika, sannan farin cikin shi daya itama tace bata son wani bidi'a walima ta isheta da za ayi a gidan su,.

Khaleel yana gefe baya cewa komai he just feel boring baiga Abun burgewa a yin Auren ba ba wani Abu da ya bashi sha'awa da har zaiji yanason yayi Auren ma, fauzy sarkin naci tazo tun Ana jibi Bikin ta tare duk inda Aunty zarah ta shiga suna tare gaba daya yabi d'an uwan nashi sun kauracewa gidan suna part din Ahmed saboda jama'ar da suka cika na momy, yaki ko Yarda su hadu da ita, ta d'an ji sanyi ganin tana cikin gidan su kuma no matter what sai sun hadu kafin ta koma gida, ita da ta samu daurin gindi a wurin uwar miji ma, ita kanta tasan mommy batason Auren Ahmed domin ta gama bata labarin ta tas.

Rana bata karya inji bahaushe, Alkawari ya cika, inda Aka daura Auren Ahmed da Naziya akan sadaki mafi daraja, sai muyi fatan Allah ya kade fitina, tunda aka daura Auren ya baro taron ya dawo gidan tareda kulle kanshi cikin dakin su, zazzabi yakeji mara dalili tareda jin wani irin bakon Al amari a tattare dashi, Ahmed nata neman shi, Saida ya kirashi ya dauka yafada mai cewa yana gida, dawowa yayi shima tareda barin Abokan shi ya same shi a dukun kune cikin bargo,

Cire babbar rigar shi yayi ya zauna gefen gadon tareda cewa "bakada lafiya ne? "Fever ke son kamani, "sorry namiji, kasan me? Yafada yana gyara zama, tashi Khaleel yayi ya jingina a jikin gadon yace what my brother? "Burina yacika khaleel, today Naziya is legally mine, but am worried me zata fuskanta a cikin gidan nan, how is she going to react after she find out about everything? "Like what brother? Like our wealth, this big mansion, and mommy. Yafada yana rage murya cikeda tausaya wa kanshi, kamar yarone yaga alawa Ana mai kwalelenta haka yakeji yanzu, yasamu farin cikin shi Amma baya cikin farin ciki.

Matsowa yayi sosai kusa da d'an uwan shi yace "Yaya this is the time da zakayi fighting back, ka tsaya akan ra'ayin ka, you have to talk brother, fight for your love, and Aunty Naziya will be happy bazaka samu Matsala da itaba, in tace zata sama yayana hawan jini bazan raga mata ba cos batasan irin fighting da kakeyi akan soyayyar taba. "Hmmm you known, nafison momy ta barni in zauna a gefen mu, bana son Naziya ta shiga cikin damuwa nasan zata sha wahala Idan akace zata zauna cikin gidan, she can't handle it, bata saba da irin wannan rayuwar ba. And mommy is our mother dole mubi Abinda takeso Auren Naziya da A hannu na yake Dana hakura for mommy happiness, but Allah kadai yasan mai ya boye a cikin Al' amarin,
Yafada cikeda damuwa, Dariya khaleel yayi mai d'an sauti wadda ta Kara bayyana kyanshi sosai, "Yaya this my Aunty is very lucky, tasamu miji mai sonta sosai Anya zaka kuma Aure nan gaba like the way mommy is planning? " no Khaleel bana son Naziyata ta zauna da kishiya Ina so tayi rayuwar y'anci ne, Ina son inganta cikin hutu da walwala, khaleel na gama tsara irin yanda nakeso rayuwar Naziya ta kasance, I love her beyond your imagination, ka tayani son Naziya kaima kamar yanda nake sonta.
Sundauki dogon lokaci yana daukewa yayan nashi damuwa ta hanyar k'arfa famai guiwa, Saida friends suka fara kiranshi ya Fita tareda barin khaleel cikin damuwa, Alwashi ya dauka mai girma akan zai taya yayan shi fighting akan duk Abinda zai daga mai hankali bazai so yaganshi cikin damuwa ba,.

Bai kuma Fita a gidan ba ko sallah a part din yakeyi ya koma ya kwanta, yarasa abunda duk ya

Cire mai walwala da natsuwa bayajin dadin jiki da zuciyar shi baki daya, he just fee like going back to bangkok, baisan mai ke hana shi sukuni ba. Sai Karfe Tara Ahmed ya kuma shigowa dakin ya tsaya a kan shi tareda cewa "brother what is wrong? You look very dull. "I don't know Yaya kawai bana jina cikin natsuwa. "relax nima haka nakeji tundazu but now am fine, your Aunty is here khaleel, finally Naziya is here. Zama yayi tareda rungume Khaleel din yana fitarda hawayen da yarasa na menene ke fitowa daga idanun shi.
Saida ya d'an natsu yace let go and welcome your sister in law. Mikewa yayi ba musu, ya bishi sanye cikin kana nan guntayen kayan da ya canja tundazu.

Gefen Naziya kuwa tunda suka sako kai cikin wannan tafkeken gidan gaban ta ke faduwa gashi gwaggonnin tane suka rakota su uku bisa ga umarnin malam domin baison gayyar tsegumi, kanta a duke yake tunda motar da ta dakko su ta shigo, cikin Y'ar rakiyar ta daya tace "t'irk'ashi wannan gidan mutum daya ne ko dai gidan y'an yankan kai? Sauran suka fara salati, shikenan malam saida Y'ar nan yayi, irin wannan gidan saikace wata unguwar? Saurin daga kanta tayi ta saki baki tareda dafe kirjin ta tana karanto Addu'ar tsari a cikin zuciyar ta, jikin ta shegen rawa yafarayi. Har motar ta tsaya Abokin da ya dakko su yace "Hajiya kufito mu shiga ciki ko? Kamar way'enda kwai ya fashewa a ciki haka suka fito ji sukeyi kamar ace ar su ruga, shi ya musu jagora kowaccen su Addu'ar da duk tazo bakin ta takeyi, rike take da tsintsiyar hannu irin wainda ake rikewa na share dattin daki a wurin sabuwar Amarya bisa ga Al Ada, nasan wasu sun san wannan Al Ada akan ce ta share duk fitinar d'akin kafin ta zauna cikin dakin ta.

Daya cikin gwaggon nin nata tace "kawo Abar nan inrike da ita zankoma Y'ar nan domin ko takarda bazaki shara ba a gidan nan, "Toh ai gidan da waje ma babu ko Alamar d'aud'a bare ciki, ai wajen ma ni yafi dakina tsafta, haka suketa sambatu tsakanin su. Ita kuwa jitakeyi kamar ta ruga da gudu saboda tsoro, wasu irin zafafan hawaye ne ke zubowa akan kyakkyawar innocent face dinta. She is regretting today, wayace ta Amince mai? wayace ta yarda da Auren shi? gashi yayi mata karya yakawo ta gidan da bata taba zuwa kusa da irin shiba.

A falon mommy ce hakimce itada y'an uwan ta, Zarah ce ke gefen ta da kuma uwar y'an kanzagi fauzy, sunayin Sallama mommy tace Zarah kusa katuwar tabar mar nan akan carpet din Idan sun tafi a fita a Y'ar da ita a waje kar k'uma ta shigo mana gida.
Sunji komai a kunnen su jikin su na rawa suka karaso akan tabarmar suka zauna tareda gaida su cikin girma mawa, cikin su daya tayi karfin hali tace "Hajiya toh ga Amanar Y'ar ki nan Allah ya tayaki riko.
"Ni Amanar me zaku bani saikace wata kishiya ta, to kuji infada muku tun mijina nada rai ko zance bai taba zuwa ba bare ayi zancen yimin kishiya, don haka karma ku fara ku jira Wanda ya Auro ta yazo kubashi..... Yauwa ga shi nan ma, Tafada tana nuna shi domin yana fitowa yaji zancen momyn wani irin zafi tareda damuwa zuciyar shi ta shiga. Khaleel ma yaji komai kuma he is not happy da irin yanda mommy takeyi ga su fauzy dake musu wata irin Dariya kamar sunga kashi itada zarah, wani irin baci ran khaleel yayi da Sauri ya matso tareda kallon Fauzy, " ke wace iri ce uban me kikeyi a gidan mu haryanzu baki tafi ba?

"Aa banson shirme Ibrahim, ya yarinya tazo maka k'ara zaka hauta da fada? "Mommy angama Bikin tazo ta wuce gidan ubanta tom. Jikin ta na rawa ta zabura ta nufoshi kamar zata fada jikin shi "no please na dauki permission wurin mommy na ta yarda inyi kwana biyu baby just for you..... "Oh come on, ke meyasa bakisan..... Saurin dafashi Ahmed yayi domin bayason more humiliation agaban y'an uwan Matar shi Dama ita kanta, yanzu yana tunanin how he is going to face her ne ma.
Shiru yayi tareda juyawa da Sauri ya yi cikin dakin shi dake part din momy, ranshi yayi mugun baci dole ya koyawa wannan fauziyar hankali gobe.
Fadin zuciyar Naziya da tunanin ta bata lokacine ma, daya daga cikin y'an uwan mommy ne tace "ku muje in nuna muku part d'in ta, Tafada tana mikewa kafin ya yar ta ta kuma kwab'a, sanyi Ahmed yaji domin yama d'askare yakasa ko motsi.
Suna shiga suka ware idanu domin basuga ko tsinken da sukasa aka kawoba, wadda ta rakosu ce tace "wannan dakin mijinta ne gidan su na waje a can akasa da kayan ta, kamar tasan me suke tunani,
Domin sunga gadajene na kasar waje ba irin nasu d'an wambai ba.

Cikin sauri sukace "tunda munrako ki Naziya mu zamu koma dare nayi, Allah yabada zaman lafiya da hakuri kinji ki rike tarbiya da mutuncin malam Dana kulu domin kinsamu tarbiya dai dai gwargwado kinsha nonon hakuri da kuma mutunci, Allah ya kade fitina. Suka juya cikeda sanyin jiki, riko daya daga cikin su tayi tasa kuka "Don Allah gwaggo karku tafi kubarni ni kumayar dani gida wurin Inna bana son nan gidan. Tafada tana kuka mai cikeda tausayin kanta da Rayuwar ta, daga shigowar ta harta karanto irin Rayuwar da zatayi a cikin wannan gidan.
Shigowar Ahmed ne yasa takara rike ta gam tana gunji. "Ahmed ka rike Amana ga Matar ka mu zamu tafi kaji. Babbar Tafada cikeda tausayin Y'ar tasu, hannu yasa zai rikota tayi tsalle ta koma gefe tareda sakin su tana gyara hijabin ta dogo.
Fita sukayi ta koma gefen dakin ta zauna tareda saka kuka mai zafi da kuma k'ara,
Rakasu yayi a gurguje yadawo domin kukan da takeyi bakaramin daga mai hankali yakeyi ba.
A zaune take ta hada kai da guiwa tana kuka mai ciwo. Zama yayi dabas a gaban ta cikin sanyin jiki, tanajin kamshin jikinshi daya cika ko Ina, takasa dagowa. Hannun shi ya dora saman kanta, da yasa tayi Saurin dagowa tareda ja baya tana Kara hade jikinta wuri daya,
"Am sorry bazan kuma tabaki ba tunda bakyaso, Amma please kiyi shiru haka kukan ki na tabamin zuciya sosai.
Yafada yana kallon yatsun Hannun ta farare tas da sukasha jan lalle Hannun ya mugun burgeshi, ji yake kamar ya riko ya tsotsa, bai taba ganin lalle ya burgeshi ba sai a Hannun ta.
Jin shirun shi yasa ta dago tareda zubamai lashes d'in ta masu kyau da kuma fararen idanun ta da suka cabe da ruwan hawaye, taga Inda yake kallo da ya shagalar dashi sosai. Saurin cusa Hannun ta tati cikin hijabin ta da yabashi damar kallon na fararen kafafun ta, wani irin gauron numfashi yaja tareda d'an matsawa kusa da ita, ta kuma ja baya again. "Why Naziya? Please karki horani a haka zuciya ta zata buga, ki horani ta kowacce hanya but karkiyi min iyaka da zuwa gareki, am dreaming about it always, nasan ni mai laifine a wurinki, Amma kisani ni mai sonki ne shiyasa na boye miki gaskiyar rayuwata Naziya banason in rasaki I love you so much my wife. Yafada yanajin wani irin shauk'i da yanayi mara misali, kallon shi takeyi wani iri kamar

zataga wani Abu daban, batajin zata iya Rayuwa a cikin wannan gidan tareda kuma mahaifiyar shi da itace farkon matsalar data Kara girgiza ta.

"Am sorry Naziya, nasan i'm wrong domin bakiyi planing zama a irin gidan nan ba, yafada yana murmurshi, domin itace mace ta farko dayaga wai batason daula. How silly? Maganar mommy tasa yayi Saurin ja baya tareda tashi tsaye ya kalleta "kazo ka zauna gaban jaririyar yarinya a daren farko to kazo ka wuce dakin d'an uwan ka kowa yasan ango baya shiga dakin Amarya sai anyi budar kai don haka wuce kabani wuri tun ban sab'amaka ba.
Daukar babbar rigarshi yayi yafita jikinshi a sanyaye. "Ke kuma ki tashi kidaina wannan kukan munafuncin kije kisha Ac anzo inda yafi gidan tsoho ga katifa mai numfashi aje a more, kin zo kina kukan munafurci. Tafada tana fita dakin cikin fada. Zubewa tayi nan kasan dakin tasa kuka, "Ahmed yasa ankawo ta inda bazata taba yin mutunci ba,har wani irin ciwo taji gefen kanta nayi saboda kukan da takeyi.

A kwance ya samu khaleel idanun shi a bude yana kallon saman dakin wani irin zazzabi yakeji har yanzu Wanda yarasa dalilin faruwar shi, jin takun d'an uwan nashi yasa yayi Saurin juyawa ya kalle shi, "Yaya ango me kakeyi a nan yau? Yanda yaga hawaye tareda ganin damuwa kwance a fuskar d'an uwan nashi yasa yaji tuni zazzabin shi ya tafi, tashi yayi cikeda damuwa yace "Yaya taki kulaka ne? Zan bata mata rai Idan ta nemi jefamin kai cikin cikin damuwa.
Yafada jikinshi na rawa domin yaune karo na farko dayaga hawaye a idanun jarumin yayan nashi mai hakuri.
"Mommy. Yafada yana Rungume d'an kanin nashi domin yasamu sauki. "Me tayi kuma?
Fadamai yayi yana jan numfashi, "oh Mommy, Bari inje inyi mata magana. Yafada yana kokarin tashi tsaye, rikeshi yayi tareda girgiza kai, "karkaje tace Al Ada ce sai gobe zan shiga wurin Matata.
"What kind of Al Ada? "Budar kai. Zabura yayi cikin haushi "let me talk to her. "No leave it, just do one thing please go and check on her please she was crying.

"No kabarta zatayi shiru ka kwanta yau ne kawai tunda ka hanani inyi mata magana.
"Please go Ina so inji ko tadaina kuka, inaji a jikina tana can tana kuka.
Bayason musu, especially da yayan nashi don haka mikewa yayi kawai ya fita.
Ba kowa a falon yanzu duk Suna cikin part din mommy Suna hira da shewa, girgiza kai yayi yana tunanin Abinda zai aikata gobe a gidan halin shi dasuka sani bai canja ba bayason rubbish. Tundaga falon yakejin kukan ta kasa kasa. Wani irin zafi yaji a zuciyar shi, da sauri ya shiga dakin, a kwance take a kasan kamar yanda take tundazu saidai yanzu Ana iya ganin kayan jikinta domin duk hijabin ya tattare ya koma wurin cikinta, zaka iya ganin perfect figure dinta, Wanda ko Ahmed bai taba samun damar ganin ta haka ba, kullum tana cikin hijabi, akan kafarta idanun shi yafara sauka.
Wanda wani irin attraction ya rika jansa ya kasa Cire idanun shi, "first time da henna designs ya Bashi sha'awa, ga kafafun ta kamar na turawa a mulmule farare tas dasu, "Wow she is Unique, zuciyar shi ta furta. Domin tsarin jikinta da yake gani, bai taba ganin small body with a perfect shape ba like her.
Motsinta yasa yadawo hayyacin shi cikin Saurin tareda tsorata ta zuba mai ido, tana zarewa,

domin ita bata taba ganin katon namiji irin shi da guntun wando da singlet a gaban ta hakaba, wane irin gida Ahmed ya kawota, da Sam ba tsari ba wani sanin ya kamata. Saurin jan hijabin ta tayi kasa tana mikewa kukan nata ya dauke dif, fuskar shi mai natsar da yaro mai kukan banza, tuni ta hadiyi wani irin miyau, she knows he's khaleel domin ganin farkon da tayimai bazai taba bacewa a idanun taba. Gaba daya jitakeyi ya cika mata dakin da girman shi, ga fuskar shi mara walwala, idanun shi masu dauke da wani irin sinadari Wanda batasan ma ma'anar shiba. Juyawa tayi ta Bashi baya ganin ya dauke kanshi batareda ya iya cewa komai ba. Saida ya dauki lokaci kafin yagama tunanin yanda zaifara yimata magana, cikin karfin hali yace "good tunda ba kuka kikeyi ba, Yaya na is worried sosai shiyace inzo in dubaki, tunda kinyi shiru shikenan, yafada yana tafiya batareda ya kuma kallon gefen taba, a falon yaci karo da ledar da yayan shi ya Ajiye Wanda kowane ango ke shigarwa Amarya da ita, dauka yayi ya koma, dai dai ta kuma juyowa, idanun ta suka kuma cin karo dashi, wani irin Saurin juyawa ta kumayi ledar ya Ajiye "you have to eat karki kwanta da yunwa Yaya na zai damu. Yafada yana fita Hannun shi cikin pocket din guntun wandon nashi.
Cikin sauri bayan ya fita ta dannawa kofar key domin Allah yagani batason ganin shi again,..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
And now AUREN GADO,

Ga masu son su biya ga account details dina, *NAFISA HASSAN SANI 7304736012 @ FCMB*

ğŸ†“ page

7â*ƒ*£&8â*ƒ*£

..... A tsaye ya samu Ahmed yanata sintiri, yana ganin shi ya rikoshi "kuka takeyi ko brother? Yatanbaya cikeda damuwa. "No Yaya tayi shiru nabata ledar da ka Ajiye a falon relax am sure zataci ta kwanta. Yana gama fada ya haye gadon ya kwanta tareda juyawa yayan nashi baya. "Tank God, and tanks to you brother. Yafada yana d'an samun natsuwa, bathroom ya shige yabarshi idanun shi kur, baya kojin bacci, saida yaji fitowar Ahmed ya rufe idanun shi kamar maiyin bacci. Saida ya shimfida dadduma ya fara jero sallolin nafila tareda Addu'oi masu zafin akan Rayuwar shi data Matar shi, ba Abinda yake nema sai farin cikin Naziya a wurin Ubangiji tareda neman zaman lafiya a tsakanin su.
Ganin har Karfe biyu shima yakasa baccin ya diro tareda dauro Alwalar ya tada sallah shima, haka gefen Naziya bayan ta kulle bathroom tafara nema saida tayi da gaske ta gano inda zata latsa ruwan yafito kafin tayi Alwala tafito, dadduma tagani a gefe da Qur'ani ta tada sallah, saida tayi raka'a biyu ta zauna tana jan k'ira'a a zuciyar ta. Domin fadar manzon mune aduk halin da mutum ya shiga to ya koma ga Allah,

:(Fadhkuroonee adhkurkum washkuroo lee wa laa
takfuroon
"So remember Me; I will remember you. And be
grateful to Me and do not deny Me.) :
Wanda duk ya tuna da ubangiji shima bazai manta da shiba a duk halin da yashiga.
Sai Asuba ta tada sallah saida tayi nafila raka'a biyu kafin farillah, taci gaba da karatun ta, sai Karfe shida ta kwanta a kan daddumar, wani irin bacci mai cikeda salama ya dauke ta domin Qur'ani maganin damuwa ne Idan har kayi Imani da Allah.

Haka gefen Ahmed da Khaleel basu runtsaba saida sukaje Mosque suka dawo, saida Ahmed ya duba kofar dakin nashi yajita a rufe, bai bugaba domin kar momy taji, dakin khaleel suka koma, kwanciya yayi yana murmurshi "daga yau bazan kuma kwana nikadai ba, ko tareda kai "am going to sleep on my wife shoulder, yafada with so much excitement, Runtse idanun shi yayi tareda yin shiru yarasa abunda yakeji a Ranshi, a haka dai sukayi bacci har zuwa Karfe Tara na safe, Wanda Ahmed din ne yafara tashi domin ya matsu ya fita yaga halin da Naziya ke ciki.
Saida yayi wanka ya tashi Khaleel "get up sleeping beauty muje muga momy inaso in duba Naziya Yafada yana goge fuskar shi da towel, tashi yayi yana salati tareda wucewa batareda ya furta komai ba,

Saida yayi wanka ya fito, yasamu har Ahmed ya shirya sai kyalkyale jikin shi yakeyi domin so yake ya burgeta, Idan ta ganshi tasan bata zabi mijin banza ba. Shiryawa yayi shima khaleel cikin shigar tashi ta fama, kallon shi Ahmed yayi "yakamata kasa manyan Kaya zamuje gidan malam later gaisuwa tareda godiya inaso muje tare dakai. "no please banason zuwa wannan unguwar Yaya."For me please. "OK for you. Amma bazan sa kayan zafi ba sai zamu tafi. "No problem muje".

Naziya saida mai aiki ta tasheta ta tashi cikin sauri ta bude kofar tace "Hajiya tace kifito kitayamu aikin breakfast. Tace tom tareda gyara zaman hijabin ta ta fito, tareda taimakon mai aikin suka shirya irin Abincin da sukeci wainda idan aka barta bazata iya ko kunna gas din ba bare sauran kayan wutar. Wurin gasa crabs din khaleel ne tasha mamaki, domin ita tsawon Rayuwar ta bata taba ganin ta ido da idoba sai a text book, da kuma manyan d'anyun crayfish da Sam basuda kyan gani a idonta tana kallo aka gasa su a oven aka yanka mai salad da kuma tumatur manya aka jera su crayfish din da crabs din akan ganyen, so takeyi taga wazaici wannan Abun, sai kwai da ko kadashi ba ayiba ansaka mishi kayan kashe k'arni, kawai fasashi akayi a frying pan aka d'an barbada chilli powder asama kadan.
Tana gefe tana kallon ikon Allah sai d'an abinda zata iya yi kawai take tabawa kamar fere dankali da yanka kayan miyan da za'ayi source dasu, Karfe Tara da Rabi suka shirya komai a dining table, dai dai lokacin momy ta fito cikin shigar Alfarma da gwala gwalai, ta kalleta cikin fada, " Ina fatan bada wainna kayan kika shiga kitchen ba? Kanta tayi Saurin dukarwa tareda gaida momyn Ina kwana. Tace "mu nan wanka akeyi sau goma in antashi domin akwai ruwa basai anje tuka tuka ba ko rijiya ba don haka karki kuma shigar min kitchen da datti, yanzu ma Allah yasa khaleel ya iya cin abincin nan kin shiga kina yimai kakkabi da wannan katon hijabi kamar wadda keda nakasa, ke Kodai wannan kyan naki a fuska ne rufa rufa akayiwa Dana a cikin hijabi? Oya Cire shi yanzu ingani wallahi inkinada ko kuna guda dayane yau sai kunbiya mu sadakin mu. Tafada dai dai y'an kanzagin ta na fitowa tareda kuma su khaleel da suka sawo kai cikin falon.
Dariya Fauzy tayi tace "may be akwai inda keda illah Mommy, Tafada tana tafawa da Aunty zarah dake biyeda ita, "kwarai kuwa a Cire kar a cuci dana,.
Cikin sauri ta Cire hijabin kanta bako d'an kwali sumarta mai tsananin tsawo da kyau kamar buzuwa na nade cikin sabon ribbon, gashine kwance har gaban goshin ta Wanda ke sanarda kai akwai sumar. Kayan jikinta kuwa atamface dai dai talaka wadda malam ya dunka mata tafitar biki akalla zatakai dubu goma, domin kawai ya fitarda Y'ar tashi ranar Aure ya dunka mata su kusan guda uku,
Atamfar mai golden ce blue, dinkin nata nazamani mai kyau na Amare Riga da sket ya mata cif mai d'an shoki ta baya perfect figure dinta ya fito fiyeda tunanin masu sa idon dake wurin, duk sun gama yarda cewa Naziya mace ce kuma kyakkyawa ajin farko ba kamar na Y'ar talaka ba.
D'askarewa Ahmed yayi domin yau ne yasan ya tsinci dami akala, yau yake ganin wacece Naziya, wani irin yanayi yakeji, burin shi bai wuce ya ganshi daga shi sai itaba a kebe ya samu ya rage damuwa da wahalar da yasha kafin yasameta.
Gefen Khaleel kuwa bazaka taba gano komai ba sai tsantsar bacin rai da bakin ciki Wanda yarasa dalilin shi, cikin zafin zuciya ya kalli fauzy " you come and get lost from my house, angama biki ki koma gidan ubanki right now. Yafada cikin karaji da fitinar da ba Wanda yataba

jin yayi irin ta. "Aunty zarah I thought Aure kikeyi kema kije gidanki mungode da zumunci we need privacy that's enough.
Fadan da yakeyi ba Wanda za a iya tsaya wa ayi musu dashi bane, mommy ma mamaki takeyi tareda kallon shi saida ya kuma cewa "I said get lost. Tace "khaleel " cikin tsawa, "ka kiyaye ni ba inda zasuje, kuma don iskanci ka manta Zarah kanwa tace uwa daya uba daya, don't forget your manners and Fauzy, karka manta she is your bride to be. "Momy tell them to stay within their limit, ita Aunty zarah ba girman mu tayi ba I can talk to her any how, and Fauzy Auren ta kikeso inyi zan iya fasawa anytime idan naso, don haka before I change my mind leave". Yafada yana nuna mata hanya.

"Innalillahi, ni Balkisu daga zuwan ki kinfara hada mana gida" Tafada tana nuna Naziya, lallai kuwa yarinya kintabo tsuliyar dodo, Ahmed kaga Abun da ka debo, yarinya mai farar kafa bad luck to our family. Wani irin zafi yakeji tareda kallon momy yana girgiza kai, "no mommy me tayi, Ina bin duk Abinda kikeso momy saboda ingama lafiya please na rokeki kibarmu mu koma gefen mu zamufi samun kwanciyar hankali.
"Naga takaina ni Balkisu kaga ni ko yarinya ta shigo da mugun Asiri, toh wallahi kunyi kadan keda iyayen ki zan nu na muku ni Balkisu in kun kwana akan buzu ni akan dadduma nake kwana mu zuba, daga shigowar ki Dana yafara musu dani. "Momy please stop" this drama is enough. Khaleel yafada yana matsawa kusa da ita tareda riko Hannun ta Alamar lallashi domin yaga Alamar nuna fushin su b'ata Al amarin zai karayi, domin kwanciyar hankalin d'an uwan nashi yace "Fauzy kuzo muyi breakfast Aunty zarah please komai ya wuce OK. "Dama Ibrahim kai raini ne dakai tun kana yaro shiyasa Ahmed yafika Abun kirki.
"Oh am sorry my Aunty yafada yana Dariya kadan, zama sukayi, ita kuma ta wuce dakin da ta kwana tana share hawaye masu ciwo da dumi, domin all her life bata taba tsayawa gaban mutane ba hijabi ba, yau gashi an wulakanta ta saboda me? Saboda tana Y'ar talaka, shiyasa batason tasa Rayuwar ta inda tafi karfin ta.

Ahmed kokarin bin ta yakeyi mommy tace "zonan d'an anace shiryawa zatayi tafito kuma kiyi sauri don bazamu tsaya jiranki ba hamshakiya. Komawa yayi ya zauna tareda zubawa bayanta ido har ta shige, ga koshi ga kwanan yunwa shine wannan.
Gudun fada yasa tayi wanka cikin sauri bayan ta gano inda zata Tara ruwan, domin ko bakomai tanajin labarai tareda gani a TV sometimes duk da ita ba ma'abociyar kallo bace, bisaga Al'adar gidansu na riko da Addini tareda kaucewa duk wata Rayuwa ta nasara, sai gata a yau tana Rayuwa cikin nasara baki daya domin a ganin ta gidan baki daya ma Rayuwar nasara sukeyi.

Ganin bataga kayan taba yasa ta mayarda na jikin ta, tareda daura d'an kwalinta ko mai bata shafa ba ta fito cikin sauri. Suna zaune yanda ta barsu, sai Ahmed da ya rike Haba yana kallon ta inda zata bullo, Ajiyar zuciya yayi ganin fitowar ta, yanzu ya samu damar karewa gabanta kallo da take tahowa toward him, Ajiyar zuciya ya jera tafi goma, domin shidai yana ganin samu da rashi ga mace Allah ya Bashi ta huce takaici Amma mommy taja layi, "bazamuga tsiya ba mudai ki kwana da Kaya ki tashi dasu ki shiga kitchen kifito yanzu kuma kizo ki zauna cikin mu kina tsami, maza ki koma ki canja Kaya, Ahmed kaga illar Auren irin wannan yaran ko? yanzu da akwai bakon ido da munsha kunya. Shiru tayi takasa cewa komai. Cikin sauri Ahmed yace

"mommy kayanta na part din mu ne shiyasa duk can aka kaisu, "oh kace kagama planing din tarewa acan to kaje ka kwaso mata kayan zuwa nan ban Amince maka zama da wannan ignorant din ba a cikin wannan gidan ba sai in kashirya yin wani Aure kwa tare da Amaryar Arziki ba wannan ba, Tafada tana nunata sama da kasa, da Alama kalaman mommy nayiwa khaleel zafi fiyema da Ahmed domin yasan d'an uwan nashi hakuri ne kawai yasa yakasa cewa komai shikuwa hakurin shi yafara karewa. "Mommy please am hungry ko intafi ne waje inci yau bazamuci breakfast din ba? "Kizo ki zubawa kowa yarona najin yunwa kinja kin tokare. Matsowa tayi jikin ta NA rawa, " gefen da Khaleel yake ta fara nufowa kanta akasa bata ma iya kallon idanun mutanen, infact haryanzu bazata iya tantance kamannin fuskokin su ba. Wani irin kamshin turaren wuta d'an mai duguri mai sanyin kamshi, Wanda ya Kama jikinta ya daki hancin shi, Hmmm yana matukar son kamshi a Rayuwar shi, ga wannan da yake shaka mai wani sirri na daban.
Plate ta dauka ta fara zuba musu chips din dankali da source, Ahmed so yake ta kalleshi, just once ko zaiji sauki domin Allah kadai yasan Abinda ke cikin zukiyar shi, damuwar da yake ciki bata faduwa.
Saida ta zubawa kowa tazo kan Khaleel, ya daga mata hannu tareda janyo tarkacen shi gabsnshi domin shi cimar shi daban take a gidan, zuba mai ido tayi tana kallon shi zaici wannan Abun? "Naziya ". Ahmed ya Kira sunan ta cikin wani irin kashe murya tareda tsareta da idanu, batada choice dole tadaga idanun ta takalle shi, nuna mata kujerar gefen shi yayi tareda mata Alamar tazo ta zauna. Ba musu ta nufi gefen shi, mommy nata hararar ta kasa kasa, Su fauzy kuwa kallon village girl suke mata, zama tayi a takure da kanshi ya zuba mata Abincin tareda hada mata tea very thick, "toh shanyayye ita batada hannu ko? Inji mommy shidai shiru yayi, saboda jin ta a zaune kawai a kusa dashi yaji ya d'an natsu kadan.

Tsit kakeji sai karan cokula, ganin hankalin kowa nakan plate ya sauke left hand dinshi tareda dafe Hannun ta daya dake Kan laps d'in ta, gam gam, wani irin zabura tayi, Wanda khaleel ne kawai idanun shi yagani, idanun ta a gefe take kallon Ahmed din tareda kokarin kwace wa ta kasa , wani irin bakon Al amari takeji domin zata iya cewa wannan ne karon farko da namiji ya rike mata hannu, gashi ba rikewar kawai yayiba wani irin murzawa yakewa Hannun kamar kwadayin shi akan Hannun yake,
Har wani irin zafi takeji, shi kuwa laushi da santsin Hannun ne ke rikitashi domin tuni yama daina cin Abincin, jiyake kamar ya dauketa suyi tsuntsuwa subar wurin, he really need privacy with his wife.
A haka kowa ya kammala batareda taci ko cokali daya ba, kuma yunwa takeji ta fitar hankali, domin tunjiya batasa komai a cikin taba, domin ko kallon ledar da khaleel ya Ajiye mata batayi ba.
Shiyafara mikewa tareda barin wurin, saida yaga hankalin mommy zai dawo kanshi ya saki Hannun tareda gyara natsuwar shi da ta dade da zuwa bulaguro sanadin jin shi cikin wani irin yanayi mara misali, bai taba jin kanshi in needs kamar yanzu ba, Hannun ta ya rike duk ya rikice idan ya Rungume ta fa? Ai suma kila zaiyi kai tsaye,

Saurin tashi tayi jin ya saki hanun tayi daki cikin sauri, dakyar ya karasa breakfast yana bawa kanshi laifi domin yaga ko tea bata shaba, mommy ta kalli plate din ta tace "Ahmed aiki ya

sameka saikaje ka siyo mata kosai da koko kasan ba asaba da shan shayi ba bare kuma chips, ta fada tana barin dining din zuwa tsakiyar falon ta hakimce tareda su fauzy,
Shigowar y'an matan kawu modu ne yasa ya saki fuskar shi tareda tasowa, yana murmurshi "sai yanzu zakuzo ganin Amaryar? "Yaya Ahmed ai jiya ma muna gidan nan saboda kana hidima ne yasa baka sani ba. "OK kun fita. "Ina Amaryar mu? Tana ciki, and please muje kutayani kwaso kayanta zuwa nan. Yafada yanayin gaba, binshi sukayi,Suna hira a tsakanin. Akwatunan da yayi mata ne kawai ya kwaso mata yabar na Khaleel a can, gudun fitinar mommy, domin ko wainda yayi hanawa tayi akai wai kar su kwaso musu kudin cizo da k'uma, inda Allah ya taimake shi malam yace bayason bidi'ar kawo akwatin abarta a dakin ta idan ta tare, Wanda hakan ya mugun sanyaya mai rai. shigowa yayi da katuwar akwatin zai shige tareda kanin nashi, "Ahmed Ajiye a nan zasu shiga da ita ciki. "Momy bazasu iyaba tanada nauyi sosai. Zabura tayi tace "Zarah kuzo ku kamamin, yana gani haka suka dauka tiki- tiki saboda dai kar Abarshi ya kebe da Matar shi, yadawo tsakiyar falon ya zauna tareda dafe kanshi, Allah yagani angama shiga Rayuwar shi, Mutum yayi Aure Amma jin dadin Aure ya gagare shi.
Fitowa tayi tana sababi tareda zama gefen shi, "na fada maka miji baya zuwa wurin mace ba ayi budar kai ba, don haka karka sake inga kafarka cikin dakin nan bada izini na ba.
Saurin kallon ta yayi "mommy ai yaune kuma shike nan ko? "Nadai na fada maka kar inga kafar ka ciki inba haka ba zan daga maka nono. Tashi kawai yayi yabar gidan cikeda tsantsar damuwa da kuma bacin rai.
Uwa uwace shiyasa kawai baida yanda zaiyi saidai ido.
Dakin Naziya kuwa ta saki jiki sosai da y'an matan wainda sun Cire mata damuwa da kadaici tareda kewar gida, su suka ware suka shirya mata komai na kayan ta a wardrp, da kayan shafan ta wa inda tasan sunja kudi sosai, kayan akwatin sunyi matukar girgiza ta domin saiti biyu ne, wai don ma mommy ta hana shi yayi yanda yaso kenan. Su suka sata ta caba Ado tareda ciro mata wani tsadadden less baki, Abunka da farar fata tuni ta haska ga dinkin kamar angwada ta, suka murza mata dauri, tafito gwanin burgewa, Karfe daya gidan ya cika da y'an uwan ta masu kawo gara Wanda sun kure kokarin su sunyi dai dai gwargwado, inji bahaushe yace ka fada wa mai zuciya biki ba mai dukiya ba.
Mommy ma tasan sunyi kokari saidai hassada da idan bakason mutum ko tsarki da madara kake mai bazai taba kaunar kaba..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
And now AUREN GADO,

Masu son su biya ga account details dina ,
NAFISA HASSAN SANI 7304736012 @ FCMB Sai Ku min magana ta wannan number 09069200154

ğŸ†“ page

9â*ƒ*£&ğŸ”Ÿ

..... Khaleel yabar gidan bayan ya gama breakfast shima domin shikadai yasan damuwar shi, bayajin zai Amince da wannan Auren tareda ci gaba da zama a Nija yana ganin irin wainnan Abubuwan, he can't take it. Saida Ahmed ya nemeshi a waya yafada mai inda yake a can suka hadu, dafashi yayi "why kafita bayan nafada maka zamuje gaisuwar surukai? "Yaya tunda na duba naga baka gidan I know you're hurt shiyasa nafita, and please Yaya don't just sit down and watch things ka dauki Action mana. Yafada yana kallon shi cikin damuwa, murmurshi Ahmed din yayi tareda cewa "my brother, a wurin wa zandauki Action? Don't forget she is our mother dole mubi ta duk yanda takeso. "Its unfair", haka zakaci gaba da kallon Abubuwa nafaruwa till when? "Ko zuwa yaushe ne Am ready inyi mata biyayya khaleel am ready to obey what ever she said, can't you do that for your mother? I can't Yaya gaskiya am seeing everything you need privacy with your wife amma an tauye ka, yakamata tunda ka rabota da y'an uwan ta ka bata kulawa, itama tanada right akan ka fiyeda mommy don haka dole ka kula da yarinyar nan, kasan yanda kukayi and you disappoint her daka boye mata gaskiya I know she is in pain, please Yaya she needs your comfort.

"Hmmm my brother has grown up, yafada yana rungume shi gam gam tareda jin dadi, "khaleel kasan how hard am trying? Banda zabi ne, Amma Inna fada maka bana damuwa k'arya nayi, "I needs my wife like any other man da yayi sabon Aure I want her very badly, yazanyi in iya Cire idanuna akan matata bayan she is closer to me, this is the hardest time for me. Yafada yana tunano yanda yaganta dazu without hijab, her shape her chest her hair, oh God! he has

the most beautiful girl as his wife.

Rungume shi khaleel yayi tareda cewa "I will help you through this brother. "Thank you". Daga nan suka wuce gidan kawun su tareda godiya akan hidimomin shi, ya musu Allah yasanya Alkhairi, tareda nasiha mai zafi akan zaman Aure, kafin ya dawo kan Khaleel, "kai balkisu Tafada min komai akan Y'ar gidan mai Nasara, and am happy da zakayi Aure kaima, kuma ni bazan hanaka Auren zabin kaba, zankuma shige maka gaba har kaima Allah ya cika maka naka burin, Amma Ahmed kayi sa'ar surukai nagari Allah ya kad'e fitina, kunje kun gaida su? " yanzu zamuje kawu friends dina ma na jirana daga nan can zamuje. "To to to, kuje Allah ya muku Albarka, zan Dauki Abokina mu samu ganin mai nasara, idan komai yayi dai dai zanfada muku. "Mungode sukafada baki daya, Wanda itace kalmar farko da ta fito daga bakin shi bayan gaisuwa domin Allah yagani Fauzy saidai idan Allah yayi baida ta cewa, fuskar shi kawai zaka kalla kasan baya farin ciki. "Relax brother, bakasan me zai faru gobe ba, kayi hakuri may be haka Allah ya tsara dole zaka yi Rayuwa da fauzy, don haka ka nemi zabin Allah, inba Alkhairi bace sai ya baka wata. "Mata biyu Yaya? "Yes kaiba namiji bane? " no please kai kace bakason biyu nida nake kanin ka inyi biyu, ni mace daya is OK for me. "You can handle two wife's nasan kanina, I believe in you. Yafada yana Dariya, haduwa sukayi suka tafi jakara tareda Abokan Ahmed din. Wanda khaleel ya daure har cikin gidan da Akwai Sauran mutane suka shiga suka kwashi gaisuwa cikin mutunci da girma. Wanda idanun shi nakan Inna kulu wadda yasani ba tantama kyanta Naziya ta dakko, haka yabi Shukrah da kallo yana ganin tsantsar kamar su tareda yayyin ta masu Aure duk Suna Kama, Amma no one like Naziya she is more beautiful a cikin su.

"Shiru yayi kawai yana nazari har suka gama gaishe gaishe suka fita waje domin gaida Malam dake dakin zauren tareda manyan Almajiran shi, a nan khaleel ya Amince yes yayan shi yayi Aure inda ya dace, dattijo na gari mai mutunci, nasihar farko itace "sai kayi hakuri da duk wani shiririta ta mata zakaci ribar zama a duniya ka rike gaskiya kabi maganar mahaifiyar ka kagama lafiya, Allah ya kade fitina ya kuma baku zuri'a tagari. Wani irin girman tsohon khaleel yagani tareda tsantsar mutuncin shi, tabe bakin shi yayi tareda kada kai kawai Wanda shikadai yasan meke zuciyar shi.

Saida sukabar gidan sukaje harabar katon gidan nasu ya dafashi "Yaya I don't know much about Al Ada, Amma nagani Ina yaro idan Ana Aure a familyn mu idan ankai Amarya the next day y'an uwan ta nazuwa, why your bride basu zoba kuma sun san zata bukace su? "Hhh Khaleel mutunci kenan da gudun Abin duniya na gidan su Naziya bakaga komai ba ma Indai zuri'ar malam Abubakar ce, "but Yaya naga younger sister d'in ta ko ita batazo wurin Y'ar uwar taba. "Kasan Abinda momy tayi musu jiya shima zai iya sawa su hana wani zuwa gidan nan. Yafada fuskar shi na canzawa,
"Is OK muje ciki yau dai zaka tare dakin ka enough of the budan kan. "Hmm Allah yasa. Anyi la'asar koda suka shiga gidan, Wanda tana takaiwa da dawowa daga kitchen zuwa falo domin shirya Abincin Dare, duk Abokan hirar nata suntafi, gashi momy tace tayi tuwo miyar kubewa da kuma farfesun kan rago.
Tana cikin Adon ta sosai haryanzu tareda baza kamshi kamar Amarya. Har zata fito cikin

kitchen din taji muryar su Suna Dariya ta koma, wani irin zafi takeji a kirjin ta she thinks kamar da gangan ma Ahmed ya Aurota ya kawo cikin gidan su domin ta wulakan ta, toh yayi kuskure, kuma zata nuna mai Abinda Aka koyar da ita daga gidan su, zai gani tarbiyar Inna bazata taba faduwa kasa banza ba, she cried yerstaday, kuma bazata kuma zubar musu da hawaye ba, aiki kuma Alhamdulillah, bazai gagare taba domin ta horu girki ma zatayi Amfani da nata salon domin gujewa damuwa, da izinin Allah zata basu mamaki.
Da taimakon mai Aikin take Amfani da kayan wutar, tsab tuwon shinkafa ta dora Wanda tasa mai ruwa wadatacce da zai dahu lugub, sai kan ragon data wanke tas ta zuba a wuta tareda neman kayan kamshi na gargajiya ta daka ta watsa, tuni kamshi ya cika ko Ina.
Tayi dai dai kuma hankalin ta kwance tana aikin ta, ya shigo ciki, turus yayi yana kallon ta cikeda mamaki domin dai bai kamata ta shiga kitchen ba, tana Amarya kuma kwana daya a gidan miji a ce tafara aiki bayan ga maids cike da gida, wucewa yayi wajen firij saida ya bude taji motsi tareda Saurin juyowa tagan shi ya daga gorar ruwa sama yana sha, Saurin juyawa tayi tana cigaba da aikin ta, domin ta lura ya cika girman kai, and she promise zata kiyaye shi tunda baice Mata ba itama bazata taba yimai magana ba.
Har ya Ajiye gorar ya juya Abun shi yana mamakin halin ta, ko kallo bai ishe taba Wato? Hmmm".

Karfe shida ta kammala tuwon tareda miyar kubewa lafiyayya da taji namomi a ciki, maid tace"Aunty Saura Abincin master karami. Kallon ta tayi "da daren ma bayacin Abincin mutane? "Yes saidai Ana dafamai ruwan tea ya hada ko coffee. Shiru tayi kafin tace ta kwaso shrimp d'in da su crabs, da kanta ta gyara ta wanke tas tasa ta gyara Mata Y'ar citta dasu garlic tace ta daka mata su da Albasa da tarugu saida suka daku ta d'an sa ruwa ta shafe su tsab harda spices, ta saka a oven, ta saka lowest yanda bazai kone ba kafin tayi wanka, maid din ta yanka mai salat ta wanke su tumatur.
Dakin ta ta koma ta tube tareda shiga wanka, cikin Sauri Sauri, ta dauro Alwala domin ankira magrib, bata tsaya yin dogon Azkar ba ta mike cikin Sauri ta canja zuwa wata doguwar rigar Atamfa mai flay cikin dinkin da malam ya Mata, tayi kyau sosai,
ta daura dankwali ta fito. Yanzu duk sunfito Suna falon momy dasu Ahmed harma da Khaleel, yana Rungume da katuwar tab yana dannawa, Suna hira kasa kasa su duka. "Toh hamshakiya abamu Abinci yunwa mukeji. Mommy ta fada. Muryar ta a kwance tace na gama momy zan shirya ne kawai a dining. "Noo ki sa maid ta shinfida mana dadduma anan bazamu hau saman ba,.
Bakomai yasa tace hakan ba saidan kar su zauna kusa itada Ahmed. Domin sa idawan ta dazu sun tsegunta Mata kamar yana rike Mata hannu ta kasan table, Wanda bazaka taba gane munafukan sungan suba.
Tunda ta fito Ahmed ya zuba Mata ido wani irin numfashi yakeja a ciki, domin Allah yagani shiba dutse bane, idanun shi ko kyaftawa basayi akan kirjin ta da yake gani, tareda Ayyana irin cika mai Hannun da zasuyi, har wani irin Aunawa yakeyi, he know dai dai Hannun shi ne. Kallo ta yakeyi sosai har mommy ta lura. Tareda Ayyanawa a ranta "Ahmed Indai ni Balkisu ce na haifeka bazaka taba hadamin iri da yar matsiyata ba muje zuwa.
Tayi k'wafa, Saida ta jera komai tareda turawa khaleel nashi cimar ta koma gefe ta zauna itama, gaba daya kamshi ya gama cikasu, ita kanta mommy miyon ta ya tsunke, wani irin

murmurshi Ahmed keyi na jin dadi, domin yana ganin yanayin Abincin yasan zaiyi dadi sosai. Khaleel ma kallon Abincin shi yakeyi, domin ba ataba hadamai shi da komai ba yana ganin yanda yayi wani irin kyau ga Aroma na tashi. Momy kallon yanda yake kallon Abincin tayi tace "idan bazaka iyaci ba ayi maka wani? "No is OK, yafada yana daukar fork yafara ci. Wani irin test yaji tareda dadin da baitaba jin yayi ba, domin ta yimai hadin da kowama zai iya ci. Kallon shi Ahmed yayi "yadai brother its good? "Of cos Yaya she is a wonderful cook. Batareda ya kalli side d'in ta ba.
Shiru kakeji a wurin kowa na zuri, saida taga kowa baiyi complain ba itama ta debi kadan tafaraci, Ahmed sai aika Mata da sakonni yakeyi ta gefen ido, ta dukar da kanta dama suna facing juna itada shi.
Saida mommy tayi nak tace "next time idan zaki tuka tuwo ki tabbatar yayi sulbi sosai. To kawai tace domin idan dai ba tuwon masara takeso ya koma ba, tasan ko hasidin iza hasada yasan tuwon nan ya tuku. Maid din ce ta tayata suka kwashe komai zuwa kitchen, tayi daki domin yin sallah. Suma fita sukayi masallaci.

Mommy ce zaune a falon tana waya da Zarah "So nakeyi Auren khaleel ayishi cikin Sauri, don haka zanturo miki kudi kifara yomin odar Kaya na gani nafada, domin bikine zamuyi shi na kece raini.
Shigowa sukayi tayi Saurin Sallama, ta Ajiye wayar, zama sukayi tareda gaidata, tace tom dare yayi ku wuce ku kwanta Allah ya tashemu lafiya. Taci gaba da latsa wayar ta, "mommy in tafi dakina? "Ahmed yafada cikin sanyin murya mai hade da lallashi. "Saurin uban me kakeyi? Da da bakayi Auren ba uban me ya sameka? Kaga Ahmed ka fita idona in rufe, saboda aji dadin Asirce ka shiyasa kake kokarin shige Mata, to kabari sai nan da sati daya idan Agumun da aka kullo Mata ya sirace ehem. Saurin kallon ta khaleel yayi tareda cewa "Haba momy haka ake Aure fisabilillahi? Ai da kin hana kawai yayi Auren wannan irin kwalelen ya isa Haba. "Toh ubana ai kai nasani zaka iya dukana ma, to dak'ar ni kaji, ku tashi ku wuce kubani wuri kafin in canja shawara.
Khaleel ya fara mikewa fuuu ya wuce saboda takaici, Ahmed ya tsaya tareda zamewa kasa ya dafa kafarta "don Allah momy in laifi nayi miki ki yafemin don Allah, kibarni in sauke hakkin Y'ar mutane ko lekata inyi infito minti biyar ya isa don Allah. Yafada yana zubo da kwalla, tace "minti biyar idan ka wuce hakan zan shigo kuma wallahi bazakaji da kyau ba.
Tashi yayi da sauri yana share kwalla "na gode mommy, ya nufi dakin yana Ajiyar zuciya, a zaune take tana waya da Shukrah a wayar Inna, tanajin motsi ta kashe tareda mikewa tana jan hijabin data Cire ta Ajiye a gefen gadon nashi. Rufe jikinta tayi a cukurkude tareda daburcewa ta rasa Ina zata shige ma, "Hmmm yayi doguwar Ajiyar zuciya. Ya fara takowa cikin natsuwa tareda zuwa gaban ta. Hannayen ta ya riko. "Naziya"Am sorry please kinji komai zai wuce please don't be angry with me I love you, hannu yasa ya zame hijabin dake kafadar ta ya fadi kasa ya zuba Mata ido tundaga sama har kasa.
"I don't know you baby, yanzu nake sanin God gift da nasamu batareda sani na ba, you are beautiful baby, yafada idanun shi na kadawa kamar zaiyi kuka, cikin natsuwa ya bude hannayen ta yajata saman kirjin shi, jikinta na wani irin rawa domin wannan ne karon farko da namiji ya rungume ta, shikuwa jin kirjinta a nashi tuni yajishi a sama, Abunka da pure man da bai saba da cakuduwa da mata ba, Saura kiris su zube kasa, yana fesar da iska bakinshi domin samun

sauki ya dago fuskar ta tareda dora lips dinshi kan kyakkyawan bakinta yaji kiran momy, " Ahmed karka Bari inshigo ciki ranka zai baci nafada maka. Saurin janyewa tayi domin a tsorace take dashi tanajin yanda yake murza jikinshi a laps dinta she can feel his hardness, da bata kawo komeye ba ma. Muryar shi a shake yaja baya "please kibiyoni Anjima Kinga mommy tace infita anan please wife kifito ko kitchen ne muyi magana. Yafada yana fita cikin hanzari da Sauri, wasu irin kwalla ne suka taru a idanun shi.
Zamewa tayi kasa ta zauna tanajin wani irin yam yam a jikin ta, Allah yagani tana son Ahmed, Abinda ya boye mata Wannan ta fahimci dalilin shi domin ita ta nunamai batason namiji mai hali, Sannan yanzu ta Kara fahimtar shi Waye daga jiya zuwa yau, yana matukar son familyn shi yana bin umarnin mahaifiyar shi mai cikeda matsaloli Wanda ta daura damarar zata yi mata biyayya muddin ranta domin Ahmed, wani irin tausayi yabata yanzu, hawayen data hango akan kyakkywar fuskar shi kawai ya karya mata zuciya, me zatayi da zai sanyaya mai rai?
Daukar wayarta tayi ta Kira yayar ta bayan ta kulle kofar ta, Aunty Raliya, itace babbar yayar su ita ma tana Auren mai d'an hali saidai kamar yanda Al Adar su take suba masu yawon gidajen y'an uwa bane, "Aunty Raliya Ina wuni. "Amarya yadai kina kirana Karfe goma lafiya ko? "Lafiya kalau Aunty yasu Abba? Duk sunyi bacci, Ina fatan ba Matsala ko? "Um um, "Ina mijinki kike Kira na by this time? " baya nan yana dakin su. "What bangane ba, kodai kinki yarda dashi ne? "Aa. "Naziya, ki fadamin damuwar ki Kinga ke ba kawaye gareki ba da zaki fadamusu ni yayar kice bazan so ki cutu ba, bakomai Aunty. "OK listing to me kije ki dafamai ruwan tea mai kayan hadi ki shirya ki kaimai dakin nashi, kinsan wasu maza basa son shiga dakin mata saidai mata su bisu, "Aunty sai inje? "Karkije kinji, ki tsaya shirme wawuya kawai. Ta datse kiran kit, domin tanada zafi, tasan duk Abinda ke faruwa kuma sunada labarin uwar mijin Naziya domin Zarah kusa da ita take kuma haryau batasan Naziya kanwar tabace don haka ko dazu tashigo tana bata labarin Hajiya bilkisu da yanda take juya Ahmed, tana dariya da jin dadi,

Shiru Naziya tayi tarasa ta Ina zata fara, tashi tayi cikin Sauri, saida ta leka falon taga bakowa domin mommy nada nauyin bacci tana shiga dakin ta ta bingire, kitchen ta shiga ta dafamai ruwan tea harda na'a na'a, yana tashin kamshi, ta samu tea jug da cup ta zuba ta fita tana tunanin Ina zata ganshi harta bashi tea din takoma dakinta, jitayi anriko Hannun ta, tayi Saurin juyawa zata Sa ihu yace "Shhhhhh, nine, ware idanu tayi, jikin ta na rawa tace "ga tea Dama shi zankai..... Rikota kawai yayi ya nufi hanyar dakin khaleel da ita, yana kan computer yana duba harkokin company dinsu da Ahmed ke gabatar mai yanzu, ganin su yayi kawai ya sauke kanshi. Saida ya zaunar da ita ya koma gefen Khaleel yace "brother please excuse us. Dago kai yayi tareda kallon yayan nashi cikin idanun shi kuma yasan sarai me yake nufi yace "Ina zanje Yaya nida dakina? "Go to my room please, "zan tsaya a falo idan kungama magana indawo but I can't go to your room yanzu na Matar ka ne, "OK tanks ten minutes kafin mommy ta farka,.tashi yayi tareda daukar wayar shi ya fita yana "quick brother kaga Ina aiki na ka tsayar dani,
Kulle kofar yayi tareda nufar inda take tsaye cikin hijabin ta,..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
And now AUREN GADO,

Ga masu son su biya ga account details dina, *NAFISA HASSAN SANI 7304736012 @ FCMB* sai ku min magana ta wannan number 09069200154

ğŸ†“ page

1â*ƒ*£1â*ƒ*£&1â*ƒ*£2â*ƒ*£

.....rikota yayi zuwa jikin shi tana zamewa yace "wait Naziya please magana zamuyi kawai. zama yayi agefen gadon, ya dorata akan kafarshi, "Kiyi hakuri da duk Abinda yake faruwa that's our destiny, komai zaizo karshe, nasan kinada tarbiya kinada hakuri please keep it up, zamuci ribar Abun, idan kikaci gaba da tafiya a haka banida wata damuwa, yakamata ace yanzu mun zama daya, yakamata ace muna cikin bargo daya, yakamata mu zauna muyi hira in kula dake kamar kowane miji, but don't worry komai zai wuce, yafada yana zagaye west dinta da hannayen shi, tareda kwantar da kanta cikin kirjin shi, wani irin Abu takeji yana mata yawo a cikin jiki duk lokacin da ya tabata, kodon bata taba experiencing irin haka a Rayuwar ta bane. Jin yanda yake cusa kanshi a wuyan ta yasa take d'an zamewa domin tanajin yanda yake kokarin daga hijabin jikinta tareda nufar kirjinta yana so yaji how they are. Tayi Saurin riko

Hannun shi tareda Saurin juyawa tana girgiza mai kai cikeda marai raicewa. Kallon ta yayi cikeda roko yanaso tabarshi yayi yanda yakeso ko zai rage zafi domin yasan bazai yuwu ya nemeta a dakin khaleel ba, kuma yana falo zai iya jinsu domin yasan bakaramin aiki zaiyi ba, kuma yasan zata iya mai kuka tunda ko kirjinta bai fara tabawa ba . "Naziya " yakirata cikin wata irin murya, "inaso intaba inji, nonon ki nada kyau dazu kamar inyi tsalle in cafka nakeji Dana ganki ba hijab, kibani Dama ingansu inyi wasa dasu ko kadan ne. Wani irin tsalle tayi tareda zamewa ta rufe fuskar ta saboda kunya da maganar shi ta bata, kai namiji baida ta ido, saikace ba Ahmed innocent man ba yafada har yana dariya, "is OK tashi in rakaki wata rana da kanki zaki bani insha. Saurin mikewa tayi ya dafata "da munkwana tare da tuni sunzama toy dina, Amma lokaci ne. Kunya kamar ta nutse kasa, shikuwa ko ajikin shi,
Fitowa sukayi yana tsaye a falon rikeda ruwa mai sanyi yana kwankwada idanun shi cikin nata karab, idan ba gizo idanun ta suke mata ba tana ganin irin kallon rainin hankalin da yake mata, hartayi Saurin kwace Hannun ta ta wuce da Sauri, yana "baby ba Sallama, ita kuwa bazata iya tsayuwa kusa da d'an rainin hankalin nan bane Sam, mai halin yahudawa, ace mutum kullum cikin guntayen kaya kamar wani nakan dutse, mtsww.

Saurin wucewa dakin yayi yana karewa gadon nashi kallo yaga yanda zanin ya zame gaba daya, saboda zaman da sukayi a gefen shi, kuma bakaramin jujjuyawa Ahmed yarikayi ba saboda mugun feelings din da yakeji, shigowa yayi yace "Sorry Bari in gyara mana gadon, shiru yayi har yagama ya wuce bathroom, yana kallon yayan nashi bai ce tak ba, ganin yayo wanka yafito yaganshi a tsayen yace "yadai ko wankan kaima zakayi? "No ba munyi wanka ba kaima naga weather din is OK why you bath again? "Hhhh oh come on brother ko bakaga ma tata ta shigo ba kaima kasan dole inyi wanka ai. "in ten minutes? Ya fada batareda ya san maganar ta fito ba, "of cos is enough for me. Ya bashi Amsa tareda hayewa gadon ya kwanta cikeda farin ciki, kafin ya tuno da tea ya diro ya tsiyaya ya farasha yana lumshe idanun shi.
Komawa yayi kan kujera ya zauna yana danna waya har Ahmed yagama ya haye gadon yana cewa "ga coffee idan zakasha narage maka. "Uhm. Kawai ya Amsa, ganin Sam bazai iya bacci ba ya mike ya shiga bathroom wanka yayi tareda Alwala yadawo dakin yatada sallah.

Gefen Naziya kuwa, tayi bacci cikin kwanciyar hankali tareda farin ciki, tasan Allah yabata miji mai halin kwarai kuma da yardar Allah zata tayashi yiwa mahaifiyar shi biyayya.
Sabo da tashi da wuri Karfe hudu ta tashi, saida ta yi sallar nafila kafin biyar tayi farillah, ta zauna Azkar zuwa Karfe shida ta fito cikin karamin hijabi zuwa kitchen, ta shirya musu breakfast mai lafiya. Kafin bakwai da rabi ta kammala ta gyara ko Ina takoma tayi wanka, shiryawa tayi cikin Riga da zani, tafito tsab, tana kamshi.
Kiran mommy yasa ta fito da gudu tana amsawa ta ganta hakimce, dukawa tayi ta gaida ita, "ke bakisan kiyi pleasing uwar miji ba ta hanyar shiga dakina ki gyaramin da kuma dakin khaleel, toh daga yau gyaran dakunan mu na Hannun ki idan kin tashi. "Toh mommy. "Oya a shirya mana breakfast anan yau ma.
Fitowa Ahmed yayi idanun shi kur akanta yana aika Mata da sako tareda murmurshi mai cikeda sirrika. Itama tayimai tareda dukar da kanta tafara aikin ta,

"Ina Ibrahim din? Bacci yakeyi jiya baiyi bacci da wuri ba yace sai ya tashi. "Aa nifa banason wasa da ciki, ke Naziya yi Sauri ki kaiwa dana Abinci a daki karya kwanta da yunwa. "Mommy da kin Bari ya tashi. "Wuce maza ki kaimai. tafada, tana cewa "jeki zanyi serving din mu maza ki tabbatar yaci kafin ya kwanta. Jim tayi kamar bazataje ba tace "me kike jira? Cikin tsawa, da Sauri ta dakko tray ta shirya mai komai nashi ta wuce jiki a sanyaye "Allah yagani itadai jinin ta bai hadu dana gayen nan ba, baiyi mata ba Sam, da Sallama ta shiga dakin, yana kwance a tree seater a kudun dune, fuskar shi ce kawai a bude. Idanun shi biyu yana kallon sama, Sallamar ta yasa ya d'an juyo cikeda yanga, ta tsaya daga nesa muryar ta na rawa ga shi inji Mommy, ta dora akan karamin table zata juya, "Serve me. Yafada cikin isa, tayi Saurin juyowa "wannan mugun d'an rainin wayau ne, batason musu don haka cikin Sauri ta juyo batareda ta kalle shiba ta hada mai komai tafita cikin Sauri.
"Hmmm kawai yace yafara cin Abincin shi. Yana lumshe idanun shi.
Komawa tayi falon tace tabashi. Kafin ta zauna tafara nata Karin.

Toh haka dai kwanaki keta tafiya yau Naziya ta kai wata daya cur Agidan komai na gidan tundaga gyaran dakunan su zuwa kitchen ya koma Hannun ta, complain din momy ya riga ya shiga jikinta, Ahmed kuwa yanzu ganin shima gagarar ta yakeyi domin dokar mommy tayi nisa yanzu, tun yana rokonta harya hakura ya zura ido, sai rama yakeyi a tsaye saboda damuwa baya ko son haduwa da Naziya saidai suyi chart da wayar da ya siya mata katuwa wadda ta boyeta a dakin ta bata Bari mommy tagani ba, by now ta fuskanci muguwar kiyayyar da mommy ke mata. Idan ya fita aiki kuwa yana kiranta kullum bata hakuri yakeyi,. Tana kwantar mai da hankali domin ta saki jiki dashi sosai, yanzu har marmarin ganin shi takeyi akusa da ita she is missing his touch, rabon da ya rungume ta tun a dakin Khaleel, kullum Aunty Raliya shawarwari take bata wainda Sam basuda Amfani a wurin ta tunda an hanata sakewa da mijin ta. Iyakar ta dashi sai ban hakuri tareda Sanya mata Albarka a kullum "Naziya ke Y'ar Aljannah ce, watara na zakiyi farin ciki, ki Kara hakuri komai mai wucewa ne.

Bikin khaleel Ansa rana wata daya mommy sai shiri akeyi An shirya event Kala Kala, khaleel ko a jikin shi domin Amaryar ma ko wayar ta baya dauka, Wanda ta watsa shi a kwandon shara tunda dai uwar miji na sonta ai zata wataya kuma dole ya sota.
Zaune suke a office din yayan nashi ya kalle shi "brother sai ramewa kakeyi are you Alright?
"Am not khaleel, yama zan zama cikin kwanciyar hankali bayan kana ganin me yake faruwa?
"Am sorry Yaya bansan yanda zantaimake kaba. "Is OK yanzu kaga maganar shigo da kaya zai zo dai dai da lokacin Auran ka naso kaje da kanka, ko zaka Bari kaje honey moon gaba daya?
Yafada yana d'an murmurshin karfin hali. "Noo wane irin honey moon? Zantafi kawai idan nadawo ai ba guduwa zatayi ba. OK kafadawa mommy ba ruwana.

Karfe biyu suka shigo gidan, an baje akwatunan sunkai saiti bakwai an narka dukiya kamar za asiyo mutum, suna shigowa tace "Yauwa khaleel zoku gani komai yaji? Tafada cikeda farin ciki, ya zauna yana kallon kayan tareda mamaki " mommy kayan Waye duka? "Ga rainin wayau, na Matar ka ne mana. "Duka? Yes gaskiya aa a raba biyu abawa Naziya rabi. "Why zan bata rabi?

Saboda am sure ba ayi mata irin haka ba. Yafada cikin zafin rai, "bazan bayar ba domin batasan darajar suba, fitar kunya nakeson inyi dasu gidan minister guda dole akai Abinda baza a raina muba, Kuma ka nemo motar da za a hada mai tsada ta mata. Ahmed ne ya katse maganar "Zamuyi placing oder momy na kayan mu sai kasa a turo motar da kakeso kafin katafi.
Saurin kallon shi tayi tareda cewa "Ina zaije? "China zai shigo mana da wasu kaya. "Yaushe? Nan da sati uku. "Saboda mugunta? yaro zaiyi Aure ya Amarce shine zaka turashi wajen kwaso kaya? "Mommy, ni nace zanje ba Yaya ya sani ba, I want to go. "You are not going don haka ya shirya shi yaje, tunda nashi Auren baida Amfani, idan kanaso kaji dadi Ahmed sai ka Auro zabin zuciya ta Amma Indai Inada rai bazan hada iri da yar masu zama akan buzuba a mallake min da'.
Kallon momyn yakeyi wani iri, sometimes sai yaji kamar ba ita ta haifeshi ba, domin duk uwa tana son farin cikin d'an ta. Tashi yayi kawai yayi dakin shi dai dai tana fitowa ya ganta Amma saboda ciwon da kirjin shi ke mai yakasa ko tsayawa yayi mata magana. Kallon shi tayi sosai, taga ramar shi a yau tareda yanda yayi sanyi sosai, duk da ba mai hayaniya bane,
Jikin ta yayi sanyi, Allah yagani yanzu ba Abinda takeso irin su zauna suyi hira ido da ido ita dashi domin kullum soyayyar shi karuwa takeyi a zuciyar ta.
Kallon momyn khaleel yayi "mommy me kike nufi da d'an uwana? "Kamar ya? "Momy ki barshi ya samu natsuwa mommy don't you see how sad he is? Bakya ganin yanda yake ramewa? Mommy Yayana na cikin damuwa sosai, I beg of you kibarshi ya huta haka. Wani irin kallon zanci ubanka tayi mai kafin ta mike cikin fada tayi dakin Khaleel din, "zanje inji dalilin da zai rika hadani da kai kana titsiyeni kamar ubana.
Binta yayi yana yi mata magana tayi banza tayi dashi. Zaune yake yana dafe kirjin shi, ta shigo "toh kanin uwata Wato da kun hadu saika rika zugo d'an uwan ka yana titsiyeni kamar ubana ko, toh ka fita I dona kuma ka saurare ni, nayiwa Kawata magana Hajiya sa'ade maganar Y'ar ta Salifa idan ka shirya zama da Matar son taka toh ka yarda ka Auri zabin rai na lokacin zanbaka damar da zaka zauna da Matar son taka.
Kallon mahaifiyar tashi yakeyi tareda yin tagumi saida ta ci gaba da fada yace "am sorry momy bazan iya musu dakeba kiyi duk Abinda ya dace insha Allahu zanyi miki biyayya. "What Yaya? Me kake fada? This is too much gaskiya Haba momy p..... "Quit Khaleel Yafada cikin dakamai tsawa, tareda nuna shi da yatsa "not a word again, why are you challenging our mother? Kar in kuma jin kalma daya daga bakin ka. Fita tayi kawai tana amsa wayar fauzy tana dariya "Y'ar Albarka wane irin product kike Amfani dashi na kayan kwalliya?
Wani irin bakin ciki khaleel yaji tareda kallon Ahmed din ya wuce domin shima ya batamai rai. kwanciyar shi yayi kawai yana kallon sama. Dawowa yayi ya tsaya akan shi "Yaya what ever is happening is not right. why zaka zuba ido kana over looking komai, how could you accept the second marriage? Ka manta me kafadamin, kaman ta kafadamin bazaka taba hada Naziya da wata mace ba? She didn't deserve All this life Yaya, she deserve to be happy. "Hmmm ya kakeso inyi Khaleel? Inyi disobeying mommy oh what? "She is my mother Ina so mu rabu lafiya, and Naziya yes I love her more than my life, yazanyi dole inbi mommy in inaso inga dakyau, ba wata mace da zata samu matsuguni a zuciya ta, ita kadai nakeso ita kadaice zabina, if Auren da mommy zatayi min shine zaisa tabarni da matata in zauna lafiya then be it, am ready to obey what ever she said that's final. Yafada yana mikewa cikin fushi yayi bathroom.

"She didn't deserve it. Yafada yana naushin iska, he feels as kamar shi yafi kowa jin ciwon Abinda akeyi mata, ita kanta nuna wa take ba Abinda ke damun ta, tun ranar da tazo gidan nan yaganta tana kuka bai kuma ganin ta cikin bacin rai ba, sai kace bata da zuciya?
Fita yayi fuu dai dai tana shiga kitchen, cikin zafin zuciya ya bi bayan ta, kafin ta ankara jin hucin mutum kawai tayi yana fesa mata numfashi cikin zafi a bayan wuyan ta, kurawa kwantacciyar Sumar dake wurin idon ta yayi, idanun shi sun kada, he don't really know why zuciyar shi ke tafasa, he is trying to control his Anger da baisan dalilin taba.
"Auzubillahi. Tafada tana ja baya da Sauri domin tsayuwar da yayi a bayan ta ya kaucewa tsarin Addini, kuma shi ba muharramin ta bane, wani irin kallon bakada tarbiya take watsa mai tareda nisan ta kanta daga kusa dashi, he can clearly read her reactions, don haka tuni zuciyar shi ta Kara hawa, "what? Why are you looking at me like that? Yafada yana describing da hannun shi, A haka zaki karasa zaman Rayuwar Auren naki you don't care about your husband, kawai kiyi bacci ki tashi ki dafa Abinci, shine damuwar ki, you are pretending as if you don't care about All this wealth, you are such a jocks, kin zauna kin baje ba Abinda ya dameki sai kici kiyi bacci you forget All your responsibilities, look if anything happen to my brother because of you, I won't forgive you.
Tunda ya fara magana kallon shi takeyi, kuma irin kallon you won't get away with this, yanayin shiru ta gyara tsayuwar ta tareda daga gira daya, and she look very cute, "oh really? So nice bansan responsibility dina ba? Saboda nayi shiru Ina kallon komai, waya fada maka Ina farin ciki da duk Abinda yake faruwa da zaman Aure na? Nice nakeda complain ba yayan kaba because I know my right, and da kake cewa duk Abinda ya samu yayan ka bazaka yafemin ba, ni kuma in wani Abu ya same ni fa? Kana tunanin iyaye na zasu yafe muku? "And don't forget he is my husband, kuma munyi Aure saboda Ina son shi ba kiyayya ba, this house Hmm who told you am happy in this house? hakuri nakeyi bisa ga irin tarbiyar da aka dorani akai, iyaye nagari suka daga rayuwata, yawo da shigar da bata dace ba duk iyayen mu sun hane mu, shiga hurumin da bana muba duk iyayen mu sun hane mu, Saboda sudin iyaye ne nagari..... "Nice ba uwar kwarai ba kenan? Mommy tafada cikin tsananin bala'i
Jikin Naziya na rawa tayi Saurin kame bakin ta, tareda dana sanin biyewa zuciyar ta ta tsaya kula khaleel bayan hakan ma bai dace ba, yanzu tun ba aje ko inaba she is regretting..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
And now AUREN GADO,

Ga masu son su biya ga account details dina, *NAFISA HASSAN SANI 7304736012 @ FCMB* sai Ku min magana ta wannan number 09069200154

ğŸ†“ page

1â*ƒ*£3â*ƒ*£&1â*ƒ*£4â*ƒ*£

..... "Mommy, magana mukeyi please don't interfere please. "Karya ne wallahi duk naji Abinda ke faruwa tundaga farko, Wato munafuka sai ki rika nuna halin kirki Wato mugun halin ki na can cikin zuciyar ki ko, "toh kin fada son ranki yanzu ki saurare ni mai miji, yau nawa ga wata? Aure zanyi wa mijin naki rana daya da Khaleel, zan Auro mai Matar kwarai Matar nunawa sa'a ba Y'ar gidan masu kwana kan buzu ba, munafuka kinayi kamar tagari Ashe bakin hali na nan a gefen zani, kin tsaya kina musayar miyau da kanin mijin ki sai kace sa'an ki. Dafe kanshi kawai yayi, you mess up things kawai, Naziya durkushewa tayi for the second time ta saki kuka mai ciwo "kishiya Aure? Bayan ita ko dama ba abata ba ta mori Auren shine ake wani zancen za ayi mata kishiya?.
Tashi tayi da gudu tawuce zuwa daki tabar aikin domin wani irin zafi zuciyar ta keyi mata. Kukan ta ya taba mishi zuciya fiyeda tunanin mutum wani irin sarawa kanshi keyi kamar zai tsage biyu.
"Kai kuma ka tsaya yarinya karama na zuba maka rashin kunya kana kallon ta, bazaka watsa mata Mari ba, kauce ni in wuce ka batamin rai. Tafada tana fita, sintiri yakeyi a kitchen din yarasa Ina zai sa kanshi, kallon da ta watsa mai ne yafi komai daga mai hankali, she really hate him. Fita yayi da sauri ya Kira maid yace ta karasa aikin girkin yayi dakin shi,
"Ahmed yasamu akan dadduma yana lazimi, yace "Yaya please go to your wife she is crying please. Saurin mikewa yayi me yake faruwa? Wa ya sata kuka? "Is you Yaya kaine sanadi,

mommy Tafada mata zakayi Aure please go to her. Yafada zuciyar shi na wani irin rawa, komawa Ahmed yayi gefen gadon ya zauna dabas, "I can't go khaleel. "Why? Yaya Matar kace, she needs your comfort please. "Mommy tayi min iyaka da ita. "Iyaka? What iyaka? "Yaya hakkin yarinyar nan bazai barka ba karka manta ba mommy ce kawai keda hakki akanka ba, why ka Auro ta idan bazaka iya ba?

Kukan da yaga Ahmed din nayi yasa yayi Saurin zama gefen shi ya rungume shi yana Ajiyar zuciya, "am sorry Yaya please nasan komai, amma kaine kabada kofar komai dake faruwa. Bai iya cewa komai ba sai shesheka yakeyi "am sorry khaleel banda karfin zuciya irin taka am weak.
Saida ya fitar da kwallar tausayin d'an uwan nashi.

Naziya kuwa tana shiga ta kulle kofar ta fada bathroom ta shako kukan ta son ranta, Karar wayar ta tasa ta fita ta dauka ganin number Ahmed dince yasa ta datse kiran kit tareda kiran Aunty Raliya.
Tana dauka tasaki kuka mai ciwo. "Aunty wallahi nagaji ni zankoma gida nagaji bazan iya ba, zan mutu a rasa dalilin mutuwa ta Aunty please kizo ki tafi dani.
Saida tayi ma ishinta ta yi shiru tana jinta, "Naziya', ta kirata, bata iya amsawa ba sai sheshsheka tace " kin taba ganin ko kwana muntaba yi agida tunda mukayi Aure, bare kuma yaji? Dagani har Aisha ba wadda ta taba kai Karar mijin ta cikin gida ko gaban malam, muna hakuri tareda bawa junan mu shawara in Matsala ta taso, infada miki gaskiya? Ba macen da batada kalar tata Matsalar Aure, please Naziya ki dauki halin Inna, kina gani kullum malam yabon ta yakeyi domin yasan mace ce tagari, nasan duk Abinda yake faruwa a gidan Auren ki, ba kanki farau ba, ki jajirce kici gaba da hakuri, yanzu fa aka fara Naziya, ni nafada miki tun farko kibi mijin ki tunda shi an hanashi binki, biyayyar Aure kikeyi bauta kikeyi, ki rungumi taki kaddarar Allah zai kawo miki mafita.
"Aunty banki ta taki ba, Amma inayin iya bakin kokari na, kinaji fa wai Aure zai karayi. "Toh sai me? Baki yarda da kanki bane? Ke ba mace bace? Look ki nuna musu Auren ba komai bane idan bakida hakki zakiga saka mako, nasan kinada hakuri ki Kara akai kar taurin kanki ya motsa Wanda bakya juyuwa.
"Hmmm nagode Aunty, insha Allahu zanyi hakuri. "That's my sister, kuma insha Allahu zamuzo karshen satin nan nida Aisha. Dadi taji sosai domin Y'ar uwarta ta bata shawara mai kyau, tareda sanyaya mata zuciya.

Sharewa tayi da komai cikin ikon Allah, ta Kara rungumar hakuri tareda daura damarar share komai, tana ganin yanda aketa shirin biki kamar da gayya itama Amarya anyo mata kayan fitar kunya, Aljihu tasa Ahmed ya bude yana bata kudi ta zabgi kaya, ciwo yakeyi a tsaye batareda ya fadawa kowa ba shikadai yasan damuwar shi, Naziya tuni ya nesanta kanshi da ita domin ya rage mata damuwa, itama ta Ajiyeshi a kwandon shara, badon bata damuwa ba, biki nata matsowa shikuma yana shirin tafiyar shi.
Khaleel yayi yayi yabarshi ya tafi yace no shi zaije Ana gama biki Washe gari zai wuce. Mommy ma basu fada mata shirin su ba.
Khaleel ma tuni ya kiyayi Naziya domin ya lura tsanar tashi ta Kara yawa fiyeda da, yana ganin

yanda take hada girar sama data kasa in sun hadu, shi yasan halinta Wanda Ahmed bai san shiba ma yanzu, daga gani macece kaifi daya inbata yinka shikenan, ga taurin kai.
Tana lura da Al amarin shi yanzu sama sama in sun hadu ta lura yanzu baya fitowa da kana nan kaya ko falo, tun ranar da tayi mai gori.

Biki fa yazo Amare nata rawar kafa, angwaye kuwa ko motsi basayi, ko Khaleel Yafada mata karta sake ta sakashi cikin shirmen party d'in su. Momy ta tattara su duka ta watsar tana hidimar ta, itadai tasan burin ta zai cika ya'yan ta zasu Auri irin zabin ranta, don haka ta zage ta bude bakin Jakarta.
Lafiyayyan mothers day suka shirya a tafkeken hall da yaji kudi, ta gayyaci manyan mata masu kudi da Aji, da kanta tayowa Naziya dunkuna Kala goma wai na dannar kirji tasa na fitar biki.

Lokacin da malam yaji labari, waya yasa aka hadashi da ita ya mata nasiha tareda Sanya mata Albarka, Wanda ta Kara mata kwarin guiwa, bawai Abun baya taba ta bane a'a "ya za'ayi bazai zafeta ba, kawai dai ta rungumi hakuri da kuma waraka, Wato Alqur'ani mai girma. Wanda shine maganin duk wata damuwa da yayewar bakin ciki.
Ana Saura kwana uku biki tasa Shukrah tazo domin ta yi mata lalle, Wanda saida tayi da gaske Malam yabari, tazo suka baje a dakin suna hira tana yimata lalle, "Aunty Kinga magana ta ko, nafada miki Yaya Ahmed mai kudi ne, gaskiya kin more irin wannan katon gidan. "Hmmm. Kawai tace, "Amma Aunty kin d'an rame kadan sai haske kawai da kika Kara, Ina Yaya Ahmed din? "Yana nan, kuma ki rage surutu kiyi sauri kafin lokacin da Malam yabamu yayi, Amma Aunty da gaske Aure zai Kara wai? "Eh. "Auren ku wata daya da y'an satika shine zai Kara? "Ya isa maganar shukrah, tafada domin batason zancen,
Maid ta kawo musu kayan ciye ciye a dakin, domin mommy tafita, har suka gama ta rakota tareda bata kyautar kayan shafa, domin batada kudi a hannun ta, suna fitowa su Ahmed sukayi Sallama, tayi Saurin dauke kanta. Shukrah baki har kunne domin tayi mugun sabo dashi tace "lah Yaya Ashe zangan ka kafin intafi? "A a shukrah kece a gidan namu? "Eh Yaya Ahmed har nagama wa Amaryar taka lalle zantafi, Saurin kallon hannun nata sukayi dukan su, khaleel yayi Saurin dauke kanshi, "kai Amma mungode shukrah da wannan zuwan Yafada yana matsawa kusa da Naziya ya riko hannun ta, shukrah tayi Saurin rufe idanun ta saboda kunya ta ruga hanyar waje tana ni na gudu gida Aunty bye, Dariya Ahmed yayi yace "please Brother ka kaita gida. Amsawa yayi kawai ya fita, motar shi ya fada dalleliya yabi bayan ta, tareda yimata horn, ta tsaya don har tafita wajen gate d'in, "muje ko' Yafada ba wani walwala, "nagode zansamu adai daita ma. "Come on ki shigo Yaya Ahmed yace inkai ki.
Budewa tayi kawai saboda batason musu, gashi ya cika mata ido, maganar gaskiya zaiyi wulakanci domin fuskar tashi Sam ba fara'a ko walwala, don haka batayi yunkurin cemai komai ba har ya Kama hanya yana driving slowly, sai kamshin shi da kwarjini da ya cika motar, "me yasa bakya zuwa kina ganin Y'ar uwar ki? Yafada batareda yako kalli gefen taba, itama Abun yazo mata a bazata duk ta diririce, saida ya mai maita, tace "ba a barin mu fita zuwa yawo. Tabe bakin shi yayi kawai bai kuma cewa komai ba har ya kaita kofar gidan tace ta gode, ya ciro kudi a gaban motar shi ya mika mata masu yawa, Saurin kallon hannun shi tayi ta koma gefe tana girgiza kai, domin kudin zai kai dubu Ashirin, "nagode bama karbar kudi a waje. Mayar wa yayi kawai yaja motar shi tareda bade ta da kura yayi gaba, "tab Aunty Naziya

wannan ai yafi Yaya Ahmed girma da cika ido ga girman kai kamar d'an gidan Sarki,. Tafada tana bin bayan motar shi da kallo har ya bace.

Su khaleel na fita ta fisgi hannun ta tayi dakin ta da gudu, yanzu ne wani irin bakin ciki yake rufe mata zuciya, bin bayan ta yayi batareda ya shirya ba, zubewa tayi agadon ta kife tareda sakin kuka mai taba zuciya, dafata yayi tayi Saurin zabura fuskar ta shabe shabe da hawaye "don't touch me. Tafada kai tsaye tana mai kallon kai ne sanadi, "Ina dana sani, nayi hakuri tunda ga ranar farko da Nazo gidanku, bawai nace mommy bata isa tayi min fada bane, a'a kaine Matsala ta, kai kakawo ni gidan nan, Amma sai dai in hadu dakai a hanya, duk na daure nayi hakuri, yanzu kishiya..... Takarasa tana kife kanta a cinyar ta, shiru yayi tareda dafe kanshi yazame gefen gadon ya Rungumo ta baki daya zuwa jikin shi tana kokarin Sauka. "Nasani Naziya, ki yafemin don Allah, nasan sai Allah ya tanbayeni hakkin ki, domin banyi miki Adalci ba, yazanyi Naziya Ina gudun bakin uwa, yanzu ma na kaucewa tsarin ta da dokar ta, don Allah kiyi shiru ki yafemin kar Kisa ni a cikin damuwa, kinsan cewa ganin kwanciyar hankalin ki ke kwantar min da nawa, Amma yanzu idan kina wannan kukan zuciya ta zata iya bugawa kowa yarasa ni. Saurin yin shiru tayi tareda share hawaye da bayan hannun ta "meye laifi na? Saboda Ina Y'ar talaka? Meye illar talauci tunda bamu nema a wurin wani ba, Alhamdulillah da gidan da na fito bama raina Abin da Allah ya bamu. "I know" Naziya please forgive me, kuma Kisa a ranki wata rana komai zai wuce, zakiyi farin ciki insha Allahu, ni nasan banda wata kalma da zanyi Amfani da ita domin baki hakuri Amma nasani na zalunce ki, ki yafemin. Naziya na gaza akanki ban sauke nauyin ki dake wuyana ba. Yafada yana dora fuskar shi akan wuyan ta, wasu irin hawayen shi taji suna bin wuyan nata, da sauri ta dora hannun ta saman kanshi tareda cewa "don Allah kayi shiru nima kaga na hakura nayi shiru, kaga bakyau babba na kuka. Tashi yayi tareda ita ya zauna gefen gadon, tareda fuskantar ta yana share idanun nashi yana mai murmushi kadan, "wayace miki ni babba ne a wurin ki? "Kai babba ne ai ka girme ni sosai. "No ni jaririne a wurinki domin wata rana shayar dani zakiyi,,, wani irin saurin rufe fuskar ta tayi saboda kunya, "Hhhhhh ko za a bani ne yanzu, Yafada yana riko west dinta cikin tsokana, ta zame cike da kunya, dadin moment din sukeji sosai, ta kalle shi cikeda tausayin shi tace, "bakada lafiya ne? Murmurshi yayi, "yes. "Meke damun ka? "Soyayyar matata, you know banason in rasaki Naziya idan nayi tunanin zaki iya gajiya ki gujeni hankalina natashi, bazan iya ganin ki kina Rayuwa ba agidana ba, banason inganki tareda wani Naziya saboda Ina sonki Ina kishin ki, ganin ki a inuwar Aurena yana sani inji farin ciki, yana rage min damuwa, please stay with me, my wife komai zaizo karshe wata rana zamu kasance a cikin inuwa daya zanganki da jini na atare dake a wannan shafaffen marar. Yafada yana shafo cikin ta, d'an zamewa tayi kadan domin yanasa ta jin wani iri a jikin ta. A wannan lokacin ya bata farin ciki mai yawa Wanda zata sakashi a tarihin Rayuwar ta domin yamata Alkawura da yawa akan yanda zaman su zai kasance, anan yake fada mata bayan bikin Khaleel da kwana biyu zaiyi tafiya, Kinga da momy zata Amince tare zamu tafi dake, muje musha soyayyar mu a can har in zagaya dake kasashe da dama.
Maganar mommy ce tasa ya mike tareda cewa mommy is here bari inje. Ya fita da sauri, tana tsaye tareda Khaleel Wanda shigowar shi kenan, tare suka zuba mai ido suna kallon shi, Wani

irin mugun kallo ta watsa mai, "uban me kakeyi a ciki? Shiru yayi ya kasa Amsata, "Ahmed idan ka ketare iyakar da nayi maka banyafe maka nono na da kasha ba. Tafada tana nuna shi da yatsa, saurin daga kanshi yayi tareda girgiza kai kawai ya wuce domin bazai iya magana ba, Khaleel ne yakalleta "why mommy? d'an ubanka, wallahi kaima kaji ko a mafarki naji ka fada soyayyar Y'ar talaka bazamu kare lafiya dakai ba. "Saboda me? Talaka ba mutum bane mommy? "Me ake da sunan talauci ma? Ni wuce bani wuri kuma kaji Abinda nace maka ko ku nemi Amaren ku sallame su banason harkar tsiya tunda dai Allah ya Azurta mu, idan bazaka iya cirewa a jikin ka ba kazo inbaka kabasu. "Wallahi mommy ba shegiyar da zanbawa kudina saboda tayi taron banza ai sunada kudi kowacce Aljihun ta yayi kuka, yafada yanayi gaba batareda ya tsaya saurarar taba, "kaga d'an banza, ai da Ahmed ne yanzu zaiyi Abinda nace Amma wannan mai taurin kan tsiyan sai mun sha fama.

Biki fa yazo, Amare nata shan even, momy yau ne take nata taron gidan makil da mutane ta gama cika gida da manyan mata y'an karya unguwar kawai daka shigo zakasan biki akeyi na kece raini, Naziya tun da gari ya Waye take jinta wani iri, mugun sanyi da zazzabi ke rufeta ma saboda damuwa, yau dai ba aiki domin komai odar momy tayo har Abinci,
Don haka tana kwance tana lazumi da carbinta na yatsa, Shigowa tayi cikin fada, "ke banason bakin ciki da kishi ki tashi ki shirya ki fito, kinzo kin kunshe a cikin daki kamar tsohuwar munafuka, Aure dai gobe insha Allahu sai an daura shi ko zaki mutu, in banda Abunki keda ko dadin Auren baki sani ba meye na kishi, don haka fito maza yanzu mutane natanbaya Ina uwar gidan Ahmed.

Tashi tayi cikin Sauri, tace "toh mommy, ta wuce bathroom ta sheko wanka, cikin kayan da momy ta bata ta ciro wani lafiyayyen leshi riga da sket kamar dinkin Amare ta saka, tana taje sumar ta taji Sallamar y'an uwan ta, Aunty Raliya da Aisha harma da Shukrah, wani irin tsallen dadi tayi domin Wannan ne karon su na farko a gidan nata, ta karbi d'an karamin goyon Aisha tace "Aunty my kalefa ya Kara wayau. Kallon ta sukeyi kawai domin sunga Alamar rama atareda ita ga kuma damuwa, basuce komai ba saida suka natsu shukrah ta tayata kwalliya ta murza dauri, sukace muje ki rakamu mugaida uwar mijin ki. "Toh tace suka fita, tana can kuryar dakinta da kawaye sai shewa sukeyi ita tafara Sallama wasu suka Amsa wasu suka zuba mata ido, suga Ina wannan kyakkywar ta fito, "mommy ga yayyina sunzo su gaisheki. "Toh sannun ku da zuwa, tafada tana gyatsina, kije dasu can dakin ki kisa Abasu komai domin akwai wadatar shi anan kuje. Tafada batareda tajira ko gaisawa suyi ba. Aisha dayake tanada fushi, har ta juya, Raliya ce ta tsaya tace "Allah yasa ayi a sa'a yakuma kade fitina, wasu sukace Amin. Ta juya Naziya tabi bayan ta,

Suna shiga dakin Aisha tafara sababi "wallahi Aunty Raliya wannan Matar batada mutunci yanzu dama Abunda ake fada gaskiya ne, gaskiya ni da malam zaiji magana ya raba Auren nan kawai. "Kinsan me zakiyi? Dakin bar nan saikije ki same shi kuyi magana kinji Aisha. Raliya tafada cikin haushi, wane irin Abu ne zaki tadawa yarinya hankali da mugayen kalaman ki, to sai me akanta farau da irin wannan uwar mijin? Don Allah kirika tausasa zuciyar ki. "Kiyi hakuri Aunty Abun ne yabata mun zuciya kalli yanda yarinya ta koma saboda fitinar wannan Matar,

yanzu yarinya ko wata biyu kwarara batayi ba za azabgo mata kishiya wallahi ba adalci. "Ya isa bashi yakawo muba munzo ne mu debe mata kewa don haka don Allah ki daina mitar haka. Shigo musu da Abubuwan ciye ciye tayi ta baje musu tareda daukar kaleefa tana mai wasa, Domin su dauke mata damuwa suka saki jikin su sosai tareda yimata hira tareda shawar wari, ta saki jiki a ranar, lokacin da aka fara taron ma tare suka shirya suka fito wanda tun shigowar ta gidan wannan ne karon farko data tako kofar gidan a yanzu ne take sanin Aljannar duniyar da take ciki, Suna fitowa khaleel na shigowa rikeda key cikin manyan kayan da ta lura yanzu yana kokarin sakawa, kallon ta yayi ya dauke kai tareda matsowa ya gaida su Aunty cikin girma yace kuzo muje inkai ku. Taso tace bazata shiga motar tashi ba Amma ba hali domin sun Ansa har suna godiya, Aunty Raliya tace munko gode domin bamu san wurin ba, shukrah ce agaba ita dasu Aunty a baya fuskar ta turbune domin Allah dai yagani tamafi kaunar mommy akan khaleel, a harabar wurin ya Ajiyesu dai dai ana kawo Amaryar tashi fauzy wadda tasha ado kamar zataje gasa cikin tsaddun bridal dress, Washe baki tayi tayi saurin nufoshi "baby "kazo. "No banzo ba mutane nakawo am going back, yafada yana shigewa cikin motar ya datse, su Aunty sukayi mai godiya yace bakomai batareda ya ko kalli gefen Naziya ba, gaba daya kawayen ta sukayo mata cah, "angon kenan Fauxy gaskiya gayen nan yaje, Amma akwai wulakanci. "Ba ruwanku I love him like that. Tafada tana juyi tareda cewa suje, suka take mata baya tana yiwa su Naziya kallon banza,
An barar da kudi a wannan taron na gagaruman mata da hamshakai, to suma dai ba laifi domin sunyi kwalliyar su cikin mutunci ba wadda tasaka gyale dukan su hijabine, Wanda ya janyo suke musu kallon rashin wayewa da tsantsar kauyanci, su momy an barar da rawa da kudi itada sauran iyayen Amaren, su Naziya na gefe itada y'an uwan ta har akaci aka sude, fitar tata tasata cikin farin ciki at least tafito a cikin wannan gidan dayake kamar kurkuku a wurin ta. aka yi komai suka yi gidajen su, tayi farin cikin kasancewa tare dasu domin sun Cire mata kadaici da damuwa, Wanda sukayi mata Alkawarin dawowa Washe gari yinin bikin, throughout ranar har dare batasa Ahmed a idoba, an zubawa Amaren kayan su a sababbin ginin nasu dake gidan, kowacce an narka mata dukiya fiyeda tunani, dama haka Hajiya bilkisu takeso.
Kayan Naziya da ko a ido bata taba ganin suba tuni antattare an zuba su a store an zuba na Amarya..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA

MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
And now AUREN GADO,

Ga masu son su biya ga account details dina, *NAFISA HASSAN SANI 7304736012 @ FCMB* sai Ku min magana ta wannan number 09069200154

ğŸ†“ page

1â*ƒ*£5â*ƒ*£&1â*ƒ*£6â*ƒ*£

..... Ta kwana da matukar tunani a wannan daren, Rayuwar ta da Ahmed, distance relationship, hatred tsakanin ta da y'an uwan shi, musamman Khaleel, she don't really know why, bata kaunar ganin shi, idan akwai Wanda zata nunawa tsana itace mommy wadda ta hanata sakewa a Rayuwar Auren ta, but why him? So take ta nemo Amsar takasa, juyi takeyi cikeda mutuwar jiki, idan tace bata cikin damuwa tayi karya, Ace Auren ta wata cikin na biyu ba kwanciyar hankali, batasan dadin miji ba batasan dadin zaman Aure ba infact ba Abinda ta karu dashi sai girki da gyaran gidan, Wanda anayi ne domin a kuntata mata, basusan ta horu da aiyuka agidan ubanta ba, ba aikin da zai gagare ta, tsoranta daya a rayuwa kar a rabata da mijin ta, domin duk Abinda ke faruwa soyayyar shi bata ragu a zuciyar ta ba, sai ma karuwa da tayi duk wani moment ita da Ahmed idan ta kadaici cikin farin ciki take kasan cewa, idan tana tuno su, tasani duk ranarda ta samu freedom da mijin ta zaman su zai yi d'ad'in gaske. Bata cire tunanin wata rana zatayi farin ciki ba, Wanda tana fatan tayi nasara insha Allahu. Tashi tayi tareda yin sallah ta roki Allah akan ya cire idanun ta akan duk Abinda zai faru da kuma Wanda ya faru a baya, tareda neman juriya da nasara a rayuwar ta ta yanzu da kuma nan gaba.

Washe gari aka tashi da shagalin biki, Wanda tun da safe jikin ta yagaza dauka daka kalleta kasan tana cikin tsananin damuwa da kadaici, Ahmed ya boyewa ganin ta baki daya, Wanda batada masaniyar baida lafiya ne, Saida khaleel ya kawo mai likita batareda sanin kowa ba. Yana tareda d'an uwan shi har safe bai runtsa ba Abu biyu ke damun shi a zuciya, why yayan shi keda mugun hakuri? And wani gefe kuwa kanshi yake tuhuma, why why why? Domin shi karan kanshi da baida karfin zuciya cikin wata biyun nan da ya ga likitan zuciya, he is in big trouble, big mess Wanda yasani shi karan kanshi, he is a fighter domin duk Wanda ke yaki da zuciyar shi shine babban jarumi, Wanda kowa yasan yaki da zuciya Abune mai matukar wahala.

Dafashi da akayi yasa ya dawo cikin hayyacin shi tareda kallon yayan nashi, daya tashi zaune yana murmurshi kadan, kana ganin shi kasan cikin jinya yake. "All night bakayi bacci ba khaleel, why kuma kasan yau ranar Auren kane dole ka raya wannan daren. "Yaya ya jikin naka? "Alhamdulillah inajin sauki a jikina, ya Naziya kagan ta? how is she? " Yaya all you worried about is her? Why bayan ita bata damu da neman kaba if tasan Abinda ya dace me zai hana ta nemeka? "Kafada mata banda lafiya? "Nop Yaya. "Kaga batada masaniya, and please Khaleel take care of her, that girl deserve to be happy. "How Yaya bayan kaine zaka kula da ita she needs you more than me, kaine mijin ta. "I know khaleel. Ya Rungumo shi a jikin shi, yace "you have alot of responsibility, mommy, Fauziya and our company, I know you are stronger than me. "Yaya please stop All this you know you're breaking my heart, Yaya I have something in mind, Wanda bai kamaci in sakashi a zuciya ta ba I hate myself please forgive me. "What is that khaleel, me kakeso I promise to give it to you koda rayuwa tace saboda kaine farin ciki na. Wasu irin hawaye masu zafi suka gangaro a kwayar idanun shi for the first time, yaji he need them, saboda sometimes tears heal some wounds.
"Noo Yaya bana son destiny din da zai zamo musayar rayuwar ka, I don't want that destiny, but Yaya is really painful, bansan yanda zanfada maka ba and please don't ask me too much question bazan iya amsaka ba. "Is OK bazan tanbaye ka komai ba, but dole inji dalilin zubar hawayen jarumin kani na, what is that, meye ya taba zuciyar the stone heart Ibrahim khaleel? "Yaya. "No am not asking the new ango but am sure kana kukan farin ciki ne yau zakayi Aure and you will last on bed more than me. Yafada yana daga gira daya, ya tuno da irin question din da yamai ranar da sukayi hira a dakin shi da Naziya. Dafe kanshi kawai yayi tareda sakin yayan nashi, "Hmmm yaja dogon Ajiyar zuciya, "I know kani na sai yafi thirty minutes. Mikewa yayi cikin sauri, am coming Yaya bari inje cikin gida. Yafita fuuu dagashi sai guntun wando yau ko singlet babu a jikin shi yama manta da taron matan dake gidan, burin shi ya ganshi a cikin gidan.
Dayake kowa na sha'anin gaban shi sannan kuma an Waye ba wani Abu bane don haka no one care, har ya shiga main palo, dai dai taci kukan ta tayi nak har wani zazzabi takeji ta fito jikinta kamar ba ruwa ba Wanda ya damu da ciwon zuciyar ta. Taga shigiwar khaleel fuuu ya wuce dakin shi, bayan shi ta hanga yana shigewa Wanda dole ta bishi taji inda zataga Ahmed domin ta gaza zuciyar ta tayi rauni, ta leka dakin khaleel din yafi sau goma tun jiya dukan su basa ciki, infact ko gyaran datayi bai baci ba.
Shiga yayi ya kalli gadon cike da wani irin zafi zuciyar shi keyi Wanda bai taba jin irin shi ba, ya fisge zanin gadon ya jefar tareda zubewa kasa yasaki wani irin kuka mai karfi kadan Wanda ba Wanda zai jishi,

Tayi matukar tsorata da kuma jin mamakin kukan namiji, tun dosowar ta kofar dakin kuma tanada yakinin a cikin dakin khaleel yake fitowa, wake kuka haka? Bude kofar tayi cikin Sauri, ya dago fuskarshi karab cikin idanun ta, tayi matukar girgiza, bata taba kawo zata ganshi yana kuka ba, meye yasa shi kuka haka ? The great mai girman kai, this is serious, kokarin juyawa tayi kawai domin a tunanin ta koma meye ba hurumin ta bane. "Wait. Yafada cikin sanyi tareda mikewa yana share hawayen shi, tsayawa tayi cak har ya iso wurin, hijabin dake jikin ta tarike gefen shi gam tana jiran taji me zaice, saida ya matsa ya tura kofar ya datse, ta zaro idanun ta, "meye na rufeni a dakin ka, bana son rainin wayau ka bude min kofa intafi. Tafada bakin ta na

rawa kamar zatayi kuka, "Hmmm, me kike nema? "Mijina. Tafada kai tsaye batareda ta kalli y'an da ma yake ba, "bakida lafiya ne? Saurin dago kanta tayi ta kalle shi akaron farko tun shigowar ta, da gudu ta datse makullin idanun ta, "Auzubillahi. Tayi saurin ja baya, Wanda Abun yayi mugun batamai rai fiyeda tunani,
Bata taba ganin bear chest din namiji ra'ayil aini ba sai yau ga kirjin nashi da shegen fadi da wata irin suma mai tada tsigar jikin mace,
Fisgo hijabin ta da yayi cikin zafin rai yasa tafara istigifari tareda bude idanun ta tana mai kallon that's why I hate you, "you are behaving like baki taba ganin namiji ba kaya ba, kina Abu kamar wata saliha, look karki daukeni jahili ko mara sanin iyakar shi, I know my limit shiyasa kike tsaye agaba na batareda wani Abu yafaru dake ba, ni kikeyiwa a'u'ziya? kamar Kinga shedan. Cikin tsiwa da zafin zuciya tace "meye banbancin ku da shi, kana ratsa mata tsirara bayan kasan haramcin Abun sannan wuce limit! yes you cross All the limit da ka rikemin hijabi now let me go. Tafada cikin karaji, saurin sakin hijabin yayi tareda sai daita kanshi yana shafo sumar kanshi tareda d'an naushin iska.
"Am sorry, kiyi hakuri am worried ne because my brother is sick tun jiya. Saurin natsuwa tayi tareda sakin jiki tace "Ina yake? Jikin ta na rawa, yana part d'in mu na waj... Ko gama sauraran shi batayi ba ta bude kofar ta fice da sauri,
She knows it shiyasa itama batada lafiya, saboda Ahmed d'in ta is sick,
Tana fita ya datse kofar tareda zubewa kasa ya hade kai da guiwa, "khaleel you are so dead. Ya furta yana sakin Kara.
Da taimakon mai aiki tasan inda Ahmed din yake Wanda shine karon farko data shiga wannan part din Wanda ya kamata ta kasance a ciki, tundaga falon take zuba ido domin tasan dukiyar dake ciki bata malam bace, infact ko kudin labulen dake cikin falon zai siya kaf kayan dakin ta, wani irin karyewa zuciyar ta tayi takasa daga kafarta daga nan ta zube, shikenan tata takare za ashiga tsakanin ta da mijin ta domin tasan burin mommy ya cika ta Auro mai burin ranta,

Jin kukan ne yasa yafito daga bedroom ya ganta a wurin da gudu ya karaso gaban ta, "Naziya Naziya, ya zube tareda rikota zuwa jikinshi, "Am sorry please, Allah yagani kukan ki yafi komai daga min hankali please kiyi hakuri komai nada dalili believe me, dago kanta tayi ta ce"harda guduna kadawo dakin Amaryar ka tun bata tareba, Ahmed meye ribar zama na a karkashin inuwar Aurenka? "Soyayya ta Naziya, soyayyar kice Ribar Auren mu, Wanda nayi miki Alkawari muddin baki tare cikin gidan nan ba bazan taba samun farin cikina ba kece walwala ta kece farin cikina, am sick Naziya saboda damuwa datayi min yawa zuciya ta na ciwo. , Hawayen ta tayi saurin sharewa, "Ahmed Ina son zama dakai, ka koyamin sonka duk da bamu zauna tare ba, halin ka hakurin ka tarbiyar ka, Ina son halayen ka, kaddarar rayuwar mu, nadauka am not blaming you for that shine kaddarar mu, please karkayi ciwo zan shiga damuwa kaji, tafada tana shigewa cikin jikin shi da kanta kuma a karon farko, taji ta iya sakin jiki dashi batareda kunya ko nuku nuku ba, Ajiyar zuciya ya sauke ya gyara zaman shi dakyau tareda rungume ta gam a jikin shi shima, "Wow Naziya sarkin kunya yau ta rungume ni haka? What a lucky day, kice intashi ingirgice kawai mu shige daga cikin dakin mu yau. Sunne kanta tayi cikin kirjin shi tana jin kunya, tareda kokarin tashi ta gudu, "no karya ne yarinya kinkawo kanki don haka let go inside ki bani Abinci inci domin rabona da Abinci tun shekaran jiya, "why? Tafada cikin damuwa, "because am worried about you kullum Ina tunanin Ina shiga hakkin ki idan namutu ubangiji zai

tanbayeni hakkin ki Naziya, kiyafemin kinji. "No bakayi min komai ba, muje in hada maka Abincin kaci, akwai komai a ciki ne? "Yes let go, yafada yana Rungumo kugunta. Ya dade a tsaye yakasa shigowa falon yana ganin yanda take shigewa jikin Ahmed, komawa yayi kan kujera ya zauna tareda runtse idanun shi gam only God knows what is going on in his mind,

Dagewa tayi ta shirya mai girki lafiyayya domin takara zama expert yanzu saboda shine kawai aikin ta a gidan, yana biyeda ita har cikin kitchen din, yana shige Mata harta gama yace suje falon domin yaji muryar khaleel na waya, kuma shima tunjiya baici komai ba saboda yaga yayan shi baici ba, tayi mugun jin haushin shi domin ya katse musu lokacin mai dadi ta hanyar zuwa musu gida,
Fitoda komai yana tayata, yana zaune a wurin batareda ya motsa ba, idanun shi a rufe har suka jera Abincin, tana gefen Ahmed yasa hannu ya cire hijabin jikinta batareda ta shirya ba, doguwar riga ce a jikinta mai kyau ta kanti, wadda ta d'an kamata shiyasa take yawo da hijabin, saurin kallon shi tayi tareda narke fuskar ta "kana so ingudu ne? "No wife inaso inyi kallon matata ne, Kinga yanda kikayi kyau, and,,ya matsa daidai kunnen ta ya rada mata "this your chest baby please agama abani hakkina I need them very badly.
Hannu tasa ta datse fuskar ta tana girgiza kai, "Allah zantafi fa. Cikeda wata irin murya mai daukeda tsantsar shagwaba mai burge y'an maza, Wanda saida khaleel ya daure ya kalleta, a yau yake ganin dariyar ta da kyau hade da farin cikin ta, he feels a little happy one side, ga dimple d'in ta wow,. "Yaya Am hungry yafada domin katse moment din, "let eat brother, ta zuba musu tareda cewa "wannan Abincin ai wasu basu san dadin irin shiba, oh zaka iya cin Abincin mu na Nigeria ba kyankyasai ba. "For the first time a lokacin yaji wata irin dariya tazomai, shima Ahmed Saida ya dara, "ke Waye yafada miki sunan su kyankyaso? " oho nidai ai mutum ba Abinci yakeci ba sai tarkace, daga kunama sai k'wari.
"Hmm, kawai yace yafaracin Abincin shi batareda yace tak ba yaci sosai saida ya kusa cinyewa tace "little brother inkara maka ne? Dago kanshi yayi ya kalleta wani iri kafin yace "am OK Aunty babba tanks. Ya mike, "Wow Wato kasan Aunty karama na zuwa ko? Harara ta watsawa Ahmed d'in tareda daukar hijabin ta ta Mayar, zata wuce. "Wait my Hajiya ai muje a yimin wanka ki karasa ladanki tukuna.
Kokarin tafiya takeso tayi, khaleel yace "Yaya please let her go kafin mommy ta ankare. "Muje intayaka tafada kai tsaye, domin batasan meye matsalar shi na yimusu karan tsaye ba yanaso ya hanata sakewa a lokacin da ta samu damar ta,

"Toh munafuka Y'ar gidan masu kwana kan buzu, zoki fita shashasha, ko kunya an narkawa yarinya dukiya kinzo kin shige, zo ki wuce, kai kuma Ahmed idan ka wuce iyakata banyafe ba, kaima khaleel dakai ake haduwa anamin bita da kulli, kuzo ku shirya ku tafi daurin Aure, in mace ce matsalar ka Ahmed na zabo maka ta kece raini ba wannan Y'ar shilar ba, koma daka nayi baki. Da gudu ta fita while khaleel ya wuce Abinshi batareda ya tanka ba Ahmed ma haka ta karaci sababi tareda turo masu aiki su Kara gyara duk Abinda aka bata a turare shi.
Saida ta shaki kukanta ta tashi tayi wanka ta caba Ado wayar ta ta dakko taga sakonnin shi da basa taba rabuwa da wayar ta, "Am sorry matata idan muka dawo zankira ki mu fita shakatawa kinji. Dariya tayi kamar dagske yanzu mommy nace wa Ahmed zai sunne kai, "my gentle man.

Tafada cikin nishadi, so hana ganin laifi,

Biki yayi biki ko Ina ba masaka tsinke a cikin babban birnin na kano a yau Auren yaran manyan mutane guda hudu at once, ga kuma Y'ar masu kasa Wato fauziya,
Daurin Aure ne Wanda ya jirkita garin ba kadan ba manyan baki ta ko Ina, kawu wakilin Angwaye Wanda baisan da zancen Auren Salifa ba sai ranar Auren, ya fara fada kamar zai Ari baki, har cikin gidan yazo ya kirata "Hajiya bilkisu halina na nan, yanzu saboda Allah yaro Aure wata biyu kisa ya karo Aure? Hajiya bilkisu kiji tsoron Allah. "Toh nidai bani nasa yaron nan Karin Aure ba ka kirashi ka tanbayeshi. "Koda bani na haifeshi ba jini nane nasan halin Ahmed nasan tirsasashi kikayi kuma Ina gargadinki da kibi a hankali. Shigowa Khaleel yayi ya zauna tareda gaida kawun yace "don Allah kasa baki ta bar yarinyar ta tare a part d'in ta kafin wata tazo kuma kawu ai itace uwar gida yakamata ace ita tafara shiga wancan gidan. "Yanzu kokarin kai karata kakeyi Ibrahim, Wato ya turoka kazo kasa kawunku ya yanke ni toh ka koma ka fadamai wallahi sai Salifa ta shiga Wannan gidan kafin Wannan Y'ar gidan malaman ehem. Tayi fuuu ta shige, ya so ya cire son zuciya ya agaji yayan shi amma mommy, Hmmm. "Khaleel ku shirya mu wuce ka Kira d'an uwan ka, mu ake jira,. Yafada domin lokaci natafiya kuma suntara manyan Kasa harda mai kano baki daya, kuma zai dawo mata idan komai ya natsa.

Andaura Auren fauziya da Khaleel sai kuma Salifa da Ahmed, Wanda akan sadaki mai matukar tsada akan miliyoyin kudi, domin gadarar mommy, Wanda Ana gama daurin Aure angwayen suka dawo dakunan su kowa kajishi shiru, ba wani motsi, lokacin da aka Kira mommy andaura ta rangada guda tareda kawayen ta, kannin mijinta ne suka iso suna Allah Sanya Alkhairi badon sun soba, babbar tace Ina uwar gidan Ahmed d'in? Tana nan zuwa anjima za akawo ta.
Mommy tafada da gadara, "Hmmm Allah ya shiryeki bilkisu Wato harda yayan mu bai duniya baki canja bakin hali ba ko?, to wallahi sai Kinga sakamako idan kika cutarda Y'ar mutane. "Toh ku dama wayake taku dama ai duk kannin miji y'an bakin ciki ne don haka ni yau banda lokacin ku nayiwa ya'ya na AUREN GATA.
Taci gaba da guda, dakin Ahmed suka nema inda suka sameta zaune yan uwan ta sunzo tana ta walwalar ta ta fauwala wa Allah, Wanda ta mugun burgesu zama sukayi a dakin suka sake sosai sukasha hira anan suke fada mata su gwaggwnin mijinta ne, ta saki jiki ta kula dasu itama dasu Aunty Raliya sai hira sukeyi.
Damuwar ta kadan ce zuciyar ta na wurin Ahmed batasan halin da yake cikiba Wanda saida yakira likita ya dubashi yace "gaskiya Ahmed idan zuwa gobe bakaji sauki ba kazo Asibiti ayima xray saboda ciwo a kirji yanada matukar Matsala.
Godiya yayi yasha maganin shi ya kwanta yayi bacci sosai har magrib.

Taro ya ragu zuwa Karfe bakwai duk taron Naziya sun watse sai ita kadai, yau ta yabawa d'an gin Ahmed harda y'an gidan kawu gefenta suka tare sun share mommy da gayyar ta, yanzu bakajin komai sai kai da kawon su Aunty zarah iyayen ango,
Takwas aka kawo Amare Wanda kafin Wannan lokacin ba Wanda yasan inda angwayen suke. Main house aka shigo dasu cikeda guda Wanda tanaji, a take wani kuka yazo mata, shikenan

rayuwar da tafara mafarki watace zatayi da mijin ta, shikenan sun samu third party tunkafin su mori Auren su.
Saida suka gama feshe feshe kafin kai Amaren gefen su wainda kowacce cike take da tata salon rashin kunyar hade da rawar kai..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
Y'AY'AN GATA
And now AUREN GADO,

Ga masu son su biya ga account details dina, * NAFISA HASSAN SANI 7304736012 @ FCMB* sai Ku min magana ta wannan number 09069200154

ğŸ†“ page

1â*ƒ*£7â*ƒ*£&1â*ƒ*£8â*ƒ*£

..... Sai Karfe goma sha daya suka shigo main house, mommy na zaune sai faman jiran su takeyi,ta gwada numbobin su ba Wanda yake shiga, tanata sababi Su zarah na tausar ta, da sallamar shi ya shigo cikin falon while khaleel na biyeda shi cikin shigar shadda bugaggiya Y'ar gaske fara dal, "ko kin ga y'an rainin hankalin ko sai yanzu zasu shigo gida kusan Karfe goma

sha daya. "Ahmed ne ya matso gefen ta tareda zama yana gaida Aunties dinsu, tareda cewa sorry mommy muna tareda Abokai ne. "Which abokai? Kai inkanada Abokai shi Wannan miskilin nadasu ne? Kun bar ya'yan mutane sukadai suna jiranku kamar masu gadi.
Carab ya bude baki a karon farko yace "jiran me sukeyi mana? Bayan ba ayi budar kai ba, sai su jira nan da sati daya idan an yi budar kai sai muje wurin su ni bacci nakeji, Yaya good night.
Yafada batareda ya jira Amsar suba ya wuce Abinshi, ido kawai Ahmed yabishi da shi, bakin mommy a sake tace "Allah ya hadani da yaron banza, kai kuma bazaka tashi ka wuce dakin Amaryar taka ba? "Mommy gaskiya ne ita baza ayi mata budar kan ba? " ubanka kaji tashi ka wuce ko ranka ya baci yanzun nan, shima zanje in same shi. Mikewa yayi domin baijin dadi sosai dauriya yakeyi kuma Allah yagani bayason kowa yasan halin da yake ciki yanzu.
Yana kallon kofar dakin shi kamar yashiga yakeji yasan halin da take ciki, Amma ba hali mommy ta kasa ta tsare. "Za abiyoka da kazar Amarci nasa anyi muku gashi mai kyau. Ko amsawa baiyi ba ya fita, a zaune Amaryar tashi take tayi dai dai cikin wasu irin fitinannun nighties duk jikinta a bayyane gata ba wani shahararren kyau ba, sai faman tauna chewing gum takeyi tana kas kas kamar wata tsohuwar karuwa.

Tundaga falon ya hango ta kafa daya kan daya tana jijjiga, zai iya cewa yaune karo na biyu ganin shi da ita Wanda baima san ta Ina zai fara yimata magana ba, domin ko ganin farko bai wani mata kallon arziki ba, don haka ko yanzu yana shigowa ya dauke kanshi ya wuce ta gaban ta. "Kai, tace cikin zafi. "Kashi ka wuce? ace ankawoni tun Karfe takwas kowa ya watse ya barni baka shigo ba sai yanzu? kuma ka ganni kamar wata Kashi ka gani. "Oh sorry ya fada batareda ya kalle taba domin bai sha'awar hakan, murmurshi tayi tareda matsowa tana karkada jikin ta da shirin rungume shi, yayi saurin ja baya tareda cewa "please bacci nakeji sosai kuma kaina naciwo, am very tired please let me go. Ya wuce da sauri yabarta tana cizon yatsa, batasan da yanajin lafiya yau sai ya nemo Matar sonshi yaci Amarci kota halin Yaya, Amma bayajin dadi shikadai yasan me yakeji a jikin shi. Yana shiga dakin shi ya datse gam batareda ya jira wani Abu ba, idanun ta sun nuna mai zata iya mai fyade inyayi wasa ta karasa shi, saida ya kwabe ya zube kan gado domin yayi sallolin shi a waje, ya janyo wayar shi yafara neman ta, tana kan dadduma tana lazumi taji Karar wayar, tasan shine don haka cikin Sauri ta mike ta dauka, Ajiyar zuciya yasauke yace "Y'ar Aljannah." Ina wuni, ta gaidashi cikeda tausayin kansu domin yama fita zama Abin tausayi, "ba lfy my wife, ko in zo ne? " aa. "Why?" mommy na falo suna hira. Hmm! zaki tayani hira har safe? eh, Amma hakkin Amarya fa? "Don't say that again sai kisa inji guiltiness akan ki" naki hakkin fa? " ni na yafe. "Nikuma fa? Ni Ina bukatar hakkina Naziya, kinsan cewa ba Abu bane mai sauki namiji yayi ido biyu da Mace kamar ke ya kawar da ido ba, mommy ce ta tsaya min akan layi da tuni munfara lissafin wata biyu cikina. Rufe idanun ta tayi gam saboda kunya kamar yana ganin, "shy girl, nasan kin rufe ido.
Hira sukasha sosai yana yi yana bata hakuri tareda alkawura masu yawa.

Gefen Amarya ta cika ta batse momyn ta ta Kira tana kuka tafada mata angon yaki ko shigowa dakin ta, a daren Karfe biyu ta Kira mommy tana sababi, "nifa ba dutse nakai muku ba yarinya ce shakaf mai jini a jika don haka kari nji kar ingani, zancen wulakan ta min ya'. Tayi ta bata hakuri kafin ta gwada kiranshi yana busy, ta hakura ta barwa safiya, banzar kuwa kazarta ta yaga iya son ranta ta sha baccin ta nak, domin tasan dai dole yagama gudun shi yadawo mata

domin a shirye take tsab.
Fauzy ma tasan halin kayan ta batasa akaba tasani tunda dai ta shigo, a juri zuwa rafi wata rana tulu zai fashe, Amma zama daram itada Khaleel tunda buri ya cika.

Gefen shi ma baccin shi yasha har safe batareda tunanin wata kaya fauzy ba,sai Asuba ya fito da shirin zuwa masallaci, ya samu mommy zaune itada bata tashi da wuri, tace Yauwa ku nake jira kuyi sallah kuzo kaida d'an uwan ka Ina jiran ku yanzu, fita yayi kawai Abun shi yasan tatsuniyar gizo bata wuce ta k'oki.
A masallaci suka hadu, saida suka idar yace "her excellency is calling. "Who? "Your mom. "Oh ba MAMAN ka bace kai? Shiru yayi kawai, domin shikam baisan me zaiyi mommy ta canja ba, ciki suka shiga yana mai nasihohi masu ratsa jiki da taba zuciya, suna saka kafa tafara sababi "nikam yau zanyi maganin ku duka sai kunfada min inkunada wata uwar bayan ni, Ina muku gata yara kuna watsa min kasa a ido, toh yau dukan ku Ina bukatar ku dakin matayen ku banason jin rashin kunyar ka Ibrahim. Sannan kai tunjiya Ina kiranka kaida ubanwa kake waya? Da ka kwashe tsawon dare kana busy? "Mommy kiyi hakuri, nida Naziya ne. "Innalillahi, Wato tanan ka bullo Ahmed kuna hadewa ta waya, ita kuma munafuka kamar salaha, mayya ta lashe min kurwar yaro to wallahi zanyi maganin Abun, karyar buzu tsohon ta yakeyi, mu munsha tabara mun sha yaseen , ta rangada mata Kira, Wanda duk tanajin komai.
Da sauri ta fito da hijabin sallar ta tace "gani momy. "Ni ba uwar ki bace ta cikin bukka munafuka, ke kin kaini bango hakurina ya kare akan ki inba zuciyar kare kikeda ba kizo ki koma gidan ubanki, ace mace don rashin zuciya miji bai neman ki baidamu dakeba saboda kin rab'i Ac kin like kin manne kamar kaska, ke wa ya iya da bakin nacin talaka? zo don Allah kibarmin gida Ahmed dai yayi Aure aje aci gaba da cin tuwon dawa da gero.
Tafada tana nuna mata hanya.
Kuka takeyi tunda momy tafara magana Wanda Wanda duk sauran bakinta sun taso, fauzy ma data bugo sammako ciki taji komai, tana dariyar mugunta tareda komawa ta Kira Salifa tazo kar ayi bata, domin tasan da zaman Naziya kuma tasan komai akai don haka tasan zatayi farin ciki yau idan taga Abinda mommy tayi,

Dafe kirjin shi yayi yana mai wani irin zafi tuni numfashin shi yafara seizing batareda kowa ya luraba, domin kan Khaleel na kasa idanun shi kamar wuta saboda bakin cikin halin mommy, da kuma irin cin zarafin da takeyiwa Naziya.
Zubewar da yayi Tim yasa khaleel ya zabura yayi kanshi, Wanda yabawa sauran damar ganin Abunda ke faruwa, har mommy tuni tayi dif kamar ruwa ya cinyeta,
"Yaya" khaleel yafada cikin tashin hankali, ya tarai rayoshi, saidai tuni jini yafara bin hanci da bakin shi, wani irin zubewa Naziya tayi jikin ta na rawa kukan da take ya tsaya ba Abinda take kallo sai jinin dake fita a fuskar Ahmed, cikin tsananin jarumta da mazantaka khaleel ya cirashi da gudu yayi waje yana mai kwalawa driver Kira yakawo mai key, yasaka shi cikin motar tareda rungume shi cikin tashin hankali driver yaja suka fita a guje domin gari yayi haske,
Mommy daskarewa tayi tana jin numfashin ta kamar zaifita saboda tashin hankali, Ba Abinda takeso duniya sama da ya'yan ta da kuma dukiyar ta, batasaon rasa kodaya a cikin biyun nan, don haka ganin yanayin Ahmed yasa tajita kamar ana zarar ranta. Saida zarah ta jijjigata ta dawo dai dai, "zarah muje wurin dana ingan shi, kar yarona ya mutu muje inga halin da yake

ciki.
Ita ta dakko mata key da hijabi suka fito, su fauzy na tsaye turus basuda niyyar motsi, sanin halin khaleel yasa suka Kira driver yafada musu inda suke, Naziya kuwa kuka takeyi kamar zata mutu, idan ta kalli jinin dake kwance inda aka dagashi, hijabin jikinta ta zare cikin rudu ta goge kasan tiles din tsab tana kuka, Aunty Raliya ta Kira tana kuka tafara fada mata, ta lallashe ta tareda cewa "kiyimai Addu'a Allah yabashi lafiya ba kuka ba, banason shirme. Toh Aunty. Ta datse kiran tana mai dauro Alwala ta koma kan dadduma hannayen ta a Asama domin neman sauki wurin mai duka.

Gefen mommy koda suka isa Asibiti daidai da zuwan kawu modu domin Khaleel ya kirashi, hawaye yake sharewa tareda sintiri, kawun na zuwa yace " Meya same shi khaleel? " d'an uwana Kawu yana Aman jini hanci da baki suna ciki har yanzu basuce komai ba, ya mugun fita hayyacin shi, matsowa Mommy tayi jikinta na rawa "Ibrahim me yasamu d'ana?. Dago idanun shi yayi ya kalle ta cikin kallon kece sanadi mommy. "Look at it mommy kinga irin ta ko, d'an uwana na cikin Wannan halin because of you, mommy don dai ke uwata ce Amma in wani ne bazan taba yafe mai ba, now just pray d'an uwana ya tashi lafiya I promise dole abashi farin cikin shi that's enough! hakurin shi yayi yawa. "Ibrahim ' kawu ya daka mai tsawa, "me yasa kake fadawa mahaifiyar ka magana haka, me yafaru? Matsawa yayi cikin karyewar zuciya, ya fada jikin kawun ya saki kuka mai zafi Wanda ba Wanda zaice jarumin namijin ne ke irin Wannan kukan.
Bubbuga bayan shi kawu yayi " ya isa insha Allahu zai tashi lafiya, Kayi shiru haka. Fitowar likita ne yasa ya yi saurin share hawayen yace "lafiya doctor yaya na fa? "Please kaine Khaleel?. "Yes". Come your brother is calling you.
Bin likita yayi da Sauri kawu ya bishi shima, mommy zata shiga likita yace su tsaya waje mutane zasuyi yawa a emergency.
Jinin ya tsaya kadan sai Wanda ke bin hancin shi kadan kadan, yana isa yaja gefen rigar shi ya goge mai, "yaya please ka cire damuwa zaka tare da Matar ka I promise you kaji. Wani irin numfashi yaja mai wuya tareda fitarda murmurshin dole.
Yace "kawu", tareda mika hannu yace ga Amanar d'an uwana, kawu don Allah ka kula dashi ka tsaya mai akan komai, inason yayi farin ciki, kawu don Allah make him happy kar ya shiga damuwa idan bana nan, Khaleel take care of Naziya, where is she? Please call her, ka kawo min ita Ina so in roketa gafara please go and bring her. Ja da baya yayi tareda girgiza kai, " no no no stop that yaya nothing is going to happen to you, bari inkawo ta please yaya kadaina magana haka ciwo ai ba shine mutuwa ba, I don't like this, stop it. Am sorry Khaleel. Yafada yana mai kallo mai cikeda sakonni, fita yayi da sauri yana yi kamar zai tashi sama, riko hannun kawu ya kuma yi, "kawu don Allah kar Kabari Naziya ta fita agidana ko bani, kawu kabawa Khaleel ita ya Aura nasan zai bata kulawa saboda soyayyar da yake min please kawu". Mugun sanyi jikin kawun yayi domin Abun ya tsorata shi, a'a Ahmed kadaina irin Wannan maganar, haka d'an uwana yatafi yabarmin Amanar ku, bangama saukewa ba zaka bani wata, Insha Allahu zaka tashi kaji, likita kuyi aikin ku mana,. Yafada cikin tsawa, "Alhaji muna bakin kokarin mu Amma zuciyar shi tariga tagama kunbura shiyasa yake Aman jini, tunfarko yasan yanada ciwon zuciyar yabari tunani yashige shi Wanda yafi karfin zuciyar.

"Karka kawo min hauka nawa zanbiya ayi mai aiki, inba zaku iya ba infita dashi waje. Mommy ce ta shigo tana kuka tareda matsowa kusa da gadon da yake" Ahmed meke damun ka? Me yafaru dakai? Don Allah katashi.
Rikota kawai yayi dakyar ma yanzu yake fitarda numfashi, "ki ya fe min mommy na. Ya fada daya bayan daya yana riko hannun ta gam Wanda tanajin rikon cikin jijiyoyin ta rikone mai matukar karfi irin na fitar rai, koda takalle shi kafin tace wani Abu sai dai ganin jinin tayi yana Kara fitowa tareda kafewar idanun shi sama, kafin ya saki Hannun ta. Suman zaune tayi na wucin gadi kafin likita da kawu su gama magana su juyo, zarah ma tashigo, wani irin tsinkewa jinin ta yayi domin ba tantama Ahmed dai rai yayi halin shi,
"Innalillahi wa Inna ilaihirrajiun. Kullu nafsin za'ikatul maut. Kowane rai tabbas ne zai daddani zafin mutuwa don haka sai muyi fatan cikawa da imani, Ahmed dai yatafi yabar Wannan duniya mai cikeda rudani.
"Aunty Ahmed yatafi" Zarah tafada tana dora hannun ta saman kai, kawu wani irin zuface ta karyo mai tuni ya ciro hular kanshi yana fifita, "ya Allah" Kawai ya iya fada saboda sarkewar kalmomin bakin shi, saida zarah ta jijjiga mommy, kafin ta fasa kuka"wayyo Allah na ni balkisu Ahmed tafiya Kayi kabarni, why Ahmed why?
Rufeshi likita yasa Akayi da farin zanin gadon, yace Alhaji sai hakuri Ahmed lokaci yayi. Dakyar kawu ya iya saita natsuwar shi yana goge gumi kamar ya hadiyi kunama, ya ciro wayar shi a Aljihu ya yakira Khaleel, " kana Ina? "Yanzu na shiga gida kawu zan dakko Matar yaya. "Stay there muna zuwa. "Why yaya yac.... "Just do as I said, yafada cikin fada kafin ya katse kiran.
Shi ya hada komai yayi clearing aka basu Ambulance Abunka da kudi cikin minti kadan suka tafi da gawar su,
Mommy kamar ta haukace ji take kamar a mafarki wai Ahmed dinta ne ya mutu. Aunty zarah ido yayi Hulu Hulu.

Naziya tun fitar su take kan dadduma, zuciyar ta bugawa takeyi da karfi takasa ko motsawa, su kuwa Amare suna hakimce kowacce taci Ado kamar masu gasar gwal. Sun hakimce a falon,
A harabar kuwa Khaleel ya kasa gaba ya kasa baya saboda tashin hankali, ga umarnin kawu, yana daskare jikin motar yaji kukan Ambulance, wani irin kallo yake wa motocin su mommy, ganin yanda Aunty zarah ta riko mommy sannan kawu shima ya fito kai ba hula, ya maida idanun shi akan Ambulance yana kallon nurses din suna bude motar, ganin sunfito da mutum rufe da farin kyalle ya zube kasa war was, domin baya bukatar Karin bayani akai. Masu aikin ne suka ruga wajen shi domin jin faduwar tashi Tim.
Mommy ta tafi luuu itama tana shirin zubewa, shima ya mutu ko zarah? In ya mutu shima ni tawa ai takare kenan. Tafara sambatu, zarah ta riketa tana jijigata a'a Aunty bai mutuba, kai ku shiga dashi ciki, kawu dai nata gawa yasa aka shige dashi ciki, hakama Khaleel anyi ciki dashi, Wanda tuni hankalin kowa ya kawo kan abinda yake faruwa banda Naziya, domin Amarya Salifa ita kanta jikin ta yayi mugun sanyi, wane irin Abu ne haka Auren ta jiya miji ya mutu yau, Kukan da mommy ta fasa yasa Naziya fitowa jiki na tsuma da carbi, ganin mutum kwance akasa ga kawun su zaune agaba ya dafe kai yasa tafito jikin ta a mace tana sand'a kamar barauniya.
Kukan dasu Aunty zarah dasu Salifa keyi yasa ta gano duk Abinda yake faruwa. Dabas ta baje akasa kamar kurma, kafin kace me, tuni ji da ganin ta sun dauke.

Koda ta farko, taga dakin ta makil da mutane harda su gwaggon nin ta dasu Aunty Raliya da kuma matan kawu.
Zabura tayi tana kallon jikewar da jikin ta yayi da ruwan da aka rika kelaya mata,
Ganin ta zaburo Aunty Raliya ta riketa, "Naziya bi a hankali ruwa ne a hannun ki. Kallon hannun tayi, tareda kallon mutanen tace mafarki nakeyi ba mutuwa yayi ba ko? Aunty bai mutuba ko? Ku fadamin Ina yake?
Dafata kanwar malam tayi tace "ki yawaita Inna lillahi Wa Inna Ilaihir Raji'una Naziya. Tafiya takuma yi luuu. Suka kwantar da ita, kowa na share kwalla,
Khaleel kuwa saida akayi da gaske ya farfado, lokacin angama hada gawar Ahmed, zabura yayi kawai, ko digon hawaye yakasa fitowa a idanun shi.
Kannen shi ne yaran kawu maza suka rikeshi "yaya Khaleel bi a hankali karka fadi. "Let me go. Yafada cikin fada. Kafin ya fisge ruwan yafice cikin Sauri lokacin za adauki gawar zuwa makwanci, harda malam yazo gidan yau.
Cikin sauri yace "kawu kubari inyi mai Addu'a, fuskar shi ba ko Alamar hawaye domin ance kuka wuri yake samu watarana zuciyar shi ta cushe ta inda bako digon hawaye dake shirin zubowa.
Kowa yasan na zuci yakeyi Wanda ke cin zuciya, don haka malam yace "Ibrahima, ka saki zuciya Kayi kuka bakyau hadiye Abu yana illata mutum cikin sauri.
"Malam muje akai yayana makwancin shi. Yafada yanasa hannu ya daga makarar gefe daya domin yasan idan shine yayan shi zaiyi mai har wankan karshe, Amma tunda bai samu yimai ba shine zai sakashi cikin Kabari tareda samai kasa da binshi da Addu'oi.

Yabawa kowa mamaki yanda ya sakawa kanshi jarumta, har zuwa makabarta, inda da hannayen shi yasakashi cikin Kabari, tareda yimai kallon karshe, Wanda anan zuciyar shi ta karye ya fara fitoda hawaye, shikenan yayan shi yatafi, gatan shi Wanda saboda shi yadawo Nija, da ana dawo da hannun ago go baya da ya canja tsarin rayuwar Dan uwan shi , da ya hanashi shiga bakin ciki, Amma me komai mukaddari ne baida Wannan damar komai, yanda Allah yatsara haka zai kasance.
Lallabo shi akayi dakyar zuwa gida malam da sauran y'an uwan su, harma da mutane gari Wanda kowa mutuwar Ahmed din ta girgiza shi, Wanda sai ka mutu ake sanin halayen ka, wasu nacewa dazufa sun gaisa a masallaci, Wanda ita rayuwa haka take yanzu kana nan Anjima baka sai wani kuma, rai bakon duniya, Allah yasa mucika dakyau da imani..... ğŸ–Š

"Kai jama'a bantaba k'isa ba a littafina irin Wannan don haka nikaina na koka na girgiza Wanda nasan watarana saidai labarina nima zantafi, ya Allah Kayi mana kyakkywan karshe kasa mucika dakyau da imani don darajar ma aiki, S. A. WğŸ™

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA,
BARIKI AUREN SOJA,
MUK'ADDARI,
WANAKE AURE,
ZANYI BIYAYYA, Y'AY'AN GATA, And now AUREN GADO,

Ga masu bukatar Wnn littafi ku turo kudin ku ta Asusun banki na 7304736012 nafisa sani hassan Fcmb ko katin wayar ku ta Wannan number 09011251444, sai kuma y'an ğŸ‡³ğŸ‡ª Niger ku tuntubi Wannan number domin biyan naku, +225 0748153903, littafina Dari biyar ne kacal 500 sai najiku nagode,

my fans masu maganar Ahmed yabar k'wanshi, ai mommy zataji dadi gwara tayi nadama ta har Abada tasan Allah yabata yaro mai yi mata biyayya har bayan idon ta, kuma shine zai zamar mata tabo har karshen Rayuwar ta don haka muje zuwa dama bahaushe yace in kana mugunta bakayi wa kanka ba to baka cika mugu ba

Last ğŸ†“ page

1â*ƒ*£9â*ƒ*£&2â*ƒ*£0â*ƒ*£

..... Naziya kuwa Abin kamar a mafarki haka take ganin shi, koda ta farfado manya suka natsar da ita sunayi mata nasiha, sai Ajiyar zuciya takeyi takasa koda fitarda hawaye, Saida Akace mata har an sallace shi an dangana shi da makwancin shi ne ta fasa kuka, shikenan yanzu bazata kuma ganin shi ba, haka rayuwar su tazama tarihi Auren ta dashi yazama tarihi, Wannan wace irin kaddara ce ta bullo a cikin Rayuwar ta? Istigifari ta farayi domin kar Imanin ta

yayi rauni, Amma kowa yasan bakaramin ciwone a zuciyar taba rashin mijin da kukayi Aure wata biyu yatafi yabarka, kowa ya tausaya mata, har kanin Baban su Ahmed din na gidan sunzo, mommy kuka take tana birgima, cikin masifa Aunty Fatima tace "Wallahi bilkisu kukan ki baida Amfani ai saiki tashi kiyi farin ciki, Ahmed yatafi yabar miki duniyar, ba Auren kece raini ba! yau gashi yabar miki matan duka, kiyi Addu'a ma ko jika ace yabar miki jikin Y'ar talakar da bakyaso, kin hana yara sakat ai munsan komai kallon ki mukeyi kawai kijira Abinda zai biyo baya, wallahi sakamako na zuwa. Matar kawu ce uwar gidan tace "Aa Fatima kubarta haka rashin d'a tayi kuma kuzo ana zama kuna tada fitina. "Nayi shiru Matar yaya".
Kuka Momy ta fasa, yanzu take data sani mara Amfani Ina ma Ina ma, Allah yasa Naziya tanada ciki, Allah yasa zata ga Abinda zai cire mata kewar d'an ta mai hakuri, Kuka takeyi mara Amfani domin batada damar maida hannun agogo baya.
Khaleel kuwa zazzabi mai karfi ya rufeshi Saida likita yazo ya kuma dubashi, su Malam na tausar shi tareda mai nasiha mai ratsa zuciya, kabi d'an uwan ka da Addu'a shine kawai soyayyar da zaka nuna mai yanzu.
Gefen Amare Fauziya tafi d'an natsuwa domin mutuwar ta taba zuciyar ta don duk shashancin mutum yau ace Wanda kasani yafadi ya mutu, dole kaji jikin ka yayi sanyi idan akwai Imani a tareda kai.
Gefen Amaryar Ahmed mommyn ta da y'an uwan ta nafama akan ta shirya takaba tace atafau bazata yimai takaba ba tunda ko kwana basuyi ba tare, maganar har taje kunnen mommy, bata iya cewa komai ba domin ta shiga rayuwar kurame na wucin gadi, Naziya kam bazata iya bude baki tace wai mijinta bai kusance taba, domin akwai Alkunya kuma ko saboda soyayyar datake mai tareda hakkin igiyoyin nan uku dake wuyan ta dole tayi mai takaba, in akwai Abinda yafi haka ma zatayi mai domin ita tasan tayi rashi babba Wanda maida irin shi zaiyi wuya, ita ai jitake ma ta rufe shafin Aure a rayuwar ta.
A cikin kwanakin uku zuwa bakwai bamasu sauki bane ga duk makusantan mamacin, tun daga kan mommy, Naziya, Khaleel da duk wasu masoyan Ahmed,
A dakinta take tanayi mai takaba mai tsabta tareda binshi da Addu'oi dare da rana, kuka kuwa kullum dare sai tayishi rayuwar da sukayi dashi batada tsawo Amma yabar mata memories da zasu rika tuno mata dashi har karshen Rayuwar ta.

Seven days

Khaleel Ko part d'in shi bai zuwa tun ranar da fauzy ta shigo ko kallon ta baiyi ba, Abinci ma baya iya ci ya rame a fuskar shi sosai daka kalle shi, Aunty zarah ce ta shiga dakin shi yana zaune rikeda waya karatun Alqur'ani mai girma natashi, idanun shi a rufe, sanye yake cikin jallabiya fara, "Ibrahim" kazo Alhaji na Kira ta fada tareda juyawa, tashi yayi yana sa stop tareda rike gefen jallabiyar shi ya fita, a katon falon ya samesu dukan su har Naziya tana nade cikin hijabin ta, gefe daya Maman Salifa ce da ta Fauziya duk suna hakimce sai kuma Amaren a gefe, Wanda shi tun ranar da aka kawo su bai sasu a idoba, Kawu da malam ne zaune a kujera sai kannin kawun mata biyu gefe, mommy ce tayi shiru kamar ruwa ya cinyeta, kana ganin ta kasan mutuwar ta tabata. Kawun ne yace "Malam Abubakar na taraku ne anan saboda Abubuwa uku na farko dai Ina Kara mika ta'aziya ta gareka Ibrahim domin kai Kayi rashi, Allah ya Kara maka dangana tareda ikon daukar nauyin da aka dora a wuyanka, na biyu akan

maganar Matar Ahmed, sun kirani akan zasu tafi da ita gida domin bazata iya yimai takaba ba, don haka ga Malam muji shima idan zai tafi da Ita uwar gidan ne gida. Saurin dago kanshi yayi ya kalli gefen ta, sai yanzu yaga yanda ta rame tareda yin zuru zuru, gwanin tausayi, ya ce Kawu duk yanda kukayi daidai ne. Abinda ya iyacewa kenan,
Addu'a malam yayi kafin yabisu da nasihohi ya karayi musu ta'aziya, ya dora dacewa Idan so samune Naziya ta zauna a dakin ta, Amma a yanzu saboda dalilai masu yawa zan mayarda ita gida tayi takabarta, Allah ya gafartawa Ahmed.
Wani irin daci Khaleel keji a zuciyar shi, yarasa wane irin tunani zaiyi baida kalma daya da zai iya furtawa a halin yanzu,
Kukan mommy ne yasa suka kalle ta, ba Wanda yaji tausayin ta har Khaleel din ma, domin tsawon kwana bakwai din nan baya ko kallon gefen ta.

Toh Hajiya bilkisu Ahmed ya tafi, Amaryar da kika buga kirji kukayi mai yau tace bazata iya zama dashi ba, sannan Inada yakinin mugun halin ki ne yasa itama Matar tashi za a tafi da ita, domin ni Nafi kowa sanin halin ki bazaki taba canzawa ba, da zaki canza da mutuwar yaya na zata fara canzaki, mundade muna daukar mugun halin ki yau kinga ni, Allah yasa ki dauki darasin idan har akwai sauran kwakwal akan ki.

"Ya isheka Modu karka manta d'ana na rasa babban dana duk Wanda yayi kukan mutuwar nan Kara yayi min, sannan maganar bakin hali, naji abarni da kayana duk ko wacce tafi ruwa gudu cikin su, ni Abarni da zafin rashin d'ana kawai, tafada tana mikewa cikin zafi tayi daki tana kuka mara madafa.
Ko dago kai Naziya batayi ba Saida malam yace "su shukrah na nan zasu hada miki kayan ki su taho dake, ni zantafi dalibai na jirana a gida. Ya musu sallama yatafi. Saura y'an uwan kawai da iyayen matan, Maman Fauzy tace toh Saura mu yaza'ayi da yarinya tun da tashigo ace bata samu kwanciyar hankali ba.
Cikin zafi yace "Zaku iya tafiya da ita in kun so I don't need her.
Yafada cikin fada da kuma iyakar gaskiyar shi, "dama momy ta Aurota idan kunga bazaku iya zama ba ga hanya.
Cikin rawar jiki tace " no mommy please kuje ni Ina nan. Tafada domin tana matukar kaunar Khaleel, bayan ta aureshi da kyar ta yaya zatayi sake ta fita, don haka tuni ta kashe bakin uwar, salifa ce taja uwar ta gefe, "mommy nidai kinga kisa kawun su yasa Khaleel ya Aureni tunda anayin Auren gado, kinga yafi ma Ahmed din haduwa mommy wallahi zan zauna in ya Yarda.
"Y'ar gari nima tunani na kenan ai kinga yaron ya Tara dukiya kan dukiya gatashi gata uwar shi gata d'an uwan shi yanzu, ke fa uwar shi duk cikin mu tafimu kudi shegiyar, bari mukoma inyi magana.

Jiki na rawa suka koma falon lokacin Naziya ta mike tayi daki inda su Aunty Raliya ke hada mata kayan ta, daga Khaleel sai kawu sai gwaggon nin shi, mommy dasu zarah na daki,
Zama Maman Salifa tayi tana Washe baki "Alhaji Inada magana. Suka zuba mata ido kafin yace "munajin ki. "Yauwa nace ba, tunda dai ga d'an uwan shi mezai hana ayi tunani mai kyau a bashi Salifa sai a hada Auren gado. Wani irin saurin dago kanshi yayi tareda watsa musu kallon kun haukace ya ce "kuna hauka wallahi kun haukace, toh kusani kune sanadin duk Abinda ya

faru a rayuwar d'an uwana, koda ace mata sunkare a duniya bazan taba Auren Y'ar kiba, don haka kawu ni natafi Inka gama domin one more minutes a nan zanyi Abinda bashi bane. Yafada yana wucewa a zuciye,
"Toh kunji sai ku tashi kubamu wuri, inji daya daga cikin matan, shigewa dakin mommy sukayi jiki a sanyaye,

Dayar tace "yaya dakasa baki ya Auri Wannan Y'ar mai Hankali, itace Matar Aure ba wa'innan y'an barikin ba. "Zamuyi Wannan maganar ba yanzu ba kubari mu gama war ware rashin da mukayi sannan shima Khaleel baya cikin natsuwar shi yana bukatar natsuwa, company su ma manager din ne ke kulada komai tunda ba Ahmed.
Dakin mommy su zarah ke lallashin ta domin sunsan koma meye ita tafi kowa rashi, har suka samu tayi shiru tana Ajiyar zuciyar, Shigowar kawar tata yasa tace kuna nan Hajiya? Eh kawata ai na canja shawara, nace ai basai na dauketa ba kawai tunda zumunci mukayi niyyar hadawa tun farko ko yanzu bata baci ba tunda kanin shi na nan sai a hadasu Auren gado kawai.
Kallon su tayi kawai domin tasan Waye Khaleel kuma yanzu bata isa ta tunkare shiba sai bayan komai ya natsa, amma Ajiye mata biyu irin Salifa da fauzy Abun Alfaharin tane a matsayin surukai.
Zarah ce tace, "ai yanzu saidai abari komai yanatsa kafin Wannan maganar ta taso, kuma Karku manta yanada wata Matar fauzy kuma kinsan Y'ar waye. "Badamuwa nidai inzai Aure ni zan zauna da ko mata goma ne Salifa tafada, domin itafa kawai tasa rai.
"Oh Allah kasa mu zamo iyaye nagari ga ya'yan mu Amen.

Kwana ki natafiya Naziya yanzu tana gidan su duk kayanta dake gidan ankwashe har wainda bata moraba, tafara warware wa Amma kusan kullum cikin yiwa Ahmed Addu'a take da sadaka idan tasamu hali, har Azumi takeyi litinin da Al hamis domin Allah yakai ladan kabarin shi.
Khaleel kuwa haryanzu bai dawo dai dai ba, fauzy tayi binshi har tagaji bai komawa kanta, ko fuskar shi bata gani. Yau yana kwance a katon falon mommy ta shigo ciki ita kanta ta rame,
"Ibrahim, wai kai wane irin yaro ne, yazaka sawa yarinya ido tun kawo ta gidan ku bayan kasan akwai hakkin ta akan ka, kai bazakayi koyi da halin d'an uwan ka ba, Ahmed dina ba haka yake ba, idan har kaunar da kakewa d'an uwan ka gaskiya ne Kayi koyi da halin shi.
Dagowa yayi tareda cewa " koyi nakeso inyi da Rayuwar da kika dora shi akai mommy, Ina ganin yadda yayi Rayuwa batareda Matar shiba, kuma kece kika sashi, ke kika hana yaya na ya sauke hakkin da ya dakko har yabar duniya, mommy kina tunanin Allah bazai tanbayi d'an uwana Wannan hakkin ba? Ta dalilin tsanar da kike yimata har tabar gidan nan bataji dadin rayuwa da mijinta ba why Mommy? Don haka itama Matar son taki tayi biyayya irin nata tagani.
Ibrahim banson rashin kunyar ka haka kaga Ahmed.... "Mommy enough, kidaina kwatance da yaya, ribar me yaci, kinga Amfanin Abinda duk yakeyi? See to avoid you and your wife, am going back to bangkok, zanje in kulada duk wani aiki da yayana yakeyi, bana ra'ayin zama anan, I don't need her idan tagaji tasan hanyar gidan Uban ta.

"Ibrahim, zan hadaka da kawun ku inni bazakaji magana taba. Wucewa kawai yayi, dama so yake kawai ayi fourty days ya yi gaba Amma yanzu baijin zai iya Kara ko kwana daya a garin

kano gwara yatafi ko zai dawo dai dai.
Duk gurmin da Akeyi Fauziya ta shigo tana kallo, yana wucewa a zuciye ta nufo mommy cikin kallon tsana da kece sanadi, tace Wallahi bantaba sanin Abinda kikayi zai shafi farin cikina ba dana taka miki burki, kuma zanje in shirya inbi mijina. Ta buga mugun tsaki, "Fauziya karfa ki manta ni uwar mijin ki ce kike fadamin maganar da kikaga dama. uwar miji uwata ce ko uwar ubana ce? I beg give me a break. Ta yi gaba zuwa dakin shi dake part d'in .

Yana hada kayan shi, tayi sallama yayi wurgi da Abinda ke hannun shi saboda haushin takurar ta, ya juyo cikeda haushi, "can't you learn from Naziya, kintaba ganin tana bin yaya the way you are following me? Please have some shame.
"Oh baby yazaka hanani bin mijina, you are my husband Inada right akan ka, and ka daina hadani da Wannan village and stupid girl..... Wani irin kukan kura yayi a wuyan ta, tareda shake ta ya hada da gini idanun shi kamar na bakin kumurci, "what did you said? Cikin karaji, don't repeat that again if not kin gama numfashi a duniya, I promise you, kin ce hakki ko kinada hakkina? gani ki diba in kinada karfi, hakkin na karfi ne kizo ki kwata, useless, now get lost. Ya saketa tareda hankada ta waje,

Da mugun kuka tafita falon Wanda mommy naji tayi Saurin tarar ta, Fauziya lafiya Me Khaleel din ya miki? karki tabani kuma wallahi sai na fadawa daddy na ke kikaja Wannan aikin da kike taka ma dashi sai kin barshi. Tafita tana kuka, hannu ta dora aka, kunga yaro zaimin salalar tsiya, Allah sarki Ahmed da kana nan kaine kadai mai iya takawa yaron nan birki, Allah ya jikan ka yaron kirki Allah yakai haske kabarin ka.
Ta share kwalla tabi bayan shi,
Lokacin yagama shirya jakar shi, kallon kayan tayi tareda zubamai ido, yanzu Khaleel bangama war warewa a rashin d'an uwanka ba zaka tafi kabarni bayan kasan banda kowa sai ku biyu kacal, yanzu shi yatafi kai kuma zaka tafi kabarni.

Baice mata komai ba yayi hanyar bathroom, fita tayi tana fitar da hawaye, wayar ta ta dakko tafara kiran number wayar kawun nasu, yana dauka tasa mai kuka tareda fadamai komai akan zaman shi da Fauziya, da kuma tafiyar da zaiyi. Yace mata Yana zuwa kawai ya katse kiran. Bayan hour biyu kawun ya iso lokacin yaci Ado cikin manyan kaya Wanda rabon shi dasu tun kafin mutuwar yayan nashi,
Lekowa mai aiki tayi tace Ana kiran shi a falon, ya ce tace yana zuwa, fitowa yayi, yasamu mommy gwanin tausayi gefen kawu akasa yau tunda tana neman taimakon shi. Sallama yayi yagaida shi, zama yayi a kasa kanshi akasa, fuskar shi ba annuri ko kadan, kawu yayi gyaran murya yace "Khaleel tafiya zakayi batareda sani na ba? "Aa kawu yanzu ma gidan naku nake shirin zuwa infada maka.Toh Amma me zakaje yi kabar nauyin da yake wuyan ka anan, nafarko Matar ka, na biyu mahaifiyar ka na uku company, sannan wasiyar d'an uwan ka, ko bazaka cika mai burin shi bane, domin yafadamin tun ranar da zai rasu saboda rashin natsuwa banyi maganar da kowa ba, sai Malam, dago kanshi yayi domin jin wane magana akayi harda malam zai shiga ciki, "Ya bar maka Amanar Auren Naziya, kuma munyi magana da malam tunda zance ne na wasiyya ya Amince sai dai muyi Addu'a ta fita takaba lafiya sai a daura muku Aure da ita.

Wani irin zufa Kebin ta kowane kofa ta jikin shi, yakasa koda motsi baya iya koda daga yatsar hannun shi balle ta kafar shi,
Kukan mommy ne yasa yadawo hayyacin shi , wallahi bazai yuwu ba, yaza ayi yaya ya Aura ya mutu kanin shi ya Aura, kuma dole ne ni sai nayi Rayuwa da Wannan yarinya mai kamar mayya, nidai ban Amince ba gaskiya bada yawuna ba.
Kallon banza kawun yayi mata kafin yace " ni nasan bazaki canja ba balkisu, kuma nasan ilimi yayi miki karanci da kin koma islamiyya, tunda bakisan Ibrahim zai iya Auren Naziya ba, kuma Ina so insani me yarinyar tayi miki, ko ince meye laifin ta? Ni tanada laifi A wurina kana ganin saboda soyayyar ta dana ya hadiyi zuciya ya mutu, banason ta kuma lashemin zuciyar Khaleel din da ya ragemin nidai bada yawuna ba.

"Yawun ki basuda Amfani a wurin mu don haka Khaleel gareka idan ka Amince kafin ka wuce kaje kaga malam Allah ya taimaka ya kuma tsareka, sannan zancen Matar ka Wannan kaidai ba jahili bane kasan hakkin Aure to don haka Kayi kokari Kayi Abinda ya dace ni natafi.
Yafada yana mikewa, tashi yayi jikin shi a sanyaye yabi kawun Saida ya shiga motar shi yadawo gidan, tana nan ta cika tayi tab. Kana jina Ibrahim, wallahi kar kasake inji kadawo min da Wannan yarinya mai farar kafa gida, karka sake ka Amince da Wannan Auren nafada maka.
Wucewa kawai yayi cikin dakin shi, ya datse key tareda zubewa akasa, wasu irin hawaye masu zafin gaske ne suka zubo mai, wainda baisamu yinsu ba tuntuni, Ashe maganar da Ahmed kullum yake fadamai zata kasance gaskiya, Wato akwai Abinda Allah ya boye shiyasa ya cusa mai muguwar soyayyar Naziya wadda bai taba yarda da itaba domin yasan is prohibited,
Yasha wahala yana kuma kan shan wahalar, zai iya rantsuwa da Al'qur ani yafi yayan shi son ta, Wanda baisan ya akayi soyayyar ta ta shiga zuciyar shi ba, how? when? Wani irin kuka yakeyi Am sorry yaya am sorry my brother da nasan zaka tafi kabarmin ita da na roki Allah ya cire min soyayyar ta ya barmin kai a rayuwa, Am sorry for loving your wife more than you brother, am sorry for feeling jealous idan kuna tare baka sani ba yaya, Inada kishin ta sosai yaya I use to cry behind door saboda zafin kishin ta, you are my brother but Ina kishin ganin ku tare, bansan ya akayi soyayyar ta ta shigeni ba, I love her more than the way you love her, I hate myself for that I swear to you, I control my feelings because of you.
You're dead because of hidden destiny, hawayen shi ya share tareda hadiye kukan, "I will make her happy yaya zancika maka burin ka, zanbata farin ciki fiyeda yanda Kayi mafarkin bata, zansata dariya fiyeda yanda take dariya idan kuna tare. Mikewa yayi ya zari key din hadaddiyar motar shi tareda goge fuskar shi da kyau ya fita cikin hanzari a falon da yabar mommy a nan ya same ta tana waya tana fadawa y'an uwan ta bakin labari, Modu ya rantse sai ya cakuda jinin ta da talaka..... . ğŸ–Š

"Comment share the free pages please and Wannan ne last free page ku biya ku karanta cigaban yanda zata kasance, ya za ayi da rayuwar Naziya shin zata Amince, shin zataso Khaleel, ya rayuwar su zata kasance da Fauziya, idan Naziya ta Amince da Auren Khaleel wace wainar mommy zata toya????? Muje zuwa yanzu za afara wasan this is just the beginning, let's

go my fans ğŸ’ƒ, ga masu bukatar biya kofa a bude take chart me up 09011251444

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA
MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA Y'AY'AN GATA
And now AUREN GADO,

Ga masu bukatar Wnn littafi ku turo kudin ku ta Asusun banki na 7304736012 nafisa sani hassan Fcmb ko katin wayar ku ta Wannan number 09011251444, sai kuma y'an ğŸ‡³ğŸ‡ª Niger ku tuntubi Wannan number domin biyan naku, +225 0748153903, littafina Dari biyar ne kacal 500 sai najiku nagode,

2â£1â£&2â£2â£

..... Tuki yakeyi cikin kwarewa tareda bin k'aidar hanya, ya riga yasan hanyar gidan nasu Naziya, tunda yazo sau biyu, har kofar gidan ya isa, lokacin yana mak'il da Almajirai, da Alama Malam na gida, fitowa yayi yana wani irin sheki da haske duk da ya rame saboda mutuwar d'an uwan shi, wani Almajiri ya Kira yace yamai iso wurin Malam yace mai Ibrahim ne kanin Ahmed, ko minti biyu ba ayi ba saiga Malam cikin fararen manyan kaya, tsohon akwai tsafta da kwarjini, yayi saurin dukawa zai gaida shi, a'a Ibrahima tashi shigo daga ciki,
Har tsakar gidan yajashi domin zauren akwai mutane, yanayi yana kallon tsarin wurin Wanda zuciyar shi ke ayyana mai komai, tsakar gidan akwai inuwar bishiya wadda a karkashin ta aka

samai kujera ya zauna Malam ma ya zauna suka gaisa kafin Matar k'irki ta fito, d'an dukar da kanshi yayi ya gaidata ta Amsa tareda yi mai gaisuwa, kafin Malam yace Hauwa Kira min Naziya, kafin nan shukrah ta kawowa bako ko sobo ne mai sanyi. Wani irin lugude yaji zuciyar shi tayi jin ankira sunan ta, ta' aziya Malam yakuma yi mai tareda fatan Samun Rahamar ubangiji, yabishi da nasihohin da duk in zakazo wurin shi sai ya maka su. Shukrah ce ta kawo zobo mai sanyi a tsaftataccen sabon jug cikin na Naziya, ta Ajiye tareda gaida shi tayi gaba, Fitowa naziya tayi cikin katon hijabin ta, kana ganin ta kasan ta rame sosai,
Sallama tayi, ya dago kanshi suka hada ido, Wanda tunda akayi rasuwar daga ita harshi basu hadu ba.
Allah ya gani bata son shan inuwa daya da gayen nan don kawai yaci Albarkacin Ahmed ne batada yadda zatayi dashi, Amma tunda yanzu mai rabawa ta raba shikenan ta huta,
Gaida Malam tayi batada niyyar gaida shi, saida Malam yace ga kanin mijin ki naziya, dama Ina so in samu lokaci muyi magana daku dukan ku, akan wasiyar da mijinki yabari, wani irin faduwa gaban su yayi duka shi tsoron reaction dinta yakeyi ita kuma batasan wace wasiyya bace.
"Ibrahim Alhaji Amadu yazo min da maganar kuma ni bazanyi jayayya da wasiyyar mamaci ba" don haka yanzu magana na wurin ku, Naziya mijinki yabar wasiyya d'an uwan shi ya Aureki, don haka idan kinfita takaba sai adaura muku Aure.
Wani irin kukan tasa tareda zama gaban Malam d'in. Kallon lafiya Malam ke yi mata, shikuwa wani irin tsalle zuciyar shi keyi saboda fargaba, "Malam don Allah karka Yarda nidai bazan koma gidan su ba, ni bazan yi Aure ba ni bana ma son shi kawai abarni haka, ni karatu nakeso inyi don Allah Malam karka hadani dashi.

Tashi kibani wuri Naziya banson shiririta, yaushe kika canja hali haka? tashi kafin ranki ya baci, wucewa tayi da gudu dakin Inna, Malam ya kalle shi, Kayi hakuri kaima bansan naka ra'ayin ba, Amma tunda kaine namiji in har ka Amince Naziya ita ba Matsala bace, kaje Allah ya maka Albarka yajikan d'an uwan ka, Ameen yace kawai zuciyar shi na wani suya, maganar ta ta bata son shi really touch his heart, wani irin zafi yakeji a kirjin shi, cikin dauriya yace Malam Wannan filin nakusa daku yaya Ahmed ya siye shi da sunan zai gina maka dakunan Almajirai batareda sanin kowa ba, bayan rasuwar shi Nagani a rubuce ya gama biyan contract din komai Allah bai nufa ya yi ba, inaso Inturo su, su duba yadda zasu tsara komai zanbar komai kafin intafi, zanje domin shigo da wasu kaya,

"Allahu Akbar Allah ya jikan shi yasa mutuwa hutuce a gareshi" Allah ya Albarkace ku baki daya. Ya Amsa da Amin, ya tashi yana farin cikin zai fara cikawa d'an uwan shi burin shi, duk da yatafi da ciwon maganar Naziya.
Bayan tafiyar shi ya kira Inna kulu da Naziya, ranshi a bace yace "Hauwa bansan cewa zan haifi yaron da zai yi musu dani ba, yau Naziya ke da nake yabonki kike kokarin watsamin kasa a ido, a gaban yaron nan kice bakya son gidan su bakya son shi, a Ina kika koyo Wannan d'abi'a? "Subuhanallahi Naziya me nake shirin ji"? Inna ni dai Don Allah ku yafemin Amma ni bana son komawa gidan nan nayi hakuri batareda nayi wa kowa korafi ba, yanzu idan na koma mutuwa zanyi, wallahi bana sonshi baida hali ba irin Ahmed bane, malam baka san shi ba.
Toh Hauwa tariga ta girma Y'ar taki, ni bazance komai ba tunda ta isa da kanta. Yafada tareda

tashi yabar gidan kawai, a tarihin rayuwar shi itace ya' ta farko data farayi mai musu da gaddama.

"Naziya me kikeso ki yi"? Kin taba ganin ko Y'ar nan malam ya yi magana ta amsa shi bare ke? Wane irin abu ne nake gani ni kulu yau? "Allah Inna bana son shi ya zan iya zama dashi ni dai bazan koma gidan nan ba. Ta tashi tana hawaye tareda shigewa dakin su, kwalawa shukrah kira Inna Tayi, "gani Inna. Kiramin Y'ar nan a waya. Tasan wa take nufi don haka takira Aunty Raliya ta bata, Inna tace "kuzo kuyiwa Y'ar uwar ku magana ta canjo hali, nan tafada mata komai, tace karta damu za tazo tayi mata magana ita da Aisha. Dakin su ta koma tana kuka, tareda kudurin duk Abinda zai faru sai dai yafaru bazata taba Auren Khaleel ba, saboda tun farko jinin su bai hadu da juna ba, tayi hakuri ta zauna da Ahmed saboda tana son shi, Amma bazata taba Y'arda ta zauna da Khaleel ba, wai ma yaza ayi ta yarda da Wannan kwamacalar, bayan agaban shi yaga yanda Ahmed yake nuna mata so lokacin da suka samu sarari, Shigowa shukrah tayi tace "Aunty wai fadan me Inna takeyi yi miki? Kuka kikeyi me yafaru? Rungume shukrah tayi tareda jin wani sabon kuka, "Shukrah bana son shi. "Waye bakyaso Aunty? " Khaleel, I hate him, bana sonshi wallahi bazan zauna dashi ba. "Ni Aunty bansan me kike fada ba.

"Ya za'ayi kisani tunda Auren ya koyo mata taurin kai, Naziya ki rufawa kanki Asiri karki wahalar da kanki a banza idan Malam ya karb'i lamarin nan ba mai canja shi, don haka na hore ki kiyi biyayya ki gama lafiya shine kawai.
Hadiye kukan ta tayi, dif jin fadan Inna, Shukrah ta tashi tabar dakin domin tasan ba hurumin ta bane, zama Inna tayi gefen ta tafara yimata nasiha akan bin duk abinda Malam ya zartar, shiru kawai tayi domin bata saba jayayya da iyayen ta ba, Amma zuciyar ta bata lankwasu ba, Sam bataji zata iya zama da wani kanin mijin ta ba, dama wani ne ba Wannan ba.

Yana tuki yana tunanin kalmomin ta," ni bana son shi. Kalmar datafi kona mai rai, don haka speed ya Kara, saida yagan shi cikin gidan su ya fito a zuciye, ya matsu gari bai Waye ba yagan shi yabar kasar nan, kwabewa yayi tareda watsar da kayan jikin shi ya zube akan kujera zuciyar shi mugun zafi da turiri takeyi, she is the first girl da ta kalli tsabar idon shi tace bata son shi, huci yake fesar wa saboda zafin zuciya.
Har zuwa dare ya kasa bacci shi kadai yasan ciwon zuciyar shi, a kwance yake dagashi sai boxer jikin shi na sheki kadaicin d'an uwan shi kawai idan aka barshi dashi wani Abu, amma yana ganin duk duniya ba wanda zai iya fahimtar halin da yake ciki, how he wish yayan shi na tare dashi, yafi son rayuwar shi fiyeda soyayyar Naziya, wadda ya Amince ta kashe shi akan yarasa d'an uwan shi gwara shi ya mutu, saboda yanzu ma ba Amfana zaiyi ba don ya dade da sanin bata kaunar ganin shi.
Turo kofar da akayi ne yasa yadago kanshi, fauzy ce, ta shigo cikin Sanyin jiki fuskar ta sharkab da hawaye, tana sanye cikin kana nan kayan bacci, kusan duk komai nata a bayyane yake Wanda shi ba abunda ya burgeshi ciki, domin zuciya ma saida natsuwa take samun wani feelings, halin da yake ciki ko tsirara ta shigo gaban shi ba tashi zaiyi ba.
Zubewa tayi kan jikin shi tasa mai kuka mai ban tausayi, "meye illa ta, meye aibuna da ka kasa bani koda sakon zuciyar kace? Khaleel Ina sonka why ni baka sona? nayi hakuri da duk wani

halin ka, yau kusan sati biyu Auren mu ba wani kulawa baka ko zuwa gefen da nake, Khaleel nifa mutum ce Inada jini, ni lafiyayyar mace ce, dole in bukaci mijina please tauye hakkin yayi yawa, sannan me nakeji? Auren Naziya? "That village girl"?.
Tunda take magana jikin shi yayi mugun sanyi, yes she is right ba ruwan Ubangiji da halin da yake ciki, tunda igiyar Auren ta na wuyan shi bai kamata ya watsar da hakkin Allah ba, amma this her last statement mess up things. Wani irin wancakalar da ita yayi kasa tareda mikewa yana nuna ta da yatsa " look that girl, I value her more than you, she is more important to me right now, karki sake inji wani mum munan kalma daga bakin ki akan ta, duk wani Abu da ya shafi d'an uwana yanada muhimmanci A rayuwa ta, ko a mafarki naji kin kuma kiran ta village girl sai na saba miki.

Tashi tayi tareda girgiza kai " lallai Khaleel, tell me, yaushe kafara sonta? This is not About yaya Ahmed ,this is about you, yes saboda naji yanda kukayi da salifa why kaki Amincewa da salifa ka amsa Naziya, why?
Zaburowa yayi ya nufota kamar zai shake ta, "baki Ajiye ni ba so don't question me again, kuma kije kiyi duk tunanin da zakayi I don't care, one last thing, in kinga ban Aure taba sai in bana raye, idan zaki iya zama ki zauna idan bazaki iyaba see your road. Yafada yana nuna mata hanya, juyawa tayi da gudu tafita ya bita da tsaki tareda cewa "useless.

Dakin momy tafada har bacci ya dauke ta Wanda ta dade batasamu tayi irin shiba domin rasuwar Ahmed, yau ma da taimakon maganin hawan Jinin da Aka bata ta samu yadan dauke ta, fadowar datayi tareda buga kofar yasa ta zabura tareda dafe kirji tana jin bugawar zuciyar ta yana karuwa, "kalu innalillahi, ke Fauziya lafiya kika bugamin kofa tareda fadomin daki kamar y'an fashi.
Kuka tasa mata mai karfi, kince zakiyi mai magana gashi yace sai ya Aureta, ni wallahi bazanyi kishi da yar talaka ba kuma Y'ar kauye. "Oh yanzu bazaki iya bari muyi maganar da safe ba? kinga bacci nakeji. "Allah bazaki runtsa ba Indai ni bazan runtsa ba."Toh baki Yarda dani bane Fauziya? nice fa, bazan taba Amince wa a hada min iri da jinin talaka ba, saboda soyayyar da Ahmed ke mata ya fadi ya mutu yabar ni don haka bazan Yarda ta dawo ta karasa min gudan da yarage ba, kina ganin Y'ar nan kinsan ta gaji maita daganin ta mayya ce.
"Ni Ina ganin yana sonta ne fa. "No no no ba wani so, yaushe d'an uwan nashi ya mutu ke baki san soyayyar dake tsakanin shi dashi bane ko Auren ki ya karba saboda sa bakin Ahmed badon niba, a duniya Khaleel zaiyi komai saboda Ahmed Inada Wannan yakinin, don haka kicire zancen Khaleel zaiso yarinyar nan bayan yanada mace kamar ke. "Hmmm ni ai baya sona kema kin sani Khaleel baya son kowacce mace baida lokacin mace, Ina tsoron ranar da zaiso wata irin su basu iya fadawa soyayya ba, ranar za ayi biyu kuwa domin zan iya kashe macen da duk Khaleel yaso, ni nayi dakon soyayyar shi don haka idan har akwai wadda Khaleel zai so to nice.
"Naji zo ki kwanta a nan don girman Allah kibarni in kwanta maganin nan aiki yakeyi ajikina. Da k'yar ta samu ta kwanta sukayi bacci.
Asubar Fari yabar musu kasar su batare da yajira sun tashiba, maid ya fadamawa tafada ma mommy ya tafi, Wanda saida tayi kuka sosai lokacin da yarinyar ta fada mata, wani gefe tana mai kewar Ahmed yaro mai biyayya, "Allah ya jikan ka yaron kirki", zabin ka ne kawai ya

sabawa ra'ayina Amma kai d'a ne nagari Ahmed, Allah yakai haske kabarin ka.
Koda ta nemi wayar shi, lokacin yayi nisa a sararin samaniya, Wanda yatafi da kewar Abu biyu, Wanda yana fatan kafin yadawo yarage tunanin su domin samun zaman lafiyar zuciyar shi.

Gefen Naziya haduwa sukayi washe gari Wanda Aisha tabi bayan Naziya tareda cewa "gaskiya Innan mu Ki cire kara ki fadawa Malam gaskiya kar ya Yarda da had'in nan, domin tasha wuya a gidan nan batareda mun fada muku ba, nidai bana goyon bayan ta Auri wani kanin mijin ta, wane dadi ta tarar a gidan mijin nata da zata koma cikin shi?.
"Toh madallah naji ku kuma nasan inda tasamu zuga, Wato dukan ku kun canja hali banida labari? Malam ya fara fada kafin ya karaso ciki ya zauna, "Hauwa, ki zama sheda, da farko bani nayiwa Naziya zabin mijin ta ba duk da a Musulunce ni keda hakkin zaba mata mijin Aure a matsayin ta na budurwa, banyi hakan ba, can suka hadu dashi tace taji tagani, duk Abinda ta fuskan ta a gidan Aure kaddarar tata rayuwar kenan, kuma yanzu mijin ki ya tafi yabar wasiyya akan d'an uwan shi ya Aureki na fita hakkin ki a matsayi na na mahaifin ki ba neman shawarar ki nakeyi ba, Agaban ido na da na yaron nan ki kace wai bakya son shi, saboda rashin da'a, to ki rubuta ki Ajiye Indai Ina numfashi, daga ranar da kika fita takaba daga ranar zan daura miki Aure da Ibrahim don Allah Naziya kifito ki nunawa duniya ni Malam Abu nayi miki Auren da bakiso, don haka nagama magana. "Kayi hakuri Malam" inji Inna da sai yanzu ta fara magana, don Allah karkayi wani dogon tunani kazartar da duk Abinda yake dai dai, nasan duk hukuncin daka yanke kana da taka hikima. "Malam Kayi hakuri kokarin lallashin ta mukeyi wallahi. Inji Raliya, tashi yayi kawai ya kade babbar rigar shi ya fita, Wanda sai lokacin tasaki d'an karamin kuka tareda toshe bakinta kar Malam ya jita, "Akul Naziya, Aure na sama da shekara talatin idan kikaja min bacin rai saboda boyayyan bakin halin ki bazan yafe miki ba. A'a Inna ya haka? don Allah karkiyi saurin yimata baki. Inji Raliya, ba baki nake mata ba dawo da ita nake cikin hayyacin ta. Rarrafawa tayi da sauri ta rike kafar Inna. "Na tuba Inna wallahi bazaki kuma jin nace wani Abu ba akan maganar nan, ba zan kuma musu ba, ki yafemin don Allah Inna. "Allah yawa Rayuwar ku Albarka baki daya, Aisha kirika hakuri ke babba ce a saman ta in bazaki kwantar mata da hankali ba karki nemi tayar mata dashi.
"Afuwan Inna kuyafe mana. Tashi tayi itama tabarsu a cikin dakin, suna Kara tausar ta. Matsowa Raliya tayi tareda dafa ta tace " ki share hawayen ki, jikina nabani Naziya zakiyi farin ciki fiyeda Auren ki na farko, kinsan me? Girgiza kai kawai tayi badon tana farin ciki ba sai don tana gudun bacin ran iyayen ta, "saboda Khaleel daban yake bazaki gane ba sai nan gaba keda kanki zaki fadamin. Allah kadai yasan Abinda ke ranta amma ita tasan bazata taba son Khaleel ba domin jinin ta da nashi bai hadu ba, zaman ta da Ahmed soyayya ce sanadi Amma shi tasan zama ne bamai dadi ba. Haka suka wuni suka tafi gidajen su, Wanda daga nan ta Kama kanta tareda dukufa Addu'oi akan mijinta.
Wasa wasa aka fara aikin ginin malam Wanda batasan daga Ina Abun ya samo Asali ba, cikin wata guda har angine dakunan Al majirai sunkoma andawo gyaran cikin gidan Wanda aka rushe gefen da suke ciki aka bugawa Inna flat Dan madai daici Da bazai cinye filin tsakar gidan ba sai dakuna biyu a waje, daya na Malam daya nasu Naziya. Aiki ne dayaja kudi Abunka da akwai su gamasu aiki birjik, mamaki takeyi sosai akan Wannan gyaran Wanda saida takasa daurewa ta tanbayi Inna shin Waye yake musu irin Wannan gyaran ne? Tafada mata wasiyyar mijinta ce kanin shi ke isarwa, a ranar saida ta shiga daki tayi kuka sosai.

Tareda yi mai Addu'ar Allah yakai haske kabarin shi, tasan tayi babban rashi a rayuwar ta, a duk lokacinda ta tuna da kudurin shi nason ya huta da ita sai tayi kuka, yaso ya taba kirjin ta kamar me kunya ta hanata, Ina ma ana dawo da hannun agogo baya da ta Bashi dama yayi yanda yaga dama da jikinta kila data rage takaici, wani irin bakin ciki takeji idan ta tuna cewar Khaleel zata Aura domin tasani Malam baya magana biyu.

Cikin wata uku gidan nan yayi tsab bazaka taba gane shiba waje da ciki kowa sai ya yaba a unguwar, Almajirai sun samu gata domin odar katifu irin na yan boarding akayi musu Wanda a wanna dalilin yasa tsangayar take Kara bunkasa. A gefen gidan momy kuwa tun bayan tafiyar khaleel da sati biyu Fauziya ta tattara nata tayi tafiyar ta Tareda cewa "wallahi sai mijin ta yadawo zata dawo bazatayi gadin wata uwar miji ba, Wanda hakan ya taba mommy sosai domin tasa ran ita zata tsaya ta debe mata kewa, wani lokacin ta kanyi kukan rashin Ahmed don dai tana fita aiki ne Amma zaman kadaicin yana mugun tabata, watannin Sam ba masu sauki bane a wurin ta. Gefen Fauziya a kullum suna waya da khaleel yana kiranta tareda fada mata tayi hakuri idan yadawo komai zai dai dai ta, domin yasan cewa akwai hakkin ta a wuyan shi yana kokarin tursasa zuciyar shine kawai gudun hakkin ubangiji, bata taba fadamai cewa bata gidan ba, sai ranarda sukayi waya yafada mata yana hanya cikin satin bayan ya kwashe kyawawan watanni hudu a kasar ta China,
Kawai Mommy ganin ta tayi tana shiga part dinsu lokacin tafito zata tafi aiki, "A'a Fauziya andawo? " eh bakya kaunar indawo din ne to na dawo. "A'a murna nakeyi ai gidan shiru ni kadai, yanzu dai zanje aiki in nadawo mayi magana, ta bita da harara, "Y'ar sa ido kawai mtswew.
Wanda Mommy murna takeyi domin ita zaman Fauziya a gidan ta Kara mata girma yakeyi tareda mutunci a cikin kawayen ta don haka duk yanda zatayi zatayi taga ta rusa maganar Auren Naziya da khaleel, zakuma ta gyaro zaman Fauziya da khaleel Indai ita tahaife shi.....
ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 7:33 AM - Fiddausi Yunus: ğŸŒ»ğŸŒ»AUREN GADOğŸŒ»ğŸŒ»

Matar soja ce

Daga marubuciyar
KUSKURE NA
BARIKI AUREN SOJA

MUK'ADDARI
WANAKE AURE
ZANYI BIYAYYA
Y'AY'AN GATA
And now AUREN GADO,

Ga masu bukatar Wnn littafi ku turo kudin ku ta Asusun banki na 7304736012 nafisa sani hassan Fcmb ko katin wayar ku ta Wannan number 09011251444, sai kuma y'an ğŸ‡³ğŸ‡ª Niger ku tuntubi Wannan number domin biyan naku, +225 0748153903, littafina Dari biyar ne kacal 500 sai najiku nagode,

2â*ƒ*£3â*ƒ*£&2â*ƒ*£4â*ƒ*£

..... A katon filin jirgin yafito yana Takawa daya bayan daya kamar wani prince, sheki yakeyi yana wani irin haske, idanun shi dauke da katon eye glass, baka ko ganin kwayar idanun shi, fuskar shi dif take ba Annuri yakara haiba da cika ido, watannin hudu sunyi matukar taimaka mai wajen warkar da damuwar rashin dan uwan shi kadan, driver ne tare da manager dinsu ya tareshi, gaisawa sukayi ya shiga motar suka zuba mai duk kayan da yazo dasu, suna tafiya yana discussing harkar business din su Wanda an samu cigaba sosai a cikin watannin fiyeda shekarun baya, domin shi mai zafine kuma baida sanyi kamar yayan shi, yana bin diddigin komai ma'aikatan sun san an samu canjin boss ba wasa, kuskure kadan yagani ko yaji tun yana China zaisa ayi firing mutum a aiki.
Kamar daga sama suna zaune dai dai itada mommy suna hira mommy na Kara lallashin ta tareda alkawarin komai zaiyi dai dai idan yadawo tunda yafara sauraran ta. Kawai sukaji sallamar shi sama sama, wani irin zabura sukayi duka tareda sakin baki, suna mai welcome, zama yayi kawai gefen mommy ya gaida ita tareda dan sakin fuska, domin uwa uwace koda kuwa abola take yawo, he missed her domin fushin da yakeyi da ita yasa tunda yaje baya kiranta baya son ko jin muryar ta sai in ita takirashi, he know she is wrong, kuma shima he is wrong, domin ba Wanda yabashi damar watsar da uwar shi, riko Hannun ta yayi tareda sakin murmushi, "mommy am back. I'm glad my son, ya harkokin ina ji a bakin manager komai na tafiya normal. "Yeah Alhamdulillah. Wani irin rawar kafa Fauziya keyi ta matso tareda zama gefen shi tadafa cinyoyin shi dake cikin blue jeans dinshi sabo dal, "Baby wannan irin surprise haka dama kafada, am happy wallahi. Ture hannun ta yayi tareda mikewa yace" OK bari inshiga ciki zanyi wanka in huta, mommy please am hungry. Jikin ta narawa tace bari in hada maka meal din ka just five minute,Ta wuce murna fal cikin ta, tarar shi Fauziya tayi tace "darling muje part din mu mana nan akwai takura ba sakewa".
Mugun kallo ya watsa mata kafin cikin zafin rai yace "uban waye zai takuraki anan, now listing I know exactly what you are doing, ko ki dawo nan ko ki yi ta zama acan ke kadai, saboda bana ra'ayin zuwa wanna gidan if you are ready ga dakin ki can! Ya wuce abun shi.
"Kutumar uba wato dakin da Y'ar kauyen nan ta zauna yakeso ta dawo wallahi bazata dawo nan

ba sai dai duk Abinda zai faru ya faru. Bin bayan shi tayi bayan ta gama dogon tunanin ta, lokacin harya tube ya daura towel, tuni taji wani irin feeling ya taso mata domin khaleel fa namiji ne complete ba algus ya ginu ya keru, wani fesar da zafin bakin ta tayi kafin ta matsa tana karairaya zata rungume shi.
Hannu yadaga mata "please, bana son disturbance, nagaji now get out.
Haba khaleel wane irin daukar Alhaki ne wannan? you're my husband why All this?, ko bankai mace bane, Auren mu wata hudu Amma ace ko hug baka bani damar yiba. "Go and ask mommy idan ta Amince da hakan saiki dawo now out. Yafada yana wucewar shi bathroom. Fita tayi kawai rai abace taci karo da mommy, me yafaru kuma kinfito da bacin rai? "Ba dole ba, yaza'ayi ace wai sai na tanbayi izinin ki zan rungumi miji na? gaskiya kekam a bincike ki kina wa yayan ki asiri ne wane irin biyayya ce suke miki kike cutar dasu, so kikeyi nima inyi rayuwa irin ta Naziya? wallahi ko kina so ko bakyaso sai kinganni da cikin khaleel. "Haba Y'ar lelen mommy zo kiji, ke baki iya siyasa ba keda zaki caba ado ki makalewa mijin ki, ya zakice banason hada iri dake Fauziya, duk soyayyar da nake nuna miki haba ki rika ragamin mana.
"Nidai kiyimai magana yadawo gefen mu Ina jiran shi. "Jeki zanturo shi kin ji. Ko sauraran ta batayi ba ta fice, saida ya dauki kusan minti talatin yana kwance tareda runtse idanun shi a cikin ruwan, shi kadai yasan tunanin zuciyar shi, wani irin murmushi yayi na gefen baki, kafin ya fito ya dauraye jikin shi, ya daura towel ya fito, mommy da ya gani zaune da Abincin shi tana jiran shi yasa yace "oh my mommy am coming tank you, I really miss your cooking.
"Oh son kayi kasa kaya kazo kaci. Kananan kaya yasaka kafin yadawo yazauna, akaron farko yafara bata labarin komai kafin yayi shiru, domin tuno da dan uwan shi da yayi, "I promise, Yaya zanyi duk Abinda kake burin yi kafin nawa. Shiru tayi tareda dafashi, "khaleel, mutuwar Ahmed gibi ne babba a rayuwa ta and all tanks to wannan Y'ar gidan talakawan, look son kaga idan Har na isa dakai kar inji ka yarda da Auren yarinyar nan, idan kana so ka ciremin kewar dan uwan ka kabi Abinda nakeso. kallon ta kawai yayi ya janyo Abincin shi yafara ci, bai kuma cewa komai ba har ya cika cikin shi fal ya kora da juice, "mommy zan kwanta domin nagaji sosai, later zamuyi magana.
Kallon dan rainin wayau tayi mai kafin ta kwashe kwanonin ta tafita, wato duk maganar ta bata bukatar Ansa, saida yaga ta fita yaja numfashi, "am sorry mommy she is my wife now! Auren mu ya dauru tundaga ranar da tafita takaba, don haka soon zata tare agidan nan.
Baccin shi ya shaka bayan ya rufe kofar saboda bai son damuwar Fauziya.
Tana can ta cika tab tana jiran mijin ta ga mommy ko zancen batayi mai ba saboda damuwar Auren Naziya yafi tsaya mata arai. Bai tashi ba sai la'asar yayi sallah ya shirya yafito domin yanada Abunyi, part din yayan shi ya leka yaga ba kayan salifa, wayar shi yaciro tareda kiran manager yabashi umarni, akan ya nemo mai best company na furniture's a kano saboda he want to renovate the house, baya bukatar tsohon Abu a ciki, saida ya gama tsara komai ya fita daga gidan.

Tun fitar ta takaba ta murmure tayi tas da ita ba ruwan ta da komai fitama batayi dama kuma ita bamai yawo bace, tana cikin gida tana taya inna aiki ko tana chat a wtstp domin yana rage mata tunani da kewar Ahmed dinta, a kullum ta kalli yanda baya duniya Amma ya inganta rayuwar su Abin na mugun faranta mata zuciya, hatta da dakin su an saka musu gado da sabuwar katifa,

dama basuda talaucin Abinci domin Malam ba mutum bane da ke zama, nema yakeyi iya karfin shi, a zaune take yanzu a karkashin bushiya itada shukrah suna hira sama sama tana chat, tana cikin adon ta cikin riga da sket na shadda orange sabuwa da Aunty Raliya ta dunka mata na fita takaba, dinkin yayi kyau sosai yayi cib a jikin ta, jikinta ba ko mayafi dankwalinta yadan zame kadan kana hango kwantacciyar sumar ta agaban goshin ta, yanzu Almajirai basa shigowa gidan saboda duk Anfitar dasu waje, suna sakewa sosai, Inna ce ta fito dauke da robar gyada mai bawo ta zauna itama a wurin, "Shukrah sa hannu mu bare gyadan nan da ita zamuyi sanwar dare, waccan inta dauki waya bata ji bata gani. Ajiye wayar tayi tana Dariya, "kai inna ai zan Ajiye tunda ga aiki, Amma inna me yasa bakya son a bare miki gyada a injin sai barar hannu? "Kyuiya ke damun ku yanzu" mu da Ina mukaga wainnan Abubuwan, ko nikan masara sai mu niketa a dutse, Yanzu aiku yan gayune, inkai gyada ta injin a farfashemin rabi yabi bawo. Sallamar da akayi ne yasa suka amsa tareda dagowa, Inna ta saki baki tareda cewa" maraba da mutanen ikko, mai sunan Malam kaine a gari?, dukan su sakin fuskar su sukayi, Shukrah ce tafara cewa " Yaya Sadiq oyoyo kaine? Matashi ne kyakyawa ba laifi ya matso wurin da suke Shukrah ta Bashi wurin zama ya zauna ya gaida Inna tareda gaisawa da Naziya tareda yimata gaiduwar rasuwar mijinta, Sadiq Almajirin Malam ne da yazauna a gidan kusan tun yana yaro yataso hannun Inna kamar d'anta, har makaranta yayi a hannun su yanzu yana business a Lagos kuma Alhamdulillah ya samu Abun rufin Asirin shi, shima don har gida da motar hawa ya mallaka na kanshi, yanada rufin asiri dai dai gwargwado, hira sukeyi tsakanin su domin ya zama dan gida basa mai kallon bare infact matsayin Yaya suke kallon shi, Sallamar da Malam yayi ne tareda kuma khaleel yasa Inna ta tashi saboda kunyar taga khaleel, Wanda Naziya bata lura ma da shi ba, dariya takeyi har dimple dinta na lotsawa, saboda sun saba da Sadiq sosai,, saida ya zo gab dasu ta shaki kamshin turaren shi, dago kanta tayi sukayi two eyes ido cikin ido tuni Annurin fuskar ta ya dauke kamar yanda nashi ya dauke dif, dama ba wani fara'a yakeyi ba, mikewa tayi kawai ta dauki robar gyadar tayi kitchen zama sukayi su uku a wurin Shukrah na gaida su ta wuce itama, fuskar shi tamke suka gaisa da Sadiq, Malam yafada mai koshi waye a wurin shi, "Ibrahim Mai suna na kamar su Naziya yake a wurina, yana kasuwanci a ikko yau ya shigo. "Sadiq wannam shine mijin Naziya na yanzu". Saurin kallon Khaleel yayi domin yana ganin shi yasan wani ne kuma ya tara ko kuma dan wani, wani iri yaji yace "Malam andaura ne? "Eh kamar yanda nafada maka rasuwar mijinta wannan dan uwan shine. Shiru yayi kawai shi yasan Abinda ke ranshi, fuskar khaleel a tamke yace "Malam zan iya ganin ta? "Bismillah ai gidanku ne ga dakin ta can kuje kuyi magana. Yafada tareda juyawa suna magana da Sadiq, "yanzu dai baka komawa sai ka kawomin Matar Auren ka Sadiq tunda dai kasamu rufin Asiri Bana son zaman magidanci ba iyali. "Insha Allahu Malam" kafin intafi zan nema.

Wucewa khaleel yayi hannun shi sanye cikin pocket din manyan kayan nashi, shadda ce fara Y'ar gaske, tayi matukar haska shi, dama ga iya wanka,

Zaune take tana cewa Shukrah" shi kuma wannan daga Ina? kalla yanda ya fadowa mutane cikin gida. "Kai Aunty bakya ganin tare yakeda Malam kuma karki manta kin kusa zama Matar shi tunda ki ka ganshi yanzu, ni Ina tunanin ma kamar baya garine tun zuwan dayayi bai kuma zuwa ba sai yau. "I don't care da yazo da kar yazo kinsan da Allah zai taimakeni Malam ya fasa zancen Auren nan da nafi kowa farin ciki. "You are too late. Yafada bayan ya daga labulen dakin nasu ya shigo, saurin tashi Shukrah tayi, ya kalleta" sister excuse us please. Yafada yana

murmushi kadan, tace "tom" da sauri ta fice, karasa shigowa yayi, taji kamar ta zura da gudu, juyawa tayi tareda daukar katon hijabin ta ta zura. "Hmmm. Kallon dakin yayi dakyau yaganshi fes yana kamshin turaren wuta ba wani tarkace daga gadon su sai Karamar waldrp da akwatunan su sai mirror dake dauke da kayan kwalliyar su.
Matsawa yayi gaban mirror batareda yace mata komai ba, ya dauki turare daya ya kalla ya Ajiye. Kallo take binshi dashi kawai domin rainin wayan shi yawa ne dashi, kuma so take taji ya karasa maganar daya faro tun farkon shigowar shi. Ganin baida niyyar cewa komai gashi haibar shi duk ta cika mata daki, duk taji she is not comfortable at all. "Malam ka taimaka ka fadawa Malam baka ra'ayin Aure na, domin ni bana ra'ayin Aure yanzu, musamman dakai. "Sai da wancan kazamin ko da kike wa dariya kamar wawuya right? Yafada yana juyowa tareda matsowa kusa da ita. "Nidai koma meye ni bazan Aureka ba". Hmm Ashe igiyar Auren a hannun ki zata zauna idan an daura? dago kanta tayi tareda kallon cikin idanun shi domin fadamai magana, "wane irin cin Amana ne zaisa ka Amince da Auren Matar yayan ka, kuma bayan kasan ba kaunar juna mukeyi ba? That's your opinion not mine! and listing, Aure an daura shi tun daga ranar da kika fita takaba, don haka ko kiso ko kar kiso you're under me, kina karkashin inuwar Aure na, sannan kina maganar cin Amana ko what ever, ai kece mai cin Amana har kin manta da Yaya na kin fara sakewa wani banza fuska kina dariya, listing to me, am not like my brother ni ba zakiyi min Abinda kikaga dama ba, wannan rayuwar da kikayi a baya ki gogeta this is Ibrahim khaleel, you better change your way, be a responsible house wife, if not bazakiji dadi naba.
Wani irin zafi zuciyar ta ke mata yanzu ji take da tana da karfi shakeshi zatayi har sai ya daina numfashi domin irin maganar dayake fada mata a sulale.
"Malam idan kana tunanin Naziyar daka sani ce a baya you are mistaken, inada nawa tsatstsauran ra'ayin idan naso, don haka karkayi mafarkin zanyi irin rayuwar da nayi da Ahmed a gidan ku, naso Ahmed shiyasa na jure wulakanci kuma kai kasani ba zaman dadi a rayuwar da baso sai tsana a cikin ta. "Hmm that means you hate me? "We hate each other. Tafada tana murguda baki, "ni bazanyi zaman Aure dakai ba. "OK naji kuma duk na haddace and lokaci ne zai fada mana komai, Malam ya tanbayeni yaushe zandauke ki da nace end of the month, yanzu nafasa so nake kitare a gidana domin inga ra'ayin waye zaiyi tasiri. "Nidai bazanje ba don Allah ni ka sakeni kafada musu kafasa. Har ya juya zaifita kalmar saki tasa ya juyo, tareda Kara tamke fuska, " in your dream. "Ni bazan zauna da wata kishiya ba ai Kanada mata, ni kuma bazan zauna da namiji mai mata ba, Tafada ne kawai badon Abinda ke ranta kenan ba sai don ta rasa wane irin excuse zata kawo mai.
"get ready domin zama zakiyi da kishiyoyi ba kishiya ba, and saboda careless baki kosan bana gari ba, anyway am back tsarabar ki sai kin tare, bye. Ya fice cikin hanzari, tabishi da kallon mamaki, duk zafin nan da take ganin yanada shi bai nuna mata ba, wai da gaske an daura mata Aure dashi? Ya bata sani ba? Shukrah ce ta shigo tace "Aunty da gaske fa Malam ya daura muku Aure da khaleel ya sadiq kefada min yanzu. Zama tayi kawai tareda dafe kanta, ta Ina zata fara zama dashi, wace irin rayuwa zasuyi, yazata zauna da Ahmed yanzu shima ta zauna dashi?
"Aunty nidai karki sa tunani kiyi Addu'a Allah yasa kiji dadin Auren nan fiyeda na farko. "Hmm Shukrah, bakisan halin shi bane, ni bazan taba sonshiba. "Aunty kin sani fa bakyau kaki mutum da yawa in zaki so mutum kiso shi don Allah haka in zaki k'i shi ki k'i shi don Allah.

Bansan wane irin zama kukayi da Yaya Ahmed ba Amma ki kyautata zatonki kisawa zuciyar ki hakuri zakiyi farin ciki. Shiru tayi tareda mikewa ta fito domin tana bukatar Amsa wurin inna.. Zama tayi a kitchen din tareda daukar Alayyaho tana gyarawa "Inna yaushe aka daura min Aure ban sani ba? Dago kai Inna tayi tace "kije ki tanbayi Malam ai kin San baya magana biyu, don haka karki manta da furucina, kuma kar inji musu ko jayayya akan zancen nan, kinji nafada miki kiyi ki yanka kitashi ki tuka tuwon nan ya dahu. Ta fada tana fita tabarta, wasu hawaye ta share masu zafi tareda ci gaba da aikinta, tayi Alkawari koma meye zai faru atsakaninta da shi ne zaiyi daya sanin Amince wa Auren ta.

wurin, budewa tayi taga ya shirya mata sababbin kaya makil tundaga dogayen riguna riga da sket su jeans passion na mata har zuwa kan kayan bacci masu matukar kyau da daukar hankali, wani iri taji, wato tana bacci yayi duk wannan Abubuwan bata sani ba. Wani irin tausayin shi taji domin tasan duk Abinda yakeyi yanayi ne domin yafaran tamata, wani nazari tayi na d'an lokaci akan Rayuwar shi, yanada murdadden hali shiyasa baida tsoro halin shi daban dana Ahmed shiyasa yazama jarumi tsayayye.
Wata riga ta zabo guntuwa iya guiwa ja rigar tayi mata kyau sosai daga ita sai d'an pant mai irin v shape din nan, gaban rigar nada kokon brah da yakamata dam, rigar ta haskata sosai ta gyara sumar ta tareda feshe jikinta da kamshi ta kalli mirror tagan y'an da ta fito kamar ka saceta ka gudu. Motsin da taji ne yasa tayi saurin juyowa, ya tsaya a bakin kofar ya nade hannu yana kare mata kallo tundaga kasa har sama, bazai iya magana ba sai ido, ganin yanda yake kallon ta tasan ya yaba don haka cikeda yanga domin daukar hankalin shi ta matso kusa dashi tace " naga kaya nagode sunyi sosai Allah ya Kara budi da Arziki, wato Ina bacci kafita har kayi wannan aikin bansani ba? Lallai nayi bacci sosai, muje muyi kallon KO?
Kur ya mata ko kiftawa bayayi, " she hardly talk, don haka duk lokacin da take magana Abin yake matukar dauke mai hankali, domin muryar ta shape din lips dinta, yanda take magana, yana tafiya da zuciyar shi baki daya, bare yau ga wanna shigar data mugun rikita shi, fisgota yayi cikin sauri zuwa kirjin shi domin yasamu saukin Al amarin, muryar shi a sarke yace " ba wani kallo bayan kin cikamin ciki da Abinci kuma yanzu kinzo kin rudani what you expect from me now?
Wani irin daukar Amare yayi mata tareda switching light yana cewa " let watch each other babe..... Suka shige blanket domin farantawa juna rai tareda manta duk wata damuwa da suka baro a 9ja.

Sati biyu suka kwashe suna murza soyayyar su, ta murje tayi bulbul da ita, kullum cikin kwaso mata kayan gayu yake , a cikin garin kuwa ba inda bai zagaya da ita ba, wasa wasa itama tafara cin cimar shi ta mutanen sinawa, har tanaso ta fishi zakewa, yana matukar mamakin tama yanzu, gashi duk matsin da yake ganin yana yimata bata nuna gajiya warta, sunyi matukar shakuwa, soyayyar su suke sha sosai, koda yaushe suna like da juna, kusan kullum sai tayi waya dasu Aunty Raliya harma dasu malam domin ya d'an karo mata wata sabuwar wayar ta yayi, gashi d'an zaman nan yana ta koya mata tuki idan sun d'an fita, ko Ina suka wuce kallon su akeyi, shikuwa haka zai kwakume abarshi gam yace " baby da zaki Y'ar da da kin rika zama a gida ko ki saka nikab kafin jini na ya hau ko mu daina fita.
Dariya kawai takeyi tace ka cika kishi Zaauji. Sunan dake matukar faranta mai zuciyar shi. Yau basuje ko Ina ba kwance take tana cin roasted lobster taji yaji, yanzu tafishi sanin dadin sea food, daga ita sai wani arnen guntun wando passion na mata da shimin shi data kamata dam, tazama Y'ar gari don baya kaunar ganin ta cikin manyan kaya, kamar baby doll, ya shigo cikin kanan kaya ya murje yayi kyau sosai yana tafe yana waya da manager dinshi na Nigeria, " kaje gidan ka dubamin lafiyar Momy na nakira wayar ta bata shiga. Yafada cikeda damuwa domin haka kawai yaji yana son yaji muryar ta domin yasan a duniya Momy nason ya'yan ta gashi ba Ahmed shima ya mata yaji, kuma yasan no matter what dole ya sauke hakkin uwar nan, kallon shi takeyi kamar ta lashe shi takeji, saboda kyau da kuma cikar haiba ga iya

soyayya ta kowanne fanni don haka yayi nasarar sace zuciyar ta baki daya,
Kashe wayar yayi tareda rike kugu yana kallon Abincin da takeci, tareda kallon y'an da take kallon shi kamar mayya, matsawa yayi ya d'an bata fuskar shi, " baby! Wannan pepper din will affect your health is too much, koni banacin yajin su saboda is too hurt amma look at the way you are eating this please. Yafada yana zama kusa da ita tareda dafa kafadar ta, " uhm ni dai inajin dadin shi ne inba yaji baya mun dadi sosai karka hana ni don Allah.
Fuskar ta ya kalla data marai raice saboda shagwaba yace, " is OK but idan nayi Ajiya anan no more pepper OK!yafada yana shafa cikin ta dake dame cikin shimi tareda zubawa welcome dinshi ido,
Kallon shi tayi cikeda tuhuma " Ajiya kuma?
" yes now, my little prince or princess, oh god baby am earger when please zaki bani baby?
Zaro ido biyu tayi " ciki? "Yes ciki baby. Yafada yana kallon kwayar idanun ta da yanda ta budesu cikeda tsoro,
"Gaskiya akwai wahala ban shirya ba. Tafada tana tura baki. Dariya yayi ya dora lips dinshi a saman d'an mutsilin bakinta ya tsotsa kadan tareda saurin cirewa " oh my god baby this kind pepper. Yana hura baki saboda zafi, tayi dariya tareda tashi ta haye cinyar shi ta mayarda bakinta tana. " ai sai ka karasa min bayan yafara dadi zaka cire. Ta hade bakin su tana lashe each and every corner na bakinshi domin jinshi takeyi kamar sweet saboda test, tuni tasa yayi lakwas tareda sake mata ragamar bakin da jikin shi ta dora hannun ta daya akan kirjin shi tana cusawa ta cikin rigar shi domin tayi wasa da nippy dinshi da suka zamar mata toy,
Hannun ta ya rike tareda d'an cire bakinshi idanun shi na wani irin shigewa yace " baby if you touch me that way am going to strip you right here.
Wani irin kallo killer smile ta sakar mai tareda kashe mai ido kamar yanda yake mata " am ready for th...., bakinta ya cafka ya cirata sama cak sukayi master bedroom..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/20/21, 5:42 PM - Buhainat: 5â*ƒ*£5â*ƒ*£&5â*ƒ*£6â*ƒ*£

..... Shafa mata mai yakeyi bayan komai ya lafa har sun sheko wanka tana lafe a jikin shi kamar wata jaririya, sai jujjuyawa takeyi a jikin shi, "hay" kinga banason Ina matsa miki Amma kina kureni fa baby, kinfasan inada lafiya, zan iya Kwana Ina baki aiki but ina jin tausayin jikin nan kar in jawa kaina jinya kin ga bazan iya hakurin Kwana daya ko wuni batareda na yi aiki ba, kinga kin sabamin zaki bani breakfast lunch and dinner every day, shiyasa nake lallabawa. Idan ina period fa ya zakayi? tafada tareda kallon shi. Tureta yayi fuskar shi a hade, that is my rival bazai zoba saboda yasan ma bazan iya hakuri ba. "Dariya tayi tareda cewa " zakayi dole gashi sai nayi one week. Hararar ta yayi " sai yazo ingani look karki sa jini na yahau tun yanzu ma, wait ba every month akeyi ba? "Yes yanzu satin mu na uku anan da sauran time. "Aa nifa ya

kusa zuwa yamayi latttin zuwa koda naje gidan Aunty banyi ba.... " oh stop this story please ya mike tana mai dariya ya kwabe towel din jikin shi tareda juyowa ya kalle ta, "yazakiyi da ita da kike wannan maganar sati daya, bayan koda yaushe tana mike bata taba kwanciya because tana ganin ki.... Hannu ta daga sama tana dariyar tsokana tace " baruwana bani bace kaga masu laifin nan. Tafada tana janye towel din jikinta a hankali ta saman, suka yi mai hy. Saida ya kusa zubewa yaja numfashi tareda hadiye miyau masu kauri, " you see. Fuskar shi kamar yayi kuka, " kinja sai na Kara wallahi haba don Allah. Ya nufota a sukwane yana wurgar da towel din hannun shi, tayi tumbling tana kyalkyale mai dariyar tsokana domin tasan tagama kunno shi, Wasan tsere suka farayi a cikin dakin tana zille mai, Saida ya gaji batareda tabari ya kamata ba ya zauna a sofa cikin wayau yace "Ahhhhh cikina zan mutu.....
Wani irin tsalle tayi tareda direwa kanshi saboda tsorata tana "me ya sameka zauji? Fisgota yayi yasa Dari ya, " nakamaki. Ya cafki Abin da ta rikitashi dasu yana murzata domin debe takaici, koda zai making love da ita sau dubu baya taba gajiya da ita don haka ko yanzu tuni ya nemi kwanciyar hankalin shi a jikinta.
Wanda taji wuya sosai a hannun shi, Saida ya tausaya mata, bayan sun natsa tasa mai kuka " nidai karka kuma yimin irin haka Allah zangudu Nigeria inbarka anan.
Lafewa yayi a jikin ta yana maida numfashi, "am sorry baby kece ai, kuma ai duk inda zakije saina biki, I can't do without you. Bayan kece kika nuna min hanyar datafi kowace dadi, baby Aure da Wanda kakeso akwai dadi, nasani idan zan zauna da wata mace bazan taba jin dadin da nakeji yanzu ba. Ya tashi tareda d'an matsawa zai sauka yace " Umm tunda inada wadda nakeso zanyi manage in hada da Salifa inji ya abun dayane ko da banbanci, don haka mukoma Nigeria din ko? Tashi tayi tareda sa mai kuka tana jifar shi da filo da duk abinda yazo hannun ta, dariya yasa yana cewa " Subuhanallah baby kina so ki kone ne kike dukan mijinki?
Biyoshi tayi tareda murde mai fatar gefen ciki " yanka ka ma zanyi da ita idan naga ka kalleta.
"Auchh baby this is wickedness mana, kaina bisa wuya wane ni inyiwa Naziya kishiya. Yafada ta sakeshi ya ruga yana cewa "bayan wadda kikeda ita fauziya ma zata dawo ai. Yafada bathroom ya kulle kofar don yasan sauran. Kishin shi da take nunawa kiri kiri na bala'in burgeshi, zai iya cewa shine first man da zaiso yaga ta daki wata mace ko tayi fada akan kishin shi don haka yana jin dadin tsokanar ta da zancen kishiya.

Nigeria

Tsawon satikan da suka wuce bamasu dadi bane a wurin Mommy, domin zan iya cewa ta hadu da kadarin ta, Salifa da mahaifiyar ta sun mayarda gidan ta d'an dalin y'an iska, tanaji tana gani sun maida ita Y'ar kallo, gashi sun toshe duk wata hanya da sukasan zata samu taimako, sun kori duk ma aikatan gidan sun kawo nasu har mai gadi wani bamaguje suka kawo mara imani tareda bashi umarnin kar Wanda ya bari ya shigo musu gida Saida Y'ar dar su, kab y'an uwanta sama sun dauke kafa sai zarah, ga ta ita kuma tabi mijinta south Africa, hatta da motocin ta duk sun kwashe sun hanata fita saboda sun tsorata ta ta hanyar nuna mata kwalba daukeda zuciyar khaleel, "kinga wannan, duk ranar da kika tsallake dokar mu sai mun fasata kirasa shi baki daya domin muna fasata kwanan shi ya kare. Shiyasa batada zabi sai zubawa sarautar Allah ido, tariga tagama nadama a Rayuwar ta, meye laifin Naziya? Yarinyar nan dai dai da kallon banza bata iya ramawa, ta zageta, ta hantareta, ko sau daya bata daga kai ta kalleta domin taji haushi

ba,
Kuka tasa data tuna yan da ta takura ta lokacin Ahmed, da irin katangar da tasa musu atsakani, da yake Ahmed yarone mai biyayya har yabar duniya bai ketara dokarta ba domin ta sheda.
Wayyo Allah ni nayiwa kaina, ni naja na rasa dana, ni na hana kabar koda kwanka ne a duniya da zai ragemun radadin rashin ka d'an Albarka, nasan da kaine bazaka taba gajiya da mahaifiyar ka ba d'an Albarka, Ahmed kagama da duniyar nan lafiya Allah ya baka sakamako mai kyau a kiyama ka yafemin d'an Albarka.
"Ibrahim nagode daka sa na gano kuskure na, nagode daka tsaya da kafafun ka, da na kuma tafka wani kuskure Allah ya tsare min kai. Shigowar su ne kamar wasu karuwai cikin sashin ta yasa tayi saurin goge hawayen ta, Salifa ce da momyn da wasu kawayen nata irinta, suka zube suna mata kallon rainin wayau, "kinga balkisu dafa mana Abinci muci yunwa mukeji ga kuma baki sunzo masu aikin nan duk basu iya girki mai test ba. Tafada tana mikewa "ni bari inshiga daga cikin dakin inkwanta kafin ki kammala. Kallon kawar tata tayi "Yanzu Hajiya sharifa abun yakai can ki kwaso min karuwa..... Wani irin kwashe ta Salifa tayi da kafafun ta, " kiga karuwa a zuri'ar d'anki kinji. Kara tasa kugunta ya Amsa saboda girma ga jiki, momyn salifa tace "Ashsha uwar miji cefa so kike ki kone an salee na?
"Sai na fara konata kafin ni inkone idan bakinta bazai mutuba, kuma ki wuce ki dafa min Abinci ko in karasa ki wallahi in binne ba Wanda zai bincike ki.
Dariya kawayen sukasa harda tafawa, ta mike da kyar taja kafa zuwa kitchen, tana share hawaye ta sai rariya da kudinta. Haka ta baje ta zuba musu girki badon Allah ba, kuka kuwa ai yazama mata sana'a, tanayi tana hakkin ki ne Naziya.
Fitowa tayi domin ta shirya musu Abinci tasame su hade a kasan carpet suna romancing juna kowace da Y'ar uwarta salifa kuwa ko rigarta ta cire tana shan yaji dayar na sha mata nono a tsakiyar falon Momy, tray din dake hannun ta ta saki saboda firgita da tsoro. Yau taga Rayuwa, Innalillahi wa inna ilaihirraji'un. Tayi taslima da karfi, Wanda karar try bai dawo dasu hayyacin suba amma salatin mommy yasa suka juyo, ko a jikin su salifa ta buga mata tsawa " meye kamar baki taba ganin romance ko shan nono ba bayan kema kinyi da tsohon mijin ki, oh come on ki zo ki bamu Abinci yunwa muke ji. "Babe bari mu koshi mu koma can part din nan akwai sa idawa. Ko momy ta fito sai tayi tofin tsiya kafin tayi shiru.
Duk inda tashin hankali yake yau mommy ta gama ganin shi da jin shi, subuhanallah me ta yayubo a rayuwar ta?
Jikinta na rawa ta tattara su plate din ta koma ta kwaso wasu ta shieya musu komai, wani irin zazzabin tashin hankali ke kamata, takasa koda magana. Tana gama shirya musu Abinci ta koma dakin Ahmed domin dakin ta kawarta ta shiga,
Kafin kace me jinin ta ya mugun hayewa.
Ba waya ba yanda zata iya kiran likitan ta.
Domin har wayar ta sun dauke tana cikin tuminin takabar salifa wai.
Ciwo ya rufeta ba mai kula da ita. Haka take cikin wahala har safe, Wanda su suna cin Abincin su suka bar mata gidan zuwa nasu domin karasa masha'ar su,

Kwana biyu tayi cikin mugun Yanayin dakyar take iya tashi tasha koda ruwa tafita hayyacin ta sosai Wanda a ranar khaleel ya tura manager Wanda yana zuwa yaci karo da sabon mai gadi

da ya hanashi shiga gidan, wai Hajiya tasa dokar kar Wanda ya shigo Saida izinin ta,
Wanda dai dai lokacin da kawayen nata suka fito zata rakasu kanta ko d'an kwali tana sanye da wasu matsiyatan kaya na rashin tarbiya mai gadin ya ruga ya wangale musu gate suka fita, haka manager ya saki baki da ido yana kallon salon iskanci, har zata juya ta koma ta gan shi ya zuba mata ido, kare mai kallo tayi, ta yaba gayen very young and handsome ba laifi shima.
Matsowa tayi tana karairaya " hy handsome me kake nema?
Kallon banza ya watsa mata yace Hajiya nake neman Oga khaleel ya ce inzo induba ta. Yafada kai tsaye, " kai waye? " manager dinshi, zan iya shigowa? Hadiye miyau tayi saboda jin sunan khaleel tace " yeah ofcos shigo.
Shigowa yayi kawai yana kallon gidan duk ya fita hayyacin shi domin ba wasu masu aikin kirki suka kawo ba,

Part din Hajiya ya shiga Wanda a nan ya sameta ta rarrafo da bin bango da kyar tafito domin muguwar yunwa takeji duk da tana cikin ciwo.
Yayi matukar firgita ganin yanda ta fada cikin sati biyu da bai ganta ba, tana ganin shi taji wani irin sanyi da farin ciki don haka ta zaburo, Wanda tuni ta zube Tim a kasa tasa Kara.
"Subuhanallahi Hajiya. Ya nufota da gudu domin ya taimaka mata Wanda yana matsawa yaga ta sume.
Cikin gaggawa ya Kira Asibitin da yasan suke zuwa yace likitan yazo domin bazai iya dagata ba Abunka da ba kadan ba.

Yadai taimaka ya jata saman kujera Saida likita yazo suka kaita dakinta da taimakon nurses da aka zo dasu, Abunka da kudi tuni aka fara bata kulawa cikin gaggawa, sun dade akanta kafin likitan ya fito yasamu manager, ya zare glass din idanun shi, " Ina me gidanka yake yakamata ya fita da ita kawai kai tsaye idan yana son ta samu kulawa domin da Alamun tasamu mutuwar barin jiki sakamakon hawan da jinin ta yayi sosai.
Hankalin shi ya tashi domin bai san ta Ina ma zai fara wannan fadawa khaleel ba halin da ake ciki,
Don haka ya Kira kawun su ya fadamai komai yayi salati yace gashi nan zuwa yanzu.
Saida ya dauki uwar gidan shi kafin ya tafi shima,
Halin da suka sameta a ciki ya mugun daga musu hankali, cikin gaggawa kawu modu ya ce a mayarda ita Asibiti zaifi kafin a Fita da ita. Fita yayi yana neman wayar khaleel, Wanda yayi dai dai da fitowar Hajiya shaeefa da salifa domin ganin meke faruwa a gefen mommy da manager yazo, basu taba zaton khaleel zai waiwayo taba sai sukaci karo da kawu modu yana saka waya a kunne, kallon shi sukayi a tsorace domin basuda gaskiya, aiki ya lalace bayan su sunyi farraku a tsakanin ta da duk wani Wanda zai taimake ta, how yanzu ba aje ko Ina ba ga modu a gidan... Murya kasa kasa salifa tace " mommy meye nake gani me Alhaji yazo yi nan? Aikin ya karye ne? Mun shiga uku. " ke don Allah yimin shiru wa ya isa ya karya aikin boka ai ko ita ban barta haka ba bare khaleel bari kigani bazai zoba ya Riga ya tafi shikuma wannan me ruwan mu dashi.
Ajiyar zuciya tayi, "Hmm har na ji tsoro domin nafara jin kamshin dollar's din da zan mallaka.
Fitowar da akayi da ita ne yasa suka bisu da kallo , ba Wanda ya koma kansu har sukabar gidan da ita,

Juyawa tayi cikin gidan ta momyn ta bita, sai zagaye takeyi, " kingani Ashe batada lafiya ne wallahi khaleel zai zo mommy ni tsoro nakeji. " relax baby me zai faru idan yazo? Bare bazai zoba wannan nadewar da kikaga tayi bazata kuma mikewa ba bakin ta bazai taba budewa ba bare tafada mai me yafaru, don haka Ina zuwa bani jakata in fita yanzu.
Itadai tafara tsorata domin khaleel ba namijin da za ayi wa iskanci a kwashe lafiya bane.
Saida suka bata special room a Asibiti kafin kawun ya Kira manager yace bani number da yake kiranka da ita.

Lokacin suna zaune a falon su suna kallon season film na Philippines tana lafe a jikin shi kamar mage shikuma hannun shi na cikin wuyan shimin jikin ta, yaga kiran manager dama jira yakeyi, saurin tashi yayi ya gyara zama tareda ciro hannun shi cikin rigarta, yayi cutting call din ya kira shi, ya akayi ne? Lafiya kalau ga Alhaji. Ya bashi wayar, gaisawa sukayi kafin yace " khaleel kazo fa domin Hajiya jinin ta ya hau yanzu haka tana Asibiti anyi admitting dinta, jikin yayi tsauri wannan karon kayi kokarin dawowa ko a turota can.
"Innalillahi wa inna ilaihirraji'un, Ina zuwa kawu insha Allahu. Ya kashe wayar hankalin shi tashe, ya dafe kai, jin yake bai kyauta ba Sam na barinta da yayi, dafashi tayi " me ya faru ne? Dago idanun shi yayi, " we're going back to Nigeria mommy ba lafiya tana hospital. Yafada cikeda damuwa, "Subuhanallah, Allah ya bata lafiya, bari in shirya mana kayan mu tom. Tafada tana mikewa, ya riketa, ta tsaya, " ki zauna inje indawo mana." no ni dai zan je kuma kaga bamusan Yanayin jikinta ba gwara mutafi gaba daya, koda zamu dawo tareda ita zamu dawo.
Rungume ta yayi " bakya tsoron me zatayi? " me zatayi? Uwace fa ta isa ne kuma kome takeyi tana yi ne saboda tana son mu don haka muje mu fara shiri. Kara damke ta yayi yana mai kisin din wuyan ta, har Saida taji tsigar jikin ta na tashi tayi saurin janyewa " karka hanamu shiryawa Malam let's go. Tafada tana dariya tareda ruko shi tana janshi yabita yana murmushin karfin hali, daurewa yakeyi karta ga tashin hankalin shi, amma a dame yake.
Duba time yayi yaga karfe hudu na yamma a kasar yace let me check in akwai available plight mu tafi yau kawai.
Yafada yana dubawa a wayar shi.
Tausayi yabata sosai domin duk kokarin shi na ganin ya daure abun yaki yuwuwa domin damuwar a bayyane take a fili.

Ita ta shirya musu kayan da zasu bukata,
Kafin ya shigo cikin sauri " let get ready akwai jirgi mai sauka Abuja. Yafada yana shigewa bathroom. Tashi tayi itama ta bishi har yafara wanka ta tsaya daga nesa tareda zuba mai ido cikin hanzari yake Abinda yakeyi, domin duk hankalin shi ya koma gida. Hmm khaleel ne zata biyoshi bathroom ya share? Lallai a dame yake, don haka bata matsa ba Saida ya gama ya matsota " quickly baby. Ya fita, tayi Ajiyar zuciya ta fara itama.
Ten minutes ta shirya domin ta lura a hanzarce yake, mai aikin shi da yabawa hutu ya Kira yace tadawo kan aikin ta na kulada gidan zai koma 9ja.
Sai zuwa tsakiyar dare jirgin su ya daga,
Like you know is a very long journey, don haka ko yanzu Saida suka Kwana a hanya da sassafe jirgin su ya sauke su a filin jirgin na babban birnin tarayya. Tayi matukar gajiya, fiyema da tafiyar su domin jikin ta mugun kasala takeji da batasan Ina ta samo asali ba. Domin ita batada ganda

ko kadan,
Cikin doguwar Riga take maroon tayi matukar murjewa tareda Kara kyau, kafarta cikin low pass baki mai kyau sai Y'ar Karamar Jakarta data rataya,
All eyes on her, gayu sai baza ido sukeyi sunga mai zafi, ya ankare don haka tuni ya matso tareda rungume kayan shi a kafadar shi saboda kuraye,
Sai da tayi dariya domin ta gano shi yace "what? "Bakomai. "Hmm I don't know why kikayi irin wannan kwalliyar?
Bafa kwalliya a fuska ta. Yes yakamata kisaka katon hijab kinga nan ba can bane sunayin kamar su dauke min ke bazan iya ba zaki dawo da saka hijab malama,
OK malam, Tafada tana jin dadi tareda dariya, plight ya Kuma sama musu zuwa kano, Wanda ba Wanda ya fadawa ya shigo 9ja, har Saida suka sauka a kano ya Kira manager yace ya sa akawo musu mota suna Aminu kano airport.
Jikin shi na rawa yace gashi nan zuwa, da kanshi ya zo tarbar su.

Sun d'an jirashi a reception kafin ya iso,
Ya musu barka da Zuwa kafin ya dauki kayan su ya zuba a motar, suna tafe yana tanbayar shi jikin Mommy, yace tana Asibiti har yanzu su wuce ne kai tsaye? " no bari muyi dropping madam dina a gida first sai mutafi. " A'a mu wuce kawai ban gajiba nima inaso in ganta.
D'an hararar ta yayi kadan, yace toh su tafi. Tanbayar shi tayi da ido what? Ya share. Saida suka isa hospital din ya fito itama zata fito yace kidaina magana a gaban wani ke bakisan yanda muryar ki take ba ko? Oh shine matsalar? Sorry Zauji. Don't repeat that. cikin bada doka ya fada. Suka jero kamar taurari,

Adakin mommy ce kawai kwance sanye da na urorin dake taimaka wa jikinta, su kawu modu da uwar gidan shi suna zaune a waje domin dokar Asibitin. Suka iso, sunyi matukar mamakin ganin su haka da sauri, Dama ka taso Ibrahim? eh kawu ya mai jikin? Toh tana ciki kaje kaga likitan first. Wucewa yayi yabarta a wurin, ta gaidasu cikin girma, mama uwar gidan kawu ta rungume ta kamar Y'ar ta cikin jin dadi sannu Y'ar Albarka.
A zaune yake doctor na yimai bayanin basu gane kan Al amarin nan ba yau jiya da aka kawota da Alamar improvement amma yau jikin ya Kara nauyi bayan duk na urorin dake taimaka mata. Dafe kai yayi yace, Zan iya zuwa in ganta? Yafada idanun shi sunyi ja tun baiganta ba, likitan yace "yeah sure muje..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/21/21, 7:43 PM - Buhainat: 5â*ƒ*£7â*ƒ*£&5â*ƒ*£8â*ƒ*£

..... Tunda ya shiga ya hango ta a zube a gadon ya shiga tashin hankali, idanun ta ta bude a karon farko ta zuba mai idanu, so take ta motsa jikinta amma bazata iya ba, bakinta takeso ta bude bazata iya ba, domin har d'an karkacewa yayi kadan, ta rame a cikin Kwana kadan, wasu irin hawaye ne masu zafi suka biyo kumatun shi, for the first time yana regret na bijirewa umarnin ta koda zai mutu, saboda soyayyar uwa da d'a sai Allah, da kyar yaja jiki ya matsa wurin ta tareda dafata yasa kuka mai ciwo, "Am sorry mommy na am sorry", nasan da yaya Ahmed ne bazai taba barinki a cikin wannan halin ba, gashi ni na barki mommy, am not a good Son mommy am sorry.
So take ta lallashe shi tare da nuna mai baida laifi amma bazata iya ba, sai hawaye da kebin kuncin ta itama, dagowa yayi cikin sauri, ya share mata hawayen " please don't cry momy", zanfita dake ko ma wacce kasa ce zaki warke da izinin Allah. Yayi saurin tashi ya koma wurin likitan.
"Doctor zan iya tafiya da ita China kai tsaye ba wata matsala? eh babu saidai mun dorata akan medication na tsawon sati daya, muna so muga ni idan maganin ya karbeta nan da Kwana uku munga cigaba basai ka Fita da ita ba, so have some patience sir khaleel.
Haka ya fito a sanyaye idanun shi sunyi jawur, tundaga nesa taji ba dadi tana ganin Yanayin shi tasan ba lafiya,
Har ya matso tareda bawa manager umurni kai tsaye fuskar shi ba walwala, "take my wife home"
Ya juya yana Kara yiwa kawu bayani, jikinta yayi mugun sanyi y'an da yaki ko kallon ta kuma tana ganin damuwa karara a fuskar shi, daga dawowar su mommy tafara shiga tsakanin su ne ko kuma ciwon tane yasa ya shiga wannan mood din?
Kasa tafiya tayi ta matsa ina dakin inganta kafin in tafi? Tafada cikin kwantar da murya,
"Kije gida no need, batada lafiya banason Abinda zai daga mata hankali kuma.
Kallon tuhuma take mai ba tare da ta gano manufar shi ba ta juya cikeda sanyin jiki domin batada zabi,
"Hajiya ina zan sauke ki? Shiru tayi kadan tana tuna ai ba a gidan shi ya dauketa ba don haka ko yanzu gidan Aunty Raliya tace suje domin batasan me zata fada ba in taje gidan malam.
Tunanin Yanayin shi takeyi a zuciyar ta, they are just fine kafin suzo Asibiti, meya faru? Haka take ta tunani har suka isa gidan Aunty, akwatin ta ta cire tace yaje da nashi kawai.
Aunty Raliya tayi matukar mamakin ganin ta kamar daga sama Saida ta tsorata.
"Naziya saukar yaushe? "Yanzu muka shigo"... Tayi mata bayanin mommy ce ba lafiya tabar shi a Asibiti, "to ke meyasa baki wuce gidan kiba?
"Aunty ba anan ya daukeni ba da zamu tafi ko kin manta meya faru? toh Naziya naga kuna lafiya kalau da mijin ki me zaisa ki dawo gidana? " ko in tafi gidan malam ne ? Tafada cikin fushi kadan da ya hadu dana khaleel ga tanbayoyin Aunty Raliya ga wata irin anger da takeji a zuciyar ta, "Aunty Matar shi na cikin gidan wadda akeso ya Aura mezan je inyi a can?
A'a kanwata duk dai haka bata tasoba, welcome back little sister, irin wannan fushi daga ganin ki kinyo mana tsarabar d'an China ne ko bangkok?
Kinga y'an da kika koma kamar atabaki jini ya fito jikin ki kamar wadda aka saka a engine, ai da badon nayi miki kyakkyawan sani ba bangane ki Naziya.

D'an murmushi tayi kadan, duk da haka zuciyar ta nakan khaleel, Sai da ta huta, Aunty Raliya ta bata Abinci taci kadan ta watsa ruwa, Aunty Raliya ta zauna gefen ta "Naziya akwai matsala na lura, meke faruwa ne meke damunki? Shiru tayi da kamar bazata yi magana ba Amma bata iya boyewa Aunty damuwar ta, da in ina tafada mata Abinda ke damunta.
"Mtsww kin dagamin hankali a banza, kika sani ko ciwon nata yayi zafine shiyasa kika ganshi haka, banson shirme ni banga Abun damuwa a cikiba.
Ajiyar zuciya tayi, badon ta gamsu ba imfact fushi ma takeyi dashi, don haka baccin ta ta shaka sosai don tagaji da zaman jirgin.

A Asibiti sai bayan ta wuce ya bita da kallo yana hango reaction dinta yasan ta shiga damuwar canjawar shi, and he can't help it domin ganin mommy cikin wannan Yanayin duk ya dagula mai lissafi, sannan gashi yanzu Yanayin da yaga ta tafi ya kuma hargitsa mai tunani, bayason barin mahaifiyar shi kuma he wants to go to Naziya, haka yayi ta sintiri gasu kawu sun wuce gida yace sutafi su huta tunda yazo, dama ba azama damai jinya don haka suka tafi.
Ko yunwa bayaji duk da baici Abinci ba ko a jirgi, wallet dinshi ya ciro tareda wayar shi ya canja layin shi zuwa na gida yafara tunanin kiranta, lokacin tana bacci kuma tunda suka sakko 9ja batabi takan wayar ba don haka bata kunnata ba, jin ta switch off ya dafe kai, malam yakira suka gaisa, "Ibrahim kun dawo gidane naga number kasar mu? " eh malam mommy ce ba lafiya shiyasa muka dawo ba shiri.
"Assha subuhanallahi toh kuna ina yanzu? Yafada mai Asibitin da suke.
Malam na kashe wayar ya tashi daga wajen ya shiga cikin gidan yasamu Inna kulu, yace " Hauwa bari inje Asibiti mahaifiyar Ibrahim aka kwantar harma sun dawo suma. Ta jajanta Abun kafin tayi mai adawo lafiya, wani Almajirin shi babba da yazo gaida shi ya kaishi a roba roba har Asibiti.

Cikin girmama surukin nashi ya tarbeshi suka shiga har dakin mommy, malam ya jajanta tareda gaida ita tabisu da ido,
"Um um Ibrahim wannan ciwo nata tun yaushe ne? "Jiyane suka kawota Asibiti Amma bansan yaushe tafara ciwon ba. Yafada yana dukar da kanshi, "Assha, toh me likita yace akwai sauki ko Alamar samu? Ya mayarmai da yanda duk likita ya fadamai, ya girgiza kai yace Allah ya sauwake zata mike da izinin ubangiji karka damu ciwo jarabtace daga Allah Kuma jinya na kankare wa bawa zunuban shi don haka kataya ta da Addu'a, Ina ita Naziyar? Yace tana gida, ga shirme itada zata tsaya tayi jinyar mahaifiyar taku me ta tafi yi gida kuma?
"Ni nace taje ta huta zata dawo. Yafada kawai. Sannan malam yayi shiru.
Zuciyar shi shima tana wurin ta dan ba halin yabar Asibitin ne, bayan tafiyar malam ya koma dakin tareda zama ya zuba mata ido, zuciyar shi ta Kara karye wa "Am sorry Mommy for leaving you behind, ban kula da Amanarki da yaya Ahmed yabarmin ba. Hawaye ne suka zubo mai har kan hannun ta, ta bude idanun da su kadai suke aiki tana juyawa Alamar yadaina kuka, da tanada bakin magana da ta fada mai duk Abinda yafaru zatayi Amma babu, haka yayita kula da ita sai magrib ya fito domin bin dokar Asibitin ya shiga motar shi da yasa manager ya kawo mai,

Gidan shi ya tafi kai tsaye batareda tunanin komai ba, lokacin su Salifa sun baje a falon Mommy har da kawayen ta y'an iska ga mommyn ta a gefe tana waya akan akawo Mata sabbin gold

tunda duniya tasu ce, sai da ta gama ta juyo tana kallon kawar Salifa da hannun ta ke cikin rigar salifan tace " kufa bakuda kunya Ko kadan ina wurin don iya shege bazaku bari intashi ba, ku yaran zamani bansan meke damunku bane ga maza agari ga Alhazai ga d'anyun jini kubi, don iya shege junan ku kuke lalubewa, kuma ku kashe min hayakin nan ya ishheni haka kuyita bankadar shisha kamar Abinci.

"Old lady bazaki gane dadin bin jinsi bane sai kin d'ana yaseen. "Aa barikin da nayi baikai can ba kudai kuje kuyita yi ni yanzu tunda dukiya tasamu banda matsala kuma kusa ido kwanan nan zata karasa domin boka yafadamin ya fara aiki ya sakar mata ciwo a hankali zata karas.....
Kasa karasawa tayi ta maida kalmar ta ta hadiye mukuth kamar ta hada da makogoron ta, tayi saurin mikewa tana diri diri don ko motsin mutum basuji ba. Tun shigowar shi gidan yasan akwai matsala domin yayi horn har yagaji ba mai gadi yatafi yawon shi, don haka da kanshi ya bude ya shigo tareda rufewa da katon kwado,
Salifa tayi mugun nisa don ba karamin jin dadin tabawar takeyi ba har wani cije lips takeyi idanun ta sun sauya tuni,
Taji salatin mommy, cikin zin zafin yanda take kokarin hanasu jin dadi tace " my God mommy please ki bar nan munaso mu huta if you can't wat..... Ai tafi mommy firgicewa ta tattaro rigarta ta na rufe kirjin ta da kyar ta zabura, mommyn ta na rawar kafafu da murya tace "khaleel yaushe ka.. Ka.. Da... Wone? Kagan mu nan muna d'an jajanta jinyar balkisu ne zanyi girki muje dubata banaso mubar part din ba kowa ayi sata. Tanayi tana kame kame.

Tunda ya shigo yake kame a jikin kofar falon ko motsi baiyi ba tunfara maganar mommy har zuwa yanzu, bazai iya misalta tafasar da zuciyar shi takeyi ba, nade hannun shi suke Saida ya gama kare musu Kallo tsaf idanun shi sunyi mugun kadawa, dukkan su bamai fuskar mutunci ko shigar Arziki, ya juya ya kulle kofar da key tareda cirewa ya jefa pocket ya nufo tsakiyar falon yana karewa ko ina Kallo.
"Hmmm I gave you ten minutes kafin inyi fresh up I want you to clean all this mess. Ya fada yana nuna musu falon da yayi kaca kaca domin sun maida shi dandalin iskancin su.
Shigewa yayi domin akwai tsananin gajiya a jikin shi, sai da ya tube ya shiga bathroom ya hada hot water ya shiga, zama yayi ya runtse idanun shi, " mommy kinga me kika janyo mana ko? kinga irin zabin naki. Yafada yana mai zubo da hawaye, yanzu yaji zuciyar shi ta samu sukunin da zaiyi Abinda yake ganin ya dace don dazu inya biye zuciyar shi kisan kai zaiyi, ya tuna da maganar Hajiya sharefa. Zabura yayi ya dauraye jikinshi ya fito daure da towel.
Waldrp dinshi da yasan akwai kaya ya bude ya ciro kananan kaya guntun wando da Riga T-shirt bakake an rubuta handsome and Arrogant, da farin Zane,
Shigowa tayi cikin karairaya wai ita mai miji, domin sun zugota taje ta yi mai kissa tunda baice komai ba, baiga komai ba, don haka Jakar ta biyoshi dai dai yana daukar wayar shi yaji maganar ta.
"Darling welcome"... wani irin juyowa yayi a hargitse tareda sa kafa ya bata wani irin shoot da bata san yana zuwa ba, don haka wani irin tumbling tayi har jikin kofar ta buga kai Tim, ba shiri tasa Kara.
Wandon da ya cire ya dauka yasa cire belt din jikin shi. Ya rike wutsiyar Alamar da karfen yake son yin hukuncin, tuni har sun shigo a tsorace saboda ihun salifa.

Idanun shi a rufe yace " kuma kunshigomin dakin ne da dattin ku"? toh duk sai kunci ubanku yau sai kungane kun shigo inda bai dace da iskancin kuba,.
Rufe ido yayi yana musu kan mai uwa da wabi har mommyn ma tana zuba salati, "d'an nan zaka iya dukan balkisu Ashe ? Indai zaka b...ai wani irin hambarin da yabata Saida tayi zaman y'an bori, kin saka mahaifiyata cikin ciwo bayan ita ba Abinda take nufinki dashi sai Alkhairi kinzo kin kawo min karuwai cikin gida har gefen uwata kuna iya shege, a kuma gabanki suke lalacewar su don kina tsinanniyar uwa, I think my mother is worst, Alhamdulillah nasan bazata taba aikata irin wannan halin nakiba, domin ta bamu tarbiya mai kyau but you, look at your daughter in front of your eyes.....
Wani irin bakin ciki ya kuma tokareshi ya Kara rufesu da duka sukayi falo suna zuba ihu, mommy da rarrafe da jan gindi ta Fita tana " ni ka daka khaleel ina Suruka..... "Kina karasawa sai na sumar dake wallahi" surukin uban wa ni na Auri Y'ar ki ko kitanbaye ta ko yatsar ta na taba Kallo, ke har kinada Y'ar da Khaleel zai Aura? look nace ku gyara gidan nan kunki wallahi billahi idan Nafita nadawo bakuyi ba zakusha mamaki na.... "Ya isa don Allah malam kai din wa da zaka zo kana dukan uwata da kawayena? Toh bazamuyi ba ka kashe mu kuma kokaki ko kaso ni Matar kace igiyata na wuyanka kuma bazaka biyamin bukata ba dole in nemawa kaina mafit..... Wani irin kwashe ta yayi da kafafun shi " tir Allah ya tsare ni in hada tsalkakakken jikina da najasa, wallahi da in zauna dake a matsayin mata gwara in mutu gauro, kuma inke kadaice mace khaleel bazai taba Aure ba, igiya ko na datseta duka ukun aje acigaba da karuwancin da license dama kin saba ko da mijin ki zai baki kulawa ba isarki zaiyi ba dabba Alade tunkiya kawai, and ke kuma, ya nuna mommy, "ba Wanda zai Fita wannan gidan sai mahaifiyata ta warke idan bata warke ba ko naga wani Abu yasameta wallahi za ayi gudu, don duk sai na nakasa ku. Ya bankada ta ya wuce tareda bude kofar ya Fita ya kuma kulle su a ciki.

Gefen Naziya ya nufa yana nan a garkame a y'an da yabar shi, ya rike kai that means ba nan tazo ba. Wayar shi ya ciro ya Kira manager yace" ina ka kaimun madam?
"Tana janbulo can tace inkaita.
"Nan ne gidana why zaka kaita can kuma bazaka fadamin ba. "Sorry sir bansani ba ne. Ya datse kiran cikin haushi ya Kara gwada kiranta ko yanzu shiru, ya nemi number Aunty Raliya, lokacin suna hira abinsu sun gama cin Abinci,
Daurewa kawai takeyi Amma zuciyar ta na wurin shi tayi mugun sabo dashi zaman su a can tsawon satunkan nan baya Fita ko ina suna likeda juna yasaba mata yau daga dawowa nan ya shareta, zata rama ne itama.
Karar wayar Aunty ce tasa ta kalla taga number shice ta basar Aunty tace "bani wayar to ni in dauka in baza ki daga ba.
Picking tayi tareda sallama, ya gaida ta cikin girma ta tanbaya mai jiki yace Alhamdulillah jiki, kafin yayi shiru yakasa tanbaya ko tana nan. Aunty tace " ga mutuniyar nan. Ta Ajiye mata wayar tareda Fita Abinta tana cewa nabarki lafiya nayi wurin neman lada tsaya yanga ke.
Tana kallon wayar taki dagawa ya katse ya kuma Kira taki dauka, yace " tofa khaleel ka shiga uku yau. Ya Kira yafi sau goma taki dagawa haka ya hakura ya kyaleta dole yaje karbar hukunci in yana son yazauna lafiya da zuciyar shi, a daren dukan su basu runtsa ba, khaleel Kwana yayi tsuki ga takaicin su Salifa ga kuma fushin Naziya, ga wani horo da jikin shi kemai wai bazai runtsa ba tunda bata kusa saboda sabo da yayi, zaune ya tashi yanajin kamar yayi tsuntsu

yagan shi a gaban ta saboda kewar ta, "kin lalatani kinaso kuma ki gujeni baby no way wannan fushin is unacceptable, bazai yuwuba dole gobe kidawo nan I can't take it.

Daren ya mugun yimai nisa, haka itama Amma saboda Yanayin kasalar da takeji daga baya tayi baccin ta, Assalatun farko yayi masallaci da badon kar ace lafiya ba zuwa zaiyi yayi gadin ta har gari ya waye ya ganta hankalin shi ya kwanta. Zama yayi yana gadin safiya, sai yanzu ya tuna da su Salifa ma, ya koma ciki tareda dakko key ya nufi kofar ya bude, suna shahsheme a kasa, Hajiya sharefa kugu yayi tsami ko motsi bata iyayi salifa kuwa hannun ta a kunbure Kwana tayi kuka saboda azaba daga gani ta targade ne. Suma sauran sai nishi sukeyi zasu iya rantsuwar ba mahalukin da ya taba musu irin wannan wulakancin na khaleel.

Taka hannun salifan da yayi ne yasa ta saka Kara mai karfin da ta tashe su har mommyn tana "wannan y'a akwai ki da shegen raki saikace nima ba ciwon nan ne dani ba wannan akwai tambadadden.... Tayi tsit ganin shi duk suka mike tareda fara bashi hakuri " khaleel kabarmu mutafi yanzu kaga mun gyara ko ina wallahi bazamu kuma shigowa gidanka.... "Kuma nafada muku bazaku bar gidan nan a banza ba bayan kunyi sanadin kwanciyar mahaifiyata Asibiti", Kujera ya samu ya zauna tareda dora kafa daya kan daya yace yanzu inaso inji duk Abinda yafaru bayan bana nan kafin inbarku kufita gidan nan oya I'm all ear's. kayi hakuri bab.... "Kul kika kirani da wannan sunan ni ba sa'anki bane, call me sir khaleel ko sir Ibrahim. "Sir khaleel nidai naso in tafi mommy ce tasa ni zama wallahi ni na hakura da Auranka tunda naga baka damu dani ba, Amma mommy..... Ta bude mai bakin Jakar tsab momyn ta na mintsilin ta karta fada maganar takardaun Amma Kash tuni tayi b'ara, "takardun ka da managern ka yakawo suna nan ban tabasu ba wallahi. Dafe baki yayi yana mamakin greediness dinsu duk Abinda suke dashi wato bai ishesuba nashi suke hari da Dukiyar mommyn shi. "Wato 419 kuke yi kenan? Shine kukazo har gidana zakiyi in the name of Auren hadin zumunci, you know what? mommyna harga Allah so take zumuncin ku ya kullu shiyasa ta matsa mana domin Y'ar ki dagani har Yaya na, Ashe ku zuciyar ku sharri kuke nufin ta da shi, alright zaku ga karshen cin Amana kuwa. "Wayar shi ya ciro ya Kira manager yace ya zomai da police yanzu yanada y'an 419 a gidan shi. Tuni suka fara kuka mommy na rokon shi kawayen nacewa " mudai meye namu aciki kawai mu masoyane abarmu mutafi ba ruwan mu da rigimar gidanku, salifa kinga kunjefa mu a matsala daga Zuwa hutawa. Karku damu zaku huta a bayan kanta. Ya mike tareda Fita ya rufesu ganin suna kokarin biyoshi suna roko. "Mommy kinga masifar da kika jefamu ko nafada miki halin khaleel kingani bantaba zuwa prison ba yau zaki sa in shiga bayan inada Abinda zai isheni Rayuwa ta ko wacce kasa nakeso inada manyan babe da zasu kaini in more, now look what you have got us in to, wallahi bazan yafe miki ba mommy.
Ga Y'ar banza don wa nake duk wannan abun badon ke nake yi ba saboda banaso ki wahala.... "Oh really? All tanks to you now we are going to rot in jail".
Ke kibarni inji da kwankwaso na dakeyi kamar ya fita da gangar jikina.
Kuka tasa tace " ni hannu na bakya gani ya kunbura dakyar nake dagashi wallahi, nidai Allah ya isar min. "Gawa? Inji mommyn. "Ga duk Wanda ya tsargu. Tafada tana murguda bakin ta saboda tsantsar rashin tarbiya.
"Toh mu muyiwa wa Allah ya isa ke Ko uwarki ?, saboda jarabar ki yau kinja mana masifa mu bamuci ko fucika ba. Amma kunci ni shegu matsiyata la'anannu kawai jarababbun ba.. ai tuni

dambe ya kaure suka fara jirgar ta mommy na ihu gashi bata Iya kwakkwaran motsi. Karku kashen ya'. Basu daina ba Saida khaleel ya bude kofar, sunyi mata lilis duk sun jijjimata da kunba, police yabawa izinin shigowa yace duk su kwashe su. Tana numfashin wuya dakyar haka aka jasu keeeee, aka watsa bayan mota, mommy sai rokon shi takeyi yayi biris, yanzu burin shi yaje yaga farin cikin zuciyar shi ko a wane halin take?

Wanda tunda ta tashi suka hada lafiyayya breakfast da Aunty suka shirya a basket, ta kintsa cikin wata tsaleliyar doguwar Riga Y'ar Oman ta nade kanta da mayafin, ba fushi yakeyi ba na ba dalili zai sha mamakin ta tayi kyau na fitar hankali dole duk Wanda ya ganta yasan Matar wanice, mijin Aunty a lokacin da zai Fita ya saukesu a Asibitin, tundaga harabar take baza idanun ta ko zata hango shi, Saida suka tanbaya dakin aka nuna musu, bashi ba Alamar shi yana can yana dealing dasu mommy, takara cika, sai a lokacin taga mommy, tayi matukar tausaya mata har wasu hawaye taji sun zubo a kuncin ta, kai Rayuwa d'an Adam ba bakin komai yakeba yanzu mommy Y'ar gayuce haka kwance ko motsi bata iyawa, matsawa sukayi bakin gadon ta dafa hannun ta, tace "Sannu mommy Allah yabaki lafiya. Ta bude idanun ta ta zuba mata ido sai hawaye, so take ta bude baki tafara bata hakuri Amma ba hali, hannu Naziya tasa ta goge mata hawaye, nurse ce ta shigo ta tanbaye ta za a iya bata Abinci? Tace eh su bata mai ruwa saboda bakin daya d'an juya.
Dama sunyi kunun gyada, "Aunty Raliya ta zuba mata, da taimakon nurses Suka d'an dagata saboda nauyin jikin ta jingina mata filulluka, cokali tasa tafara bata kunun Tanayi tana gogewa saboda dawowa yakeyi kamar jaririyar da ake koyawa cin Abinci, ido kawai take binta dashi da hawaye, sai sannu sukeyi mata, Aunty Raliya tace " kinga shirmen ki Naziya ki tsaya tunjiya saboda kula da ita kin kama kin tafi. "Aunty laifin shine ko bari baiyi na gantaba Ashe jikin yayi tsanani har haka ne, yanzu bazan koma ba zan tsaya da ita anan inkinje ki sa akawomin ko Kala biyu ne masu saukin sawa.

Tunda yagama dasu cikin gaggawa yayi wanka ya shirya cikin d'an kareriyar shadda Arsh guntun Riga tasha dinkin gayu na maza, ya fito yafada mota, hankalin shi ya kasu kashi biyu, mommy da Naziya, don haka ya yanke hukuncin zaije Asibitin first ya dubata don yasan inyaje wurin Naziya zai iya mantawa da kanshi acan, koda ya isa Asibitin yasha mamaki, Wanda tundaga kofar dakin kamshin ta yafara yimai welcome, wani irin Ajiyar zuciya yayi tareda murmushi kadan yace " my happiness tunkafin ya ganta..... ğŸ–Š

Matar Soja
10/22/21, 12:00 PM - Buhainat: 5â*ƒ*£9â*ƒ*£&6â*ƒ*£0â*ƒ*£

..... Ita kanta ta san ya isowa tunbai karaso ba, don haka tuni ta Kara hade fuskar ta tamau domin tayi mugun daukar fushi dashi, tuni ya ji wata natsuwa ta ziyarci zuciyar shi, cikin takun kasaita ya shigo, hade da sallama kasa kasa idanun shi a sama, domin ba Abinda yake buri sama da yayi ido biyu da ita, yayi matukar kewar ta, sai jera Ajiyar zuciya yakeyi tunda ya sauke idanun shi akanta, gangar jikin shi tuni ta amsa gayyatar ganin ta da tayi tank God ma manyan kayane a jikinshi, a bu biyu yanzu zai hanamai rungume ta ya rafe zafi, nafarko Aunty Raliya na biyu momy, don haka ya saita kanshi yayi gyaran murya, tareda gaida Aunty, tamai ya gajiyar hanya da mai jiki, ya Amsa cikeda jin kunyar ta.
Kafin ya matsa gab da gadon, taki ko dago kanta sai bawa momy kunun take tana gogewa, he wants to touch her amma no way, don haka ya waske yana fisgo maganar "momy sannu. Ido ta juyamai Alamar amsawa, fita Aunty Raliya tayi domin amsa waya, yayi Ajiyar zuciya yayi saurin riko hannun ta batareda damuwa da idanun momy ba saboda he can't help it, tayi saurin dago kyawawan idanun ta masu rikita shi tace " meye haka agaban momy please stop. Tafada tana karkata kanta, " why kika ki tafiya gidanki kikatafi na Aunty Raliya? Hannun ta take kokarin kwacewa amma takasa don rai ita tasan kunya, momy Naji Nagani wani irin dadi takeji y'an da yarinyar ta nuna mata kulawa ga kuma Alkunya da zata iya mikewa itama zata basu wuri su zanta da junan su, Amma ko yanzu abun mugun faranta mata rai yakeyi har ya nuna a fuskar ta, "let me go please. Tafada" I want sai kin fada min dalilin da kika tafi gidan Aunty kuma nakiraki kinki daukar wayata kuma kinki kunna taki why?
Dago kanta tayi ta kalle shi cikin fushi tace ka sakarmin hannu idan kai bakajin kunyar idanun momy ni inaji please let go. "Never ever, if I let you go in zauna da wa? "Your second wife da kakeson kasancewa da ita that's why ka koreni batareda kama bari na duba lafiyar Momy ba jiya that's why na koma inda dama ka dakko ni kafin mubar kasar nan, ni nasan matsayina banda wani value a wurinka, kuma am not here because of you, nazo saboda nadamu da lafiyar momy tana warkewa shikenan.
Wani irin kallon what is wrong yake mata, momy feels bad saboda itane duk wannan mis understanding din ita tajawowa d'an ta, kallon Naziya tayi taga ita din dai data raina ita tafi dacewa da d'an nata ga hakuri da tarbiya, don haka taji duk duniya ba Abinda takeso yanzu kamar ta warke ta gyaro kuskuren ta,
Mikewa tayi da cup din ya Kara rikota, " Naziya please stop it, ko so kike ki dagamin hankali um? Dagowa tayi taga momy ta rufe idanun ta, ta ce "I said let go of me. Shima kallon momy yayi kafin ya Kara matsota cikin rage murya sosai dake dauke da damuwa, "meye nayi kike kokarin horani haka please am sorry koda ni bansan laifina ba kiyafe min but I can't handle your anger on me.
Fisgewa tayi ta yi bathroom domin dauraye cup din da spoon, ya runtse idanun shi tareda dafe kai " oh my god khaleel ka boni. Yafada tareda binta cikin sauri, tana kokarin fitowa ya maida ita tareda datse kofar, "kallon shi tayi fuskar ta a tamke "meye haka Aunty Raliya zata iya shigowa kuma kasan momy dai Nagani ko? " Hmm so what? In zaki yi kokarin horani da irin wannan new attitude din ya kikeso ni inyi behaving, tell me? Look am not use to this, and I can't take it any longer please forgive me if I wrong you.
Ji tayi yakara tunzura ta wato shi baisan laifin shiba, don haka cikin zafi ta dago tareda cewa " ba Abinda kayimin kawai bana son damuwa leave me alone OK.
"Hhhhh story, rubbish, you are insane Naziya, leave you alone, ni khaleel? You are dreaming

wallahi, ban hakura dakeba tuntuni sai yanzu da kika gama shigewa cikin rayuwata kika yimin dalla dalla, hannun shi yasa cikin sauri ya fisgo kugunta ya hade ta da Kirjin shi, Saida yaji kamar ya shekara bai kusance taba saboda shauki da kewar ta, "Ahhhhhh Hmmmm. Yafada tareda kankameta kamar zai mayarda ita cikin jikin shi, kokarin kwacewa takeyi ya hanata dole tayi lakwas tana sauraran bugawar zuciyar shi tareda rawar da jikin shi keyi kamar bai saba rungume taba" baby banyi bacci ba jiya kinsaba min da yin bacci kina saman kirjina bayan kin shayarda ni zumar ki tareda madarar ki mai rikita kwakwal war mutum, why kike fushi dani why kika barni nikadai jiya why kike son ki gujeni bayan kinsan zuciya da gangan jikina bazasu dauka ba?
Samu tayi ta fisge haka kawai taji yanaso ya tayar mata da feelings a Asibiti a banza yabarta da Abin kunya, tana juyawa ya kuma hade jikin shi da bayanta yasa hannu ya rungumo Dukiyar fulanin ta tareda matsawa kadan yana gwama numfashi, "Am honey, kinji let go home yanzu zamu dawo please baby. Yafada yana goga mata jikinshi, she can feel how hard he is, tayi saurin bude kofar domin takai gab ta fisge ta gudu.
Matsawa yayi baya kadan ya dafe bango tareda runtse idanun shi ya dade a wurin kafin ya d'an dawo hayyacin shi,
Ta gyarawa momy kwanciya tareda komawa gefe taja kujera ta zauna, Aunty Raliya tashigo, Wanda har lokacin bai fitoba, tace "ni zantafi nabar yara Allah yakara lafiya Ina khaleel din? " gani Aunty yafada kanshi kasa domin yasan for sure yadago fuskar shi zata ga canjawar idanun shi, yace "bari muje in sauke ki tom, "Aa Wallahi ga mota nan megidana ya aiko yaron shi Allah ya bata lafiya.
Godiya yayi mata Naziya ta rakata ya zauna tareda bin bayanta da Kallo yana tausaya wa kanshi, Saida Auntyn ta tafi tadawo,
Still fuskar ba walwala, ya kalleta cikin da tausayin kanshi yace " muje ne? Banza tayi mai ta dauki Jakarta karama ta ciro wayar ta ta kunna.
Tafara game, karkace kai yayi yana kare mata Kallo tundaga fuskar ta har zuwa kirjinta har kafafunta data zame takalmin ta dora daya kan daya, jajur dasu mulmul, ya hadiyi miyau Kut a zuciyar shi yace " kinada Abinda duk zakija min aji yarinya is your time. Haka suke zaman kurame Wanda har doctor ya shigo tareda duba momy yafita, suka cigaba da zaman haka badon zuciyar shi nasoba sai dan baida yanda zaiyi, idanun ta akan su momyn khaleel din ma kebata tausayi yanzu da tanada baki da ta lallashi Naziya domin ta rikemata yaro hankalin shi ya kwanta,
Sallamar su Shukrah da malam harma da Inna da sadiq ne yasa ta zabura cikin matukar murna ta nufesu, shima mikewa yayi cikin girma mawa ya gaida surukan nashi, malam yace yamai jikin? Sukace Alhamdulillahi.
Matsawa tayi zata rungume Inna tace " ke bani wuri ingaida mai jinya mara kunya. Shukrah tayi dariya tace Aunty nidai Rungume ni nayi kewar ki. Suka rungume juna yana kallon duk wani motsinta kamar ya sace ta ya gudu yakeji, ganin ta yakeyi kamar ma bai taba Rayuwa da itaba,

Komawa sukayi gefe itada Shukrah su kuma suka matsa jikin gadon suka fara gaida ita, "Sannu Hajiya Allah yasa kaffara ne. Inji Inna da sai yau suka hadu da juna ido da ido, kallon iyayen Naziya takeyi tana hango tsantsar datti jantaka a fuskokin su, malam yace "kulu ciromin Ruwan zam zam din nan da kunnen magaryar. Yafada yana zama gaban gadon, a wurin ya balle Y'ar

Karamar robar Inna tabashi cup ya juye ya fara Addu'a a ciki tareda mutsika ganyen magarya yace Naziya zo ki karba ki juye a gora kuna shafa mata a hannu da kafafun ta har fuska sau uku a yau.
Ai kamshin baya damuna yanzu. "Hmm why to baki koma dakin kiba? " kunya nakeji ai. "Ok jekici gaba da zama da Momy ni zanje in Auro wadda zata zauna dani batareda tabarni ina walagigi ba kamar maraya, kinsani baby kinsani this is not easy for me amma kin kyale ni kusan tree weeks marana na ciwo look. Yafada yana zameta tareda zare towel ya nuna mata hajiyar, " kingani she needs you badly kin gujeta bayan kin saba mata da dumin ki da dadin ki. Yafada yana fitar da nishin sha'awar ta da kuma zakuwa. Hannun ta mai laushi ta saka ta kama kamar tanajin tsoro ta d'an murza kamar mai lallashi tace "Sorr..... Saurin kama bakinta yayi domin gudun karya kurma mata ihu momy tajisu, jikin shi na rawa ya dora hannun shi saman marar ta"

Sorry baby I miss your momy badly kasa an horani.
Tsit kakeji na tsawon awanni baka kuma jin duriyar suba nidama na tsere don kar in makance, koda naga ankwashe hour biyu na koma naganta dunkule a cikin bargo, yana makale da ita kamar ya shige jikinta yana rage murya, " baby last round please please please.... "Um um wayau ne kace last dazu yanzu kuma kace last nidai a'a. "Oh baby wallahi kece kikaja fa how many weeks? Da wayo yasamu ya shige cikin bargon na kuma guduwa,, domin gwara inyi musu nisa Aunty Aisha ta hanani leken Asiri,
Har dare momy bata kuma jin duriyar suba, tayi dariya tareda wucewa dakin ta da taimakon mai aiki nurse dama zuwa takeyi kullum ta zo ta dubata ta tafi.
Dadduma ta hau ta yita addu'oin ta na neman kariya tareda yiwa Ahmed Addu'a, sukuma tayi musu Addu'ar Daurewar zaman lafiya.
Zuwa dare kuwa tattarawa sukayi suka gudu gidan su, soyayya ta dawo sabuwa fil, tattali da tarai raya kamar ya mayarda ita ciki, Washe gari koda ya tashi yayi sallah da kanshi ya hado mata breakfast ya bata yace su koma bacci kafin suje part din Momy, kallon shi tayi " bazaka je aiki ba? "Yes am the boss so na dauki hutu saina huta kafin inkoma sai duk kinbiyani bashina da kika dauka. "Nafa biyaka tunjiya. " waya fada miki ko yanzu kar'i nake nema yafada yana hayewa jikinta tasa Y'ar Kara, "cikina! Yayi saurin sauka tareda shafa cikin "sorry baby na dady wants more, kasan momyn takace ta mallake ni.

Basu suka fitoba sai karfe shabiyu, sunci adon su kamar ka sace su ka gudu saboda haskawa fuskar khaleel shar ya wani murmure tsab kamar bashi bane jiya kalar tausayi, momy na ganin su taji wani farin ciki, bakin ta kamar ya yage tayi hamdala, suka tsuguna tareda gaishe ta, tace "khaleel ya jikin? "Jiki kuma momy? Waye ba lafiya? Naziya da duk kunya ta gama rufeta ta dukar da kai tana murmushi, "kace jiya bakada lafiya, ka warke ne? Sosa kai yayi yace " oh momy kaina ne ke ciwo dama yanzu kuma yadaina saura kadan shiyasa ma bazanje office ba sai man da sati biyu. "Hmmm yayi kyau Allah ya bada lafiya, shikuma maganar Auren fa yasha ruwa kenan? Tafada tana dariya tareda kallon Naziya, da duk kunya ta rufeta, " momy ni na isa inkara Aure bayan inada mata am just kidding karkija a hanani sakewa kuma.
Haka sukayita raha a tsakanin su, ta mike ta wuce kitchen domin shirya musu Abinci, momy tace " karkiyi aikin wahala kibari mai aiki tayi. " momy zan iya ai. Yana binta da Kallo tareda shafa kanshi yana tuna duk wani moment nashi da ita tareda hamdala.

Saida ta wuce momy tace " khaleel ka kai yarinyar nan gidan su ta gansu tunda tadawo bataje gida ba sai dai su da sukazo duba ni suka ganta. "Zamuje zuwa gobe nasa akawo mata motar ta ma yau zata iso. "Masha Allahu dama yakamata ace Matar ka batada motar kanta, nace cikin motocin Ahmed ka bawa malam daya mana me zakayi da tulin motocin nan daka Tara ka samu wasu kudi ka ware ma ka bada tallafi ga Almajiran da yake koyarwa nasan da Ahmed na nan zai yi hakan. Farin cikin canjin halin momy yakeji sosai yace " momy duk karshen wata ina ware musu na Abinci, duk wani Almajirin Malam baya bara yanzu ana dafa musu Abinci ana basu suturu da Abubuwan rufa. "Toh Masha Allah Allah ya yi Albarka ya Kara budi ya sauki Naziya lafiya.

A ranar kuwa dalleliyar motar ta ta iso sabuwa dal ja mai duhu, tayi farin ciki sosai har momy

saida ta lallaba ta fita tagani tareda tayata godiya, tace " madallah saura kuma koyon tuki.
"Momy ai na koya a can da mukaje bari kigani ta bude ta shiga suna kallon ta, sai murmushi yakeyi yana kallon yanda ta bayyana farin cikin ta a fili, bai taba yin Abinda yajishi ya faranta mai ba kamar y'an da yau yaga fara'ar ta a bayyane, ga Addu'a da take zabgamai da tafi komai dadi a wurin miji, ta tayar tareda d'an tukawa kadan ta kashe tafito tana mai rungume momy saboda farin ciki, yau itace da motar kanta, " Aa sakeni kije ki rungume Wanda ya siya bani ba. Tafada cikin tsokanar ta, " kyaleta momy ai tsegumi ne yasa ta tsallakeni ina ware hannu. " to rasa kunya. Ta juya ta wuce cikin gidan ta tabasu wuri.
Matsowa yayi ya riko hannun ta "let's go ayimin godiyar a ciki not here yafada yana daga mata gira tareda cirata sama ba ruwan shi da idanun mai gadi, tako sagalo wuyan kayanta tsab, domin ta shirya biya da kudin da ba aganin su..... ğŸ–Š

"Toh a hankali dai munkusa kai karshen wanna labarim da ikon Allah don haka ina fatan Allah yabani Iko tareda juriya kukuma Allah ya Kara muku hakuri masoya yakaro kauna ya Kara budi ya warware wa kowa matsalolin rayuwar shi Allah masu Aure Allah ya karo d'an kon kauna, wainda basuda miji Allah yabasu nagariğŸ™.

Matar Soja
11/3/21, 1:14 PM - Buhainat: 6â*ƒ*£5â*ƒ*£ &6â*ƒ*£6â*ƒ*£

..... Alhamdulillah Rayuwar tayi dai dai a wurin wainnan ma'aurata khaleel a kullum cigaba yake samu cikin Naziya ya girma sosai ta shiga wata na tara khaleel kullum cikin shopping din baby yake har online yaga sababbi sai yayi oder daki guda ya ware ya shirya kayan harda painting dakin anyi shi irin na dakin yara gadaje hudu different design itadai tace Abubuwan sunyi yawa momy tace ba ruwan ta tabarshi yayi idan taga wani Abu ma ita ke tunamai ya siya, tace "Momy toh ni ko kyalle bai siyamin ba sai baby. "Dole ne wannan kwantar da hankalin ki. Saidai momyn ta siya miki ina zaki kai kaya wasu ma fa ko kalarsu bazaki iya tunawa ba a cikin akwatin ki madam. "Kaifa akwai Wanda yakai ka tara tsumma ko bazaka saka ba,wainnan na Aure ne ka shirya zaka hada akwatunan haihuwa yaro. "Kai lallai zan hado set biyu kuwa harda na Amarya. Yafada ya gudu domin tsokana don yasan ta tsani kalmar Amaryar nan, "ba ason kayan tom. "Ke dalla har yau baki gano halin shi ba ya gane kina nuna kishin kine shiyasa yake tsokanar ki share shi Amarya sai dai yajira ta Aljannah. , momy kafa ta warke tsab zumunci tsakanin ta dasu inna Abun ba'acewa komai, yanzu ta Ajiye aiki tunda tayi jinya, don haka takan

ware lokaci kawai domin fita ziyarar y'an uwan ta, ta dunke sosai da gidan kanin mijinta nata wato Alhaji Muhammadu, Rayuwa ta koya mata darasi mai zurfi harta haddace, da kanta idan taga mai bukatar taimako tana taimaka mai, har gidan su Fauziya taje tabawa iyayen ta hakuri sosai suka ce bakomai ai haka Allah ya tsara, Fauziya na nan na aikin ta tasamu wani Alhaji mai mata daya zasuyi Aure abinsu, don haka Rayuwar ta natafiya y'an da Allah ya tsara mata, ta hakura da Khaleel domin tasan baya ta ita, in akwai mace guda a rayuwar shi to itace Naziya, baya ganin wata mace a suffar mata sai Naziyan shi,

Cikin gidan na koma tana zaune a tsakiyar falon ta, tayi kiba sosai ta bude ga kyau da shekinta na nan sai ma kar'i, da tayi, cikinta yayi katoto dashi kafafun ta sun kunbura, rigar less ce a jikinta fubu domin yanzu sune suturar ta, sukawai take iya jin dadin su, madara da milo ta kwaba wuri daya tana d'an gwala,
Momy ce ta shigo dauke da plate din tuwo da miyar shuwaka, tana jin sallamar ta tafara kokarin boye d'an cup din madarar ta, "turus tayi tace " fito da Abinda kike sha ingani. d'an tura baki tayi tace " kai momy bafa komai bane madara ce. " wato bazaki rufawa kanki Asiriba Naziya, anfada miki nauyin babyn nan ya wuce misali ki rage ciye ciyen nan bakyaji. matsowa tayi ta Ajiye tuwon tace " mikon nan dama nasan tunda najiki shiru anan akwai Abinda kikeyi to nagano ki ai. Sallamar shi ne yasa momy tayi shiru tareda juyawa gefen shi " jinan Ibrahim yarinyar nan zata koma gefe na harta haihu tunda bazaka daina bata Abinda na hanaka ba yazaka rika biye mata kalli y'an da take Kara kunbura kullum.
"Wallahi ba ruwana momy ni ba Abinda nake bata impact nakwashe duk madarar dake gidan nan nima na hakurada shan shayin. " ina ta samu wannan tom. Ta nuna mai wadda ke cikeda cup. Murmushi yayi mai kyau ya matso kusada ita ta dunguri kanta " look baby karkija momy ta rabamu akan wannan Abubuwan da kike yi kinga yanda kika zama kuwa kinkusa biyuna fa, please ayi hakuri da madarar nan. Yafada kamar mai lallashin Y'ar yaye, " wallahi inban shaba jinake kamar numfashi na zai fita don Allah kubari inrika shan kadan bada yawaba. Kallon momy yayi da fuskar tausayi " momy ki taimaka mana kinji.
Tsaki tayi ta tura mata kwanon tuwon "sakko ki mike kafafu kici Wanda zai wanke miki yaro da nono tunkafin ki haihu maza. Tana tura baki ta sakko kasa,
Ta wuce kitchen din ta domin kawo mata ruwa, yayi saurin zama, " baby lokacin tashi office baiyi ba fa nadawo. Dago sexy eyes dinta tayi bayan tasa lomar tuwon ta tace " why? Duk da tasan me ya dawo dashi. "Oh don't pretend like you don't know, kwana nawa rabon da kibarni in huta, nakasa hakurine nadawo. Ganin momy yayi shiru, " kai matsa mata taci abincin ta tunda kai baka lurada taci bataci ba. "Momy nima fa bawanda yadamu da damuwa ta me nadawo yi meke damuna ba Wanda yadamu nazama maraya tun yanzu, toh inta haihu ba mai komawa kaina ma gaba daya. "Ka shirya ma gida zataje wanka tunda ni kun raina ni nafadawa Kulu harma nafara yimata shiri tana haihuwa daga Asibiti sai gidansu sai tayi Arba'in zata dawo.
Dariya yayi harda jingina a jikin kafadar Naziya kafin ya kalli momy da duk sun zuba mai ido suna kallon dariyar rainin wayan shi, "Amma dai momy wannan story ne kawai ba gaskiya bane? "Tatsuniya ce kaji, zaka gani in lokaci yayi. "Gwara ta zamo ta tsuniya kuwa don bazai yuwuba, ina ban Y'ar da ba wallahi, yaron nawa yazo duniya baza akawomin shi gidan ubanshi ba afaramin yawo dashi ina. Tuwon ta takeci tana kallon y'an da ya hakikance yana zuba rashin kunya akan d'an da baizo duniya ba. Saida taci dayawa momy ta kwashi kwanonin tafita ta

kyalesu, yana ganin ta fita ya mike zunbur ya dagata sama daga ita har katon cikinta, yayi cikin dakin su na bacci.
Tsayar da ita yayi ya na kallon katon cikinta abun na burgeshi sosai, wayar shi ya ciro yafara daukar ta hoto, yasaba yanzu kusan kullum sai ya mata hotuna saboda gani yake ba macen da ta taba burgeshi da ciki sai Naziya cikin yakara mata kyau da cikar haiba, tazamo hamshakiya.
"Nidai kadaina daukata haka bayan nayi muni wannan cikin yasa duk nazama wata giwa. "Keke waya fada miki? Ai bazaki gane y'an da kike burgeni bane badon na matsu inga baby naba da nace kiyita zama ahaka ina more Idona, look at my wife, ba raini kinga duk Wanda ya ganki yasan yes bakya tareda lauzy man nacika ki ta ko Ina. Yafada yana wani bubbudawa.
Rigar ta tube domin zafin dake taso mata duk da iskar Ac dake hura ko ina a cikin dakin, tarage daga ita sai under wear da bra, " nima ai ba raguwa bace kasani nima nayi kiwon ka look at you harda wani tunbi ka Ajiye fa, ka kwashe min farin fata ma. " I agree wallahi, domin bakaramar madara nake kwankwada ba, dole aga canji a jikina baby kedin ba ta wasa bace shiyasa kike juyani yadda kikeso, to yazanyi dole in lallaba ki. Yafada yana shigewa jikinta cikin dabara da wayau, tace " banson wayau fa da dadin baki. " Allah ba wayau sai gaskiya, nidai a samma Almajiri yana bara don Allah. Yafada yana mai dora hannun shi saman kirjin ta tareda hade bakin su wuri daya.
Na janyo y'an kafafuna na gudu domin banason ayi aika aika ina wurin,
Sai bayan hour biyu suka fito cikin wani adon yana faman tarai rayar ta,
Ta lafe a Kirjin shi tana nishi " nidai kajamun bayana na ciwo har wani budewa naji yanayi.
"Sorry sorry kinga ki wartsake kafin momyn ki ta hauni yanzu da fada, guduwa ma zanyi office inada aiki da yawa, muje in rakaki wurinta in wuce.
Daga Kofar gidan ya juya ta shiga tana yatsunar fuska, momy na zaune tana kallon labarai a Aljazera tayi sallama.

Can karshen kujera takoma ta zauna dakyar, momy ta kare mata Kallo tace " kai zamani yazo ya wahalar da ita da tsohon ciki abanza, kai khaleel ai dama ina ganin d'an banzan yaron nan nasan me yadawo dashi gida. A zuciyar ta take surutun ta saida taga ta zamo kasa tareda janyo trow pillow ta kwanta akasa, tace " ina shi Ibrahim din? " ya koma office yanzu. "Hmmm. Taci gaba da kallon ta saida taga juyin yaki karewa tace " ke meke faruwa ne? "Bakomai momy. " idan da akwai matsala kifada muje Asibiti yanzu kinji. "Aa babu komai momy.
"To tashi a kasa ki shiga cikin daki ki kwanta kinji kar jikin ki yayi ciwo. Dakin momy ta wuce taje ta haye gadon ta ta kwanta da kyar, maganar gaskiya khaleel yaja mata domin jin bayan ta takeyi kamar zai cire, sai can taji ya tsagaita ta d'an yi Ajiyar zuciya ta gyara kwanciya, tana tunanin halin khaleel, kamar magnet haka ya koma mata gashi baya taba fushi indai akan hakan wannan Abun ne sai yasan y'an da yayi ya mata wayau ya more, All this months bayan dawowar su daga bangkok yaki Y'ar da yaje ko nan da can saboda ita duk da yanada appointment dayawa bai Y'ar da ya tafi ba sai dai yayita wakilta manager dinshi, domin yaso yaje da ita momy ta hana, saboda cikin tace ba inda zaije yakai mata yarinya da ciki sai ta haihu.
Har bacci mai dadi ya dauketa ta zabura tareda tashi zaune domin wani irin amsawa bayanta yayi da ma marar ta bana wasa ba, tuni ta sakko tsaye tafara kai kawo, momy dake falo duk hankalin ta nakan ta tataso ta shigo, y'an da taganta ne yasa tace " ke nakuda kikeyi, kinga y'an

da kike gumi, ina kayan haihuwar taku ko baku hada ba ne? Tace an hada suna side din mu Amma momy ai EDD na bai kaiba.
"Banson shirme nidai ina zuwa ta wuce Abinta cikin sauri ta dakko Karamar akwatin ta fita da ita ta. Driver ta Kira tace ya gyara mota zasuje Asibiti,
. koda ta koma abun fa da gaske ne duk ta gigijce tayi saurin saka mata hijabin ta ta rikota suka fito tana yimata sannu,

Ba bata lokaci suka karbeta lokacin tanajin kamar marar ta zata fashe saboda azaba, sai salati takeyi tana Addu'a , Sukace ai Abun yazo gadan gadan don haka sai labour Room, saboda sauri ko wayar su bata kwaso ba, bare ta Kira khaleel din, shikuwa y'an da yaga Tanayi yasa yayi ta Kiran ta bayan fitar shi, wayar kuma na gefen ta, bata dakko ba don tayi ta ringing shiru. Haka ya daure yaci gaba da aikin dake gaban shi domin bayaso ya kuma barin office sai ya gama, can ya kasa daurewa ya Kira layin momy shima shiru lokacin tana Asibiti itama tata na gida.
Bai kawo komai ba ya ci gaba da aikin shi,
Bayan minti talatin ba tareda doguwar nakuda ba ta sunkuto katoton d'an ta kyakkyawan gaske mai farin fatar ta da fuskar ubanshi,.

Nurses sai santi sukeyi suka shirya su duka uwar da d'an, aka fitowa da Momy da sunkucecen miji, ta karba jikinta na rawa tace "Ahmed dina ya dawo kalle shi sak Ahmed saboda fatar shi da idanun shi, taganshi sak d'an ta mai hakuri, wasu irin hawaye suka zubo mata a fuskar ta, ta fara tofeshi da Addu'a tana Allah ya sa ka gado hakurin mai sunan ka. Momy da karfin hali tuni ita ta lakaba mai suna. Saida aka fito da Naziya dakin hutawa ta tuna da ita taga miji jiki na rawa bakinta har kunne sai lokacin ta tuna da zancen waya, tace " kinga saboda rudu ban dakko wayata ba. Saida ta shiga sadin da aka kwantar da ita ta shinfida yaron kusa da ita tace "Sannu Naziya kinji Allah ya miki Albarka kinga Abinda Allah ya Azurta mu dashi, bari insa driver ya dakko min waya ta a gida nabarta kema taki na can kar khaleel yakira bai san halin da ake ciki ba.
Ta fito tafadawa driver wayar ta na falon ta yasa mai aiki ta bashi ya kawo.
Yana shiga harabar gidan misalin karfe hudu khaleel na shigowa da motar shi, badon ya gama ba yadawo sai don yakirasu basu dauka ba, fitowa yayi cikin sauri ya gaida khaleel din yace "ranka ya dade su Hajiya na Asibiti yanzu ma wayarta tace indakko mata.
"What Asibiti? Meyasa tunda ka kaisu baka kirani kafada min ba? Come on bani hanya ya koma motar ya yi reverse ya fita aguje, kardai ya bantalo aiki ne gashi lokacin haihuwar bai gama cikaba sai nan da sati biyu, don haka a high speed ya isa Asibitin, ko wani rufe motar bai tsaya yiba ya wuce da sauri, ganin momy tsaye tana leken hanya ya karasa da gudun shi " Me ke faruwa momy ina babyn take meke damunta ne? Duk ya rude jikinshi har rawa yakeyi karyayiwa kanshi asara, daure fuskar ta tayi kamar mai fushi tace "kai meye haka tana ciki ga dakin can. Ko jira baiyi ba ya tafi a sittin tabi bayan shi tana dariyar rudewar shi,
Tunda ya tura dakin yayi turus domin ganin jariri kwance a gefen ta yana motsa hannu yana cilla kafafu yana kuka tareda tande baki saboda yunwa.
Idanun shi a waje na mamaki yakasa koda motsi saida momy tace " ko in shafa maka ruwa ka suma ne? Cikin tsokana, " momy baby..... my baby.... Da gudu ya karasa ya na kokarin

sunkutar yaron ya kasa, "tsaya malam inbaka, kallon Naziya yayi data runtse idanun ta saboda marar ta dake ciwo kadan kadan, karbar shi yayi bakin shi har kunne saboda murna da farin ciki ya zauna gefen ta "baby look at our baby yafada yana kallon kyakkyawan yaron shi tareda riko hannun Naziya daya ya naji kamar ya mayarda su ciki, kukan da yaron yakeyi ne yasa ya ce "momy ko yunwa yakeji ne kinga y'an yake bude baki yana kuka. Yafada yana kallon jan bakin yaron d'an mitsili dashi,
"Ai wannan Yaro zaiyi ci tun da yafito yake wannan tande baki, ga uwar na fama yabari ta d'an huta sai a wanke nonon yasha. "Sai an wanke me za awanke they are clean momy tabashi kawai. Yafada yana kokarin kwantar da yaron, momy tabishi da kallon bakada ta ido, shi ko a kwalar shi, "kai bari ta huta kawoshi inbashi ruwan zam zam da Zuma.
Ta bude kayansu ta ciro wani d'an mitsilin cup da spoon ta fita ta dauraye ta dawo ta bude zam zam da kwalbar Zuma mai kyau ta diga ta zauna tareda cewa "mikon shi saika tashi ka Sanar wa su kulu da gidan kawun ku dasu zarah.
Cikin doki ya mike ya fara kiran number Malam suka fara gaisawa tace mikon nan don tasan baida kunya sai yanzu yayi Abinda zai sata a kunya ita, ta karba tace "Sannu malam ya kokari' to dai kayi Aboki kafadawa kulu tasamu miji na kwace. Yayi hamdala tareda godewa Allah yace toh Masha Allahu Allah ya barmana ya raya bari in shiga infada musu.
Kafin kace me kowa yaji wannan haihuwar kafin wani lokaci Asibitin ya cika makil da d'an gi saida momy ta koreshi, su Shukrah Aunty Aisha Aunty Raliya su Zarah sai hira akeyi, ganin yaron na d'an gine Asibitin na cika likita yace zasu iya tafiya ai komai normal ne daga, d'an har uwar don haka zuwa magrib sun gama hada kayan su ta kirashi bayan ya idar da sallah tace yazo ya kwashi Naziya yakai gidan malam an sallame su. Ta kashe waya, Aunty Zarah dake Rungume da yaron tace " tab Aunty bakiso zaman lafiya Khaleel din ne zai bari atafi da Naziya wani wankan gida y'an da yake wannan rawar kafar.
"Yoh biyemai zamuyi, kinsan y'an da nake fama dashi ne ni zanso taje tayi wankan ta mai kyau a gida cikin natsuwa. "ai momy tunda kina nan da kinbarta malam bazai bari ba ma don bayason wannan al Adar. Inji Raliya, ai kuwa malam ya Kira yakai karar Momy yace " ai baza ayi haka ba Ibrahim bana bin wannan Al Ada, dakinta zatayi wanka kaji karka damu.
Yayi Ajiyar zuciya ya buga mota yayi gidan shi saboda yasan yayi tsiya, suna jin shiru momy tasa zarah ta Kira driver ya kwashe su, tace wato saboda nace yazo ya kai ta gidan shiyasa ya gudu ko? Toh tun baizo duniya ba nake hawa mota d'an ubanshi, su Aunty sai dariya sukeyi itadai tayi tsit tana jiran karon su dashi, don ita tagama murna zata je wurin Inna, don wannan ce kawai damar ta idan ta wuce shikenan sai dai ziyara aje adawo gashi idan taje gida baya barin ta ta dade ya rika damun ta kenan ta dawo gidan shi kamar zata gudu,

Suna shiga harabar gidan sukaga motar shi momy tace su wuce nata gidan da Naziyar zataga tsiya, haka aka kaita har gadon momy Aunty Zarah ta shirya ruwan zafi tareda na jariri, Momy tace" Raliya taimaka wa Naziya tayi wankan bari inyiwa yaron. "Toh tace ta taimaka mata tayi wankan tsab ta gyara jikinta su Aunty Aisha suka gyare gadon tareda baza turare ko Ina na baza kamshi, Aunty Zarah ta shiga kitchen ta samu mai aikin ta shirya farfesun naman kaza da yayi lugub ta hado mata da tuwon shinkafa da miyar Agushi, tana fitowa ta shirya, momy tace su Aunty Raliya suje su kwaso mata duk Abinda zata bukata itada yaron su kawo nan kafin su

wuce domin dare nayi.

Oga khaleel na can yana tunanin ta inda zai bullowa Al amarin yaji sallamar su Shukrah, tashi yayi cikin jin kunya dama a shirye yake kawai yana tunanin rigimar da zai tarar yagansu, "Aunty yaushe kukazo? Yafara kame kame " ai mundade da dawowa kayan Naziya zamu kai gefen momy tana can itama..... ğŸ–Š

Matar Soja
11/3/21, 1:14 PM - Buhainat: 6â*ƒ*£7â*ƒ*£&6â*ƒ*£8â*ƒ*£

.....Fita yayi zuwa cikin gidan fuskar shi a turbune, yasamu momy na magana da Aunty Zarah tana ganin shi tace "here he comes, ni na shiga daga ciki. Aunty Zarah tace " ka taro march khaleel. "Aunty wai me kuke nufi dani ne da zaku ajiyemin ita anan. "Ka gode Allah da ta tsaya ma a nan din kai dai ka lallaba Aunty kafin KO dakin ta hanaka shiga wannan ciccin magana da hura hanci kasan badamuwar tabane better come down. "Aunty mutum da iyalin shi sai anyi tajamai rai? "Ni kaga sauri nake inyi gidana ka gyarota baruwa na. Zama yayi a falon ya dora daya kan daya yana latsa wayar shi saida yaga su Aunty sun gama shigo da kayan suna kaiwa dakin momy Aunty Zarah tace "ku muje Raliya in sauke su Aisha mu muyi gidan mu. "Kutafi kubar mana Shukrah nayiwa malam magana, gobe driver yaje ya kaiki ki kwaso kayanki mu na nan zaki taya mu reno, ga dakin Ahmed can ki je kiyi wanka ki huta kinji.
Toh kawai tace ta wuce, su Aunty suka dauki jakun kunan su suka wuce, saida ya musu sallama ya dawo zai shige dakin momy tace "dakata malam bacci zatayi tagaji karkaje ka damesu. Sanin fushi want solve his problem, yace "Ayya Am momy gaisawa kawai zanyi infito kinji please, gaba tayi jin kukan yaron ya take mata baya, " tashi Naziya daure ki gwada bashi Mama mugani tunda yaki yin shiru.
Dago kanta tayi suka hada ido ya mata kuri tareda kallon kirjin, he is eager to watch her feeding his baby, kashe mata ido yayi momy ta fita da feeding bottle din yaron tace bari inyi boiling kan indawo bashi kinji. "Zantaya ta momy don't worry. Yafada yana matsowa, ta harare shi tayi gaba kawai, saida yaga ta fita yayi saurin kulle Kofar yadawo da gudu tareda zama gefen ta ya rungume ta itada babyn dake kan kafarta, " I love you hayati, tank you so much Allah yayi miki Albarka keda yarona, ya bata fake a kunci tareda manna mai shima yace "meyafi wannan farin ciki a Rayuwa? I have everything best wife and now this, best blessing in the world, sune ya'ya baby we are blessed Alhamdulillah, and Allah ya horemin Abinda zan wadataku insha Allahu batareda kun rasa komai ba a Rayuwa in ina numfashi you want lack anything, kinga am ready next year ki suburbudo min twins or triplets. Harar shi tayi tareda cewa "eh mana tunda haihuwar ba wahala badole kafada haka ba. "Hhhh oh come on baby keda daga fita ina dawowa sai naji good news, tell me how, ya akayi ne? " ai bazaka san ya akayiba tunda kaine

ka takalo min nakudar tunfitar ka bayana bai daina ba. Tafada mai komai ya rungume ta gam yana dariya "wow kice akwai wani sirri dake kawo saukin labour amma kike min rowa, OK next time bazan daga kafa ba duk rakin ki. "Nice ma mai rakin? " no ni na isa infada matata jarumace tunda ta sunkuto min wannan katon babyn. karbar shi yayi ya ciro dabino ya mai huduba tareda diga mai ruwan abaki ya fara lashe bakin shi soo cute, yana kallon shi itama tana kallon baiwar da Allah yayi musu, tana godiya ga Allah a cikin zuciyar ta, saida ya kammala ya dora mata shi saman cinyar ta yace "bashi nono ingani kafin momy ta dawo, yasa hannu yana kokarin zage mata zip, ta rike hannun shi tace "wait basai ka cire ba zan daga rigar. " no salon ki danne mai hanci remove the shirt, bai saurareta ba ya zage tareda cire rigar, yaja Numfashi tareda cewa "Hmmm sun Kara kunbura baby. Tana runtse idanun ta taciro nonon a bra ta daga kan yaron ya taimaka mata ta manna bakin shi a kai, kamar yana jira ya cafke yafara ja kamar ankoya mai, tayi Y'ar Kara saboda zafin y'an da yakeja, "yadai? "Zafiiii. " oh meyasa ni idan na kama bakya yin karar? Bude idanun ta tayi tace " naka ai bazanji ba. Tafada tana kashe mai ido. Kuri ya mata na d'an lokaci kafin yace " look you just born karki dauki Alhakina kinga KO yanzu bakisan wane irin hali nashiga ba seeing my son sucking this. Yafada yana dan matsawa, idanun shi na wani lumshewa, ta buge mai hannu tace "zai kware fa. Saida yaron yayi bacci ta zare bakinshi nonon ya biyo domin yariga yakawo, d'an karamin hanky ta dauka zata goge mai baki ya, yayi saurin karba ya saka bakinshi ya sude nonon tas daya zubo, tana kallon shi, kafin ya duka ya lashe d'an mutsilin bakin d'anshi,
"Ruwan nonon kakesha? Fuskar ta a yamutse, dagowa yayi ya daga mata gira Alamar what? No be my property. "Na shanye ruwan.... Bare wannan mai dadin, wow baby zan rika taya yarona shan wannan sweet milk din, meyasa ni da nakesha ba ruwa sai yaro yazo ruwan kezuwa? Hmm bazan taba bari ruwan ya koma ba zaki dauki ciki ki haihu.
"Da gaske kakeyi ko wasa? "What? " shan nonon. Tafada tana kallon shi cikeda son gano gaskiyar zuciyar shi, "of course am serious, in naga dama ma ma ba fura zansiyo ina gutsira inashan nonon ba.
Kyalkyale wa tayi da dariya y'an da yake magana da zuciyar shi daya, kwankwasa Kofar momy yasa ya zabura " good night momyn ki zata fara fada na rufe mata kofa. "Zakazo ka bude ko sai ranka ya baci. Tafada da karfi cikin fada. Yayi saurin budewa ta tureshi ta shigo "bani hanya uwar me kakeyi harda rufe kofa don iya shege kabarni waje yarinya ta haihu yau ma bazaka daga mata kafa ta kwanta ta huta ba. "Haba momy biki fa takeyi mezanyi mata. "Fita don ubanka mara kunya. Tafada tana kokarin kaimai jifa saboda ya fassara ta, dariya yasa yana cewa "Allah ya barmin ke momy natafi nabarki da Ahmed da momyn shi, nayiwa d'an ki takwara. Fuskar ta ta Washe "Allah yayi Albarka ya raya Ahmed. Tana share hawaye da suke kokarin zubo mata. Naziya ma saida taji jikin ta yayi sanyi ta kalli yaron a zuciyar ta tace "Allah yasa kayi halin mai sunan.

Cikin kwanakin ba karamin gata da kulawa take samu a wurin Momy ba, harma da d'an gi, har malam yazo yaga Abokin shi Inna dai taki zuwa saboda Kara momy tayi tayi tace mezan zo inyi da wani miji bana bukata nabar miki Hajiya balkisu, tace toh nagode nikam ina son Abuna, su Aunty Raliya kullum sai sunzo zuwa yamma su tafi, angon k'arni baida sakat Yanzu saboda taron mutane a kullum, saidai yasa Shukrah ta kawo mai shi yaganshi uwar tayi tsadar gani,

Har zuwa ranar taron suna daya tara d'an gi da y'an uwa da Abokan Arziki, Wanda khaleel ya gwangwaje su da shatara ta Arziki Abin ba acewa komai sai sanbarka, momy ma bakaramin kudi ta ke kashewa little Ahmed ba Wanda sukewa lakani da Nur, domin shidin hasken zuciyar sune baki daya, harda sabuwar mota ya d'an karo mata, ranar suna, Ana tsaka da taron aka kawo mai ita, sai lokacin ya shigo cikin gidan duk da taron mutanen ya Kira Aunty Zarah yace " please ku Aramin mai jegon minti biyu, momy ta fito da fada, " kai wai baka ganin taron mutanen nan ka ratso kana wani neman ta mezata yimaka?
Dai dai tafito cikin Adon wani d'an kareren leshi mai shegen kyau da tsada tana walwali tasha kunshi kafafu da hannu ga wani head da aka nada mata ya zauna kamar wata sabuwar Amarya ba mai jego ba, kowa idanun shi ya koma kanta, harda uban gayyar, wani irin narkewa yaji zuciyar shi nayi ganin ta, zai iya rantsuwa ba wata mace kamar Matar shi a duniya, tuni aka fara kashe mata hotuna, kallon ta takeyi da wani irin sirri Wanda tuni ya fahimci itama tana kewar shi don haka bai damu da idanun mutane ba yafara takawa cikeda kasaita dajin yafi kowa sa'a ya matsa kusa da ita tareda rikota, ya ciro dalleliyar wayar shi ya mikawa Aunty yace "snap us Aunty. Akasa shewa domin bakaramin daceew sukayi da juna ba, ga shaddar jikin shi tayi Kala da tata, yaci hula tangaran, ita kanta tasan tasamu miji, yes she can shout out loud and say this is my husband, kowa yaji, ya mugun yimata kyau kullum Kara murjewa yakeyi, she really admire him, har wani kishi taji yana d'an tabata don akwai y'an mata na family dayawa a gidan datasan wata zata iya k'yasa mata miji, don haka ta rike Abinta kam,
D'an dukowa yayi a kunnen ta " let go out side I have a surprise. Yajata suka fita ana binsu da guda tuni momy ta kauce tana farin ciki, duk da harabar gidan akwai motoci birjik bai hanata hango wannan farar motar sabuwa dal ba taji flowers da balloons a gabanta an manna sticker katuwa mai daukeda "For you my wife.
Kafin ta ce wani Abu ya d'an ka mata key din "tank mom nur. Tareda dora mata kiss a bakinta, wasu irin hawaye na farin ciki suka fara gangarowa a fuskar ta, takasa cewa komai domin bakaramin kaya ya d'an karo masu ba, harda gwala gwalai na kece raini da batasan ta ina zata fara sakasu ba, Rungume shi tayi tareda cewa " ina kakeso insaka kaina saboda farin ciki this is too much my love.
Kara rungume ta yayi yana murmushi mai cikeda farin cikin my love data kirashi, " kin biya ni yanzu yanzu for calling me your love baby, I want you to love me more only me, ki nuna min so ki tarai raye ni ki maidani d'an lelenki that's all what I want from you.
"I love you dadyn Nur,zan nuna maka duniya ma zata shaida hakan because I really do love you, you are the best husband the best father and the best son, am very proud of you Allah yakara Arziki da budi yakuma tsaremin kai.
Dagata yayi cak yana juyi da ita duk da mutane na yawo a wurin ko ajikin shi, " Wayyo dadi kice inrika kawo miki surprise domin insamu Addu'a da wainnan sweet sweet words din. "Kai son irin wannan Abu a idanun jama'a? "Kai Aunty wallahi keda momy kunason hana ruwa gudu, sauka tayi cikin jin kunyar Aunty Zarah tace "Aunty nayi sabuwar mota. Tasa guda tareda cewa Masha Allahu Allah yasa Albarka, gaba yayi yabarsu ganin duk Anfito ana tayata murna, tabi bayan shi da Kallo, she feels like following him ganin ya shige gidan su,
 Yanzu take blaming kanta na kin bashi kulawa sosai duk da suna gida daya batasan wane irin hali yake ciki ba, tasan momy na kulada cikin shi, Amma tasan halin shi ta gefen rashin hakuri ta wani wurin gashi bai samu damar complain ba,

Haka taron sunan ya ci gaba anci ansha sun samu sha tara ta Arziki, har zuwa lokacin da kowa ya watse yarage daga momy sai Shukrah domin har naman sunan ma da rana aka soyeshi aka rabe Abunka da manya, nidai nasamu naci hanji domin a cikin naman suna ba Abinda yakai hanji dadi, don haka ni acan na makale.
Tun karfe tara momy tace Shukrah ta koma dakin ta wurin Naziya tanaso tasha magani ta kwanta tagaji da yawa yau. Naziya tace "gaskiya momy kije ki huta tunda akayi haihuwar nan bakya wani hutawa. "Toh miji fa nayi badole ba, nasa sun kai muku duk kayan da kuka samu gidanku kafin sutafi. "Toh Allah yakara girma momy da lafiya. "Amen. Ta yiwa Nur Addu'a ta Kara rufeshi ta fita, tana fita Naziya ta mike tace "Shukrah zanje wurin Baban shi don Allah karkiyi bacci ya farka yayita kuka, har momy tagano bani. "Hhhhh ba ruwana idan nayi bacci yayita bare baki. "Don Allah karkiyi zandawo zuwa karfe goma nan da thirty minutes kinji. "Toh kiyi sauri. Matsawa tayi ta gyara jikinta da kyau tareda feshe jikinta da kamshi ta zunbula katon hijab ta sudada ta fice.

A zaune yake yana kallon hotunan su na dazu yana murmushi, kallon bangon falon yayi inda ya jera hotunan su a bango daya na farko nashi na tsakiya Nur sai nata a gefe, tunda aka haifeshi yamai wannan hoton yasa A gidan, bata ma sani ba,
"Allah ya jikan takwarar ka, yaya Ahmed banda kamar ka duk duniya kayimin komai kana raye katafi kabarmin Abinda zantuna dakai a kullum, Naziya itace kyautar da tafi komai da kayimin a duniya, look at your name sake he is just like you. Yafada yana danna hoton Nur ya bawa wayar kiss "I love you my family, I miss your mother soo much my son har bana iya bacci saboda kewarta. Yaji anturo kofa, a hankali yayi saurin juyawa, zabura yayi tsaye "baby!!!!, ist really you? Hijabin ta tacire tareda ratayawa a jikin hanger ta fara takowa cikin y'anga domin Kara siyemai zuciya. "Yeah nice ko sai na nemi izinin ina son ganin mijina? Jikin shi na rawa saboda tsananin farin ciki Da murna ya karaso da gudu ya rungume ta. "Wow my baby am very happy for this special visit, were is my son? " nabar shi da Shukrah nace bari inzo in shayar da dadyn shi shima tunda shi ya koshi. Saurin dagowa yayi ya zuba mata ido domin kalmar ta tasa yaji tsigar jikin shi na wani irin mikewa da yin zillo, yafara kallon rigar bacci dake jikin ta baka ta lafe saboda silk, kirjin nan dake cike sun wani irin tsone mai ido saboda kunburi, cikin wani irin rawar murya yace "da gaske baby you are going to feed me your special milk? "Yes if you really want t..... "Ofcos I love too ya sunkuceta sai kuryar dakin, sai samata Albarka yakeyi, sanin yayi matukar kewar ta ta dage tabashi taimako sosai har yasamu natsuwa, yana lafe a jikinta sai kissing dinta yakeyi ta ko Ina yace " tank you baby, ina momy kika zo nan? Kara rungume shi tayi tace "tayi bacci da wuri kasan tagaji dayawa, nabar wa Shukrah na gudo nan. "Naji dadi sosai baby ta damu dani sosai. "Bari in koma kar ya tashi yafara kuka Asiri na ya tonu. Tashi yayi ya zauna tareda kallon y'an take kokarin mayarda rigar ta, "kiyi wanka mana. "Sai naje can banda pad inna cire anan. "Wai yaushe wannan abun zai dauke ne yaufa sati daya. "Kai ance sai mutum yayi Arba'in fa. "What da sake fourty? "Bakowa bane fa ni bansan nawa kwana nawa zaiyi ba, "please idan ya tafi kifadamin I can't wait, kinga yanzu kinki bari ko gogawa inyi kadan am missing it "you are shameless. Tafada tana direwa a gadon da gudu, yabita..... ğŸ–Š

Matar Soja
11/3/21, 1:14 PM - Buhainat: 6â*ƒ*£9â*ƒ*£&7â*ƒ*£0â*ƒ*£..... ğŸ”š

bazan rufe wannan Ibr ba batareda godiya a gareku ba y'an uwa marubuta, kun nuna min kauna ta gaskiya kunbani goyon bayan da bazan taba mancewa ba
Gareki my writer SA'ADATU BINT ABDULLAH,
tareda ke AUTAR MANYA, karamcin ki bamai faduwa bane Allahu yabar kauna da soyaya.
Hazika mai yayi fasihiya NIMCY LOVE jin jinar bangirma.
Hakurin ki abun kwatance ne my Aunty, BINTA UMAR ABBALE.
ina maganar hakuri karamci bazan manta dakeba MAMAN NURUL HUDA.
Addu'a tareda jinjinar bangirma mai rubutu da ilimi da hangen nesa HASSANA D'AN LARABAWA.
... GARKUWAR MARUBUTA uwa maba da' mama Allah yasa ki gama labrin tubali lafiya, Kunada matukar yawa bazaku fadi dukaba sai dai kusani duk kuna zuciya ta Allah yasadamu da Alkharin sa Ameen.
Sakon ta Aziya garemu baki daya na marubuta biyu da muka rasa kwanan nan Allah muma yasa mu cika da kyau da Imani, ina kewar ki Zinariya Allah ya Albarkaci Abinda kika bari. Amen Amen

.....shiya rakata har cikin dakin Shukrah nata baccin ta, Nur yafarka tareda saka hannu yana wulwula kafafun shi na shirin yin kuka, da saurin shi yana dariya ya daukeshi tareda fita ya na mata ido ta biyoshi, dakin shi suka tafi ya shinfide shi a gadon shi ya na mai wasa, saida ta shige tayi wanka tafito takarbeshi yana kallon su ta bashi nono ya cafke yana sha, matsowa khaleel yayi tareda hadasu ya Rungume, "my boy na maka wayau nasha nima. A wannan daren baiyi wani baccin kirki ba yana nan makale da iyalin shi, harta ti bacci haka ya zuba musu ido yana godiya ga Ubangiji,
Tsabar gajiyar da tayi batasan gari ya waye ba, haryayi wanka ya shirya ya dauki yaron shi yafito falon dai dai momy na tanbayar Shukrah ina Y'ar uwar ki take? Bata kaiga bada amsa ba tayi wuki wuki domin ba Naziya ba har Nur batasan inda yake ba itama tayi baccin gajiya, "ga jikan ki nan Momy. Suka juya tareda zuba mai ido yana wani irin sheki da daukar ido, "kai ina uwar shi take? "Bacci takeyi Momy kinsan gajiyar taro. Kallon Shukrah tayi tace jeki nemi breakfast kinji, kai kuma mara kunya bani shi inyi mai wanka, Allah ya shirye ka, don iya shege don nayi bacci ka lallabo kazo ka takure yarinya bayan tagaji, kaga kabi yarinyar nan a hankali tana biki karkasa ta kwainuka. "Meye haka kuma momy? Ubanka modu ne. "Momy ba ruwana ita tabiyo ni dakanta fa narakota shine muka kwana anan. "Allah sarkin y'an sharri? "Oh yanzu baki Y'ar da ba Momy? " get away. Ta wuce Abinta. Yayi dariya tareda cewa "sai kin shafa kinga takoma gidan ta zaki gane itama tana kewa ta.

A haka sukaci gaba da jegon su cikin gata da kulawar momy Shukrah dai sati biyu tayi dakyar

inna tace abata Y'ar ta haka, momy tace ai mungode ma ko a hakan kulu. Shukrah ansaka ranar ta da Almajirin malam sadiq, tuni anfara shirye shirye, Wanda khaleel ya biyawa malam da Inna Ummara harma da Shukrah, yace su hajji zasuje bana shida Naziya in Allah yakaimu, sunyi murna sunyi farin ciki sunyi Addu'a tareda sa Albarka.
Momy ce ta tsaya tsayin daka ta hadawa Shukrah kayan daki dana kitchen kafin su Inna sudawo Ummara, Wanda koda suka dawo suka tarar da Abin Arziki, malam Yayi ta fada yace abun Yayi yawa, momy tace Shukrah Y'ar tace da Ace tanada wani d'an ma shi zata bawa ta hada su biyu a gidan ta, domin ba Wanda yaki irin Arziki a gidan shi, suna dawowa aka fara shirye shirye, Nur nada wata biyu, Yayi bulbul, kullum suna hanyar gidan malam a cikin motocin ta sai wadda taga damar hawa, wani lokaci harma ta khaleel tukawa takeyi, kowa yaganta yasan yes tana cikin lokacin ta a gidan mijin ta, tazamo Y'ar gata gidan miji da cikin d'an gi,su suka dage suka gyara kanwar su wadda itama tabi tana gyara kanta domin tasani tana tareda gwarzon miji, da baya gajiya da ita.

A haka sukayi Auren Shukrah cikin girma da farin ciki kowa ya koma gidan shi ya tsuguna, Wanda saboda karamci malam yabawa kawu modu wakilcin uban Amarya shi yayi na ango Wanda ya mugun farantawa kawu dasu khaleel rai, harma da momy tayi farin ciki Wanda wannan dalilin yakara musu Y'ar da da shakuwa a tsakanin su.

Ina labarin su Salifa? Tuni momy ta roki khaleel tareda sa bakin Naziya yasa aka kyalesu, sunyi matukar nadama domin sunga jarabawa don Salifa tuni tafara wani irin ciwo duk ta rame ta fita hayyacin ta Wanda koda aka kaita Asibiti gwajin farko aka gano ta daukeda ciwon zamani, tayi kuka momyn ta harda suma saboda tashin hankali haka ta zauna jinyar ta gata itama kwankwason ta sai a hankali tun buguwar da tayi, fadin halin da suka shiga ma bata lokaci ne, don haka Allah yasa muyi kyakkyawan karshe a rayuwar mu.

Bayan wata shida da haihuwar Nur, a zaune take tana share hawaye yana faman lallashin ta, kallon pregnancy test strip din takeyi tana share hanci, dariya yake hadiyewa ya kalli d'an shi dake zaune yana wasa da kayan wasan shi yayi kamar d'an larabawa saboda sha'awa, "what is your problem Momyn Nur? " kaine matsala ta nafada maka tunfarko muyi planing kaki now look yarona six months ace inada cikin wata biyu, gaskiya kasan y'an da zakayi dashi. Hade fuskar shi yayi for the first time a rayuwar Auren su dayaji ta mugun batamai rai, ya mike zunbur ya fita sai gidan Momy yana huci.
Zaune take sanye da eye glass tana karatun jarida ya shigo a fusace ya zauna tareda dafe goshi. "Kai lafiya ka shigomin gida bako sallama?
"Please yarinyar nan ce fa momy zambata mata rai? "Wace yarinyar ka keda ko ka Haifa a gidan nan inji? " Momy Naziya, wai... She is crying because she is two months pregnant, tundazu take kuka ina lallashin ta, can you imagine she have the gut tace incire cikina momy my baby. Yafada yana nuna kanshi, Ajiye jaridar tayi tareda zuba mai ido nadan lokaci kafin tace "now tell me how you react to her, kayi mata hauka ko? Jinan kar inji kar ingani wai ka hau Y'ar nan da fada, yoh badole tayi kukaba yaro d'an wata shida ace ciki wata biyu. "Ni bance komai ba kawai nafito ne. "Better.
Mikewa tayi taje gidan tareda barin shi anan, tana ganin Momy ta goge hawayen ta, matsowa

tayi tareda zama kusa da ita Nur nata washe mata baki tareda mika hannu ta daukeshi tana mai wasa kafin ta koma kan Uwar.
"Naziya. "Na am momy. "Ina ilimin ki yaje? Ina hankalin ki ya shiga, bakin ciki kikeyi saboda Allah ya miki baiwa,? Kinsan cewa yaran nan biyu dana Haifa ba a son raina bane, naso in tara yara Allah yagani sai ya kasance tundaga Ahmed da Khaleel ban kuma samun haihuwa ba, kinsan me, ina matukar farin ciki kuma ina son duk Abinda zaku taramin koda dubu ne inda rai da lafiya zanrike muku su, kika sani ko biyun sune rabonki? Karki kuma fadar a cire miki ciki koda daga Arba'in kika samu wani kinji ni.? " toh Momy kiyi hakuri. "No mijin ki zakibawa hakuri bani ba. Ta mike da Nur ta fita daga gidan dai dai yana shigowa, "ka Kara lallabata yarinya ce Ibrahim, ta wuce.
Yana shigowa ta tashi tareda nufar shi ta rungume shi gam, "Am sorry Abban Nur, bazan karaba kaji forgive me. "No problem karki damu am ready to take care of you and my child, cikin minti kadan sun gyaro Al amarin su tareda taimakon Uwa tagari a yanzu.

Alhamdulillah, cikin shekara biyar Naziya ta Ajiye yara Hudu bayan Nur, tayi twins maza sai Karamar su yanzu da take goyo balkisu wato Ummul khair, gaba daya batasan wahalar raino ba kakarsu ta dauke musu komai, haka take bin mijin ta duk inda zaije hankali kwance sun yawata kasashe a wannan shekarun, idanun ta sun bude sosai ta Kara wayewa tareda Aji, taso taci gaba da karatu Amma ganin khaleel bai so kuma ya bude mata hanyoyin samun kudi da yawa business center nata nakanta Wanda tafi karfin hidima tundaga dubu daya zuwa dari biyar har million, y'an uwan ta ma sun shaida ita din mai sa'ace.
Kudi na musamman tasa khaleel ya ware tareda gina wata babbar makaranta mai suna Ahmed foundation, wadda take taimakawa marayu da basuda karfi suke samun kulawa sosai batareda ko sisin suba,
Momy ta Ajiye aikin ta tuni bata zuwa sai kula da y'an jikokin ta, haka zata zuba Abinta a mota suje ziyara gidajen y'an uwa, har gidan malam sai suje su wuni susha hirar su sai sun ishi inna da barna tace "Hajiya balkisu ki kwashi mazajenki sun isheni da barna suna fama da jajayen kunnuwa. Haka zasuyi ta raha a tsakanin su, haka take zuwa gidan kanin mijin ta ma, ta canja sosai kamar ba itaba,
A cikin wannan satin su Naziya suka shirya fita bangkok kamar duk kowane karshen shekara yanzu saboda kasuwancin shi. A dai dai lokacin Ummul khair nada wata takwas kuma tagano tana daukeda wani cikin don haka ba wani dogon bayani ta cireta tareda Ajiye wa takwarar ta tabi mijinta domin su hole, tuni ta gano cewa Matar so ke gwarne don haka ta daina damun kanta domin duk cikin dazatayi khaleel na farin ciki, toh meye damuwar ta Sai muce Allah ya karo Arziki da zaman lafiya a tsakanin wainnan ma Aurata..... Pen's ğŸ–Š
Alhamdulillah nagode wa ubangiji da ya nufeni da ganin karshen wannan littafin
Dubun godiya gareku masoya aduk inda kuke, my Real fan's wato AUREN GADO paid grp one and two, domin kune real fan's dina domin kun nunamin kauna da soyayya ta hanyar rububin siyan wannan labarin, fatan Alkhairi agareku bazan taba mantawa da Alkharin ku da hakurin ku gareni ba,
Ina rokon Afuwa saboda yanayi na jinkiri da aka samu akan wannan labari, ba son raina bane kana naka Allah na nashi, this is the though time for me saboda situation dina, am sorry duk Wanda na batawa rai a wannan tafiyar, saboda ajizanci na d'an Adam, ku yafemin don girman

Allah.
Darasin da na ke son y'an uwa su dauka a wanna lbr shine, kaso mutum don Allah,mucire hassada son zuciya handama mugodewa ubangiji da duk Abinda yabamu a Rayuwa, sannan kuma Muna fatan muyi kyakkyawan karshe irin na momy Allah ka nufemu da gyara kura kuranmu kafin mutuwa. Ayi Amfani da Abinda zai amfane mu a wannan lbr sannan mu watsar da duk Wanda baida Amfani kuskuren da ke ciki Allah ya gafarta min Alkharin dake ciki Allah yasa Al umma su anfana dashi,
Dubun godiya gareku masoya da nake bawa a pc kunada yawa, lallai soyayyar ku babbace a wannan labr da kuma gareni Nafisa na yinku over Allah ya karo Arziki ya kareku daga dukkan sharri.

TAMMAT BIHAMDILLAH